OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

*Sadaukarwa ga Ahlina*
Hon- Tasiu Umar Munture (My mahaifi😘)
Haj Mariya Tasiu Umar (Kaunata uwa ta gari😍)
Aunty Khadija Tasiu Umar Dije (My yayas🥰)
Mahraz Tasiu Umar (Dan kanina)
Sailuba Tasiu Umar
Ibrahim Tasiu Umar
Halima Tasiu Umar
Hauwa'u Tasiu Umar
Safwan Tasiu Umar (Autan Ummuh)

Allah ya karama Mana zaman Ify da kaunar juna cikin wannan family kadan me albarka.

*Special gift to My kids*
My jinin jiki my ruwan jiki  ƙalbi na.
Hairan & Affan Allah ya rayamin ku ya albarkaci rayuwarku data yaran musulmi baki ɗaya, My Affan naji kokenka insha Allahu ilahi zai amsa, yace Momynsa taƙi siyo masa ƙani sai auntyn Momy ce ta siyo masa ƙani.🤣🤣

*Tsokaci*
Labarin BAMAGUJIYA labarine me dauke da manyan darrusa da jigogi masu muhimmanci, zakuji salonsa daban da sauran salo please kuyi hkr kubini a sannu kamar yanda kuka bini a Juhud Gidan Uncle Ruwan jira insha Allahu zan warware muku zare da abawa.

*Jan kunne*
Allah daya bazan dauki zagi cin mutumci a wannan karon ba babu wacce nayiwa dole ta karanta littafin nan bana son shisshigi da katsalandan cikin lamura na domin bana shiga lamarin kowa kowa yasan wannan, harkar gabana nakeyi.

*Gargadi*
Haramun ne wani ko wata ya canzamin littafi ta kowacce siga batare da izinina ba idan kina/kana ganin bazan iya nemoka na dauka mataki ba akwai Allah yasan duk inda ka boye a fadin duniya Kuma da sannu zai fitarmin da hakkina.

*PAGE 1*

★★★~~~★★★~~~★★★

“Bibo! Bibo!! Jummala wai ina Bibo ne nifa gsky na fara kosawa da abinda takeyi Mana Kullum zamuje gurin bauta saita makarar damu karshe ma tace bazata ba Jummah idan bazata rinka zuwa ba ta fadamin na daina wahalar da kaina"
Fitowa tayi daga dakin kasar da take ciki tace “Kincika korafi lantai Nifa bawai gurin bauta ne banson zuwa ba samarin garin nan ne suke takurani amma yau naji inason zuwa da alamun addu'a ta zata karbu gurin uwa me tsarki"
Jerawa sukayi kowacce dauke da yar salkarta ta ruwa suna tafe suna taɗinsu suna dariya, Lantai da Ladiyo da Innu sune suke ta shewarsu itakam Bibo hankalinta yabar garesu kamar yanda ta saba ji idan sun tunkaro wajen bautar yauma hakan ta rinƙa ji gabanta na faduwa zuciyarta na harbawa da ƙarfin da takasa sanin dalilinsa.
Ajiyar zuciya suka sauke a tare suka dubi juna Lantai tace “Bibo yau ranar zagayowar haihuwar ki saboda haka ranar ta zama takice me daraja saboda haka kece zaki jibanci lamuranmu zuwa ga mika bukatunmu ga uwa me tsarki"

Lumshe dara$^{2}$n idanunta tayi ta buɗesu tare da karyar dakai suka fara hawa saman Tsaunin gawo wanda wannan Tsaunin shine ya samar da asalin sunan wannan ɗan karamin kauye me dauke da albarkatu birjir a cikinsa kama daga ma'adanan ƙarƙashin ƙasa dake da jiɓi da manyan duwatsun da sukayiwa ƙauyen ƙawanya da kuma albarkar noma data samu tushe da tushiya tun kaka da kakanni da kuma albarkar ruwa wanda yake kewaye da manyan duwatsun da suka zagaye garin,
Wannan tasa al'ummar wannan ƙauye suke rayuwa cikin wadatar buwayi gagara misali.
Al'ummar Kauyen Tsaunin gawo sun kasance Asalin Hausawa na fil azal marasa sallah wato

waɗanda ake kira maguzawa, asalin kakanninsu suna rayuwa a saman wannan tsauni da ake kira Tsaunin gawo wanda ya kasance shine tushensu.

Mazansu da matansu yaransu da manyansu sun kasance suna bautawa wani dutse ne a saman wannan tsauni da suke kira Uwa me tsarki.
Shi wannan abin bauta tasu ya kasance wani mulmulallen dutsene da yake tsaye cikin hukuncin Ubangiji saman wani babban dutse kamar dai ka ajiye kwai kwaya ɗaya saman faifai.
Asali ba wannan ne yaja ra'ayinsu wa bautawa wannan dutse ba face ya kasance wannan dutse Ubangiji ya gina shi kamar ganga in ka sanya hannunka ka daki dutsen zakajishi da tauri ko kara bayayi amma idan kasami itaciya ko dutse ka buge shi dashi sai kaji yana baka wani sauti me zaƙi da daukar hankali kamar dai kana kada ganga haka zakaji sautin na tashi ya cika dukkannin dajin da wannan tsauni yake.
Ba iyanan bane abin ya tsaya a gefe da gefen wannan dutsen bauta akwai wasu dogayen massu guda biyu da suka kangeshi daga gangagewa idan iska ta busa, kuma su wadannan massu duk wata canza kala suke yi batare da kowa yasan Ikc da sa'o'in da yake canzawa ba sannan ta saman su tsinin mashin kenan yana fesar da ruwa a kowanne Ikc yana gangarawa kasa yana haɗewa da wani babban kogi da suke kira kogin wankin zunubi, shi wannan kogi aikinsa na zuwa ne a duk lokacin da wani ko wata ya aikata wani aiki da wannan al'umma take dauka na tur ne da Allah wadarai.
To a wannan lokacin ne za'a kama mutum a daure shi da sarkoki ajashi a ƙasa a kaishi a jefashi wannan kogi a tafi a barsa idan yayi kwanaki uku za'a dawo a dauki gawarsa to wannan shine yake nuna ya mutu salihin bawa domin sunada tabbacin uwa me tsarki ta yafe masa shiyasa ta karɓi rayuwarsa, idan kuma ba'a ga gawar mutum ba to wannan yake tabbatar da cewa wannan bai samu yafiya daga uwa me tsarki ba.

*****

Isa sukayi gaban abin bautar suka dunkule hannayensu tare da lumshe idanunsu suna karanto wasu addu'o'i da su kadai suka san meye suke cewa,
Tsayin Ikc a haka sannan suka buɗe idanunsu Wacce suka kira da Bibo ta durƙushe saman gwiwowinta ta kika hannunta tafin yana kallon sama ta ɗora kanta samansa dogon gashinta ya bazo ya rufe mata fuskarta gabadaya bata damu da gyarawa ba domin tayi imanin a gaban majiɓinciyar lamuranta take,
Cikin siririyar muryarta me kama da busar sarewa tace “Mun kasance masu biyayya a gareki da gujewa saɓa Miki ya abar bauta meye yasa kullum nake kawo kukana gurinki baki sharemin hawayena Jimo Ciwake ya kasance me yawan ziyartarki da hidimtawa gareki, yau gashi can cikin halin jinya baya iya gane kowa da komi saidai ayi masa komai.
Yake wannan Uwa me tsarki idan har kin tabbata abar nufi da bukata to a matsayina na wacce bantaɓa aikata zunubi ba ina nemawa mahaifina Ify da amincewark....."

Da sauri dukkansu suka dago Ikcn da ƙarar faduwar wani abu me karamin sauti ta ziyarci dodon kunnensu suka zubawa sashin da sukaji motsin idanu tare da miƙewa a tare saboda ganin baƙin halittun da suke takowa daga nesa dasu.
Turawa ne su uku sai wasu baƙin fata biyu samari, Ja suka fara yi da baya suma wadannan baki suka tsaya suna kallon kallo can Lantai tace "la ashe idan mutum yana mafarki gani shikayi uwa me tsarki jiya nayi mafarki naga fararen kwaɗi ashe turawa zan gani" yanda tayi mgnr ya Bama daya cikin bakaken fatar nishaɗi har Saida ya dara inda shi kuma dayan hankalinsa ke kan Bibo da ta sunkuyar da kanta ko dagowa batayi yana mata wani kallo na sama da ƙasa zuciyarsa na bugawa da ƙarfi hakanan yaji ruhinsa ya kwaɗaitu da son ganin fuskarta.

Ɗaya cikin turawan ne ya dubi abokan tafiyarsa yace " ma iya tafiya ko?" Cikin harshen nasara yayi mgnr, inda wanda aka kalla ɗin yayi firgigit ya dawo hayyacinsa yayi gaba, suka rufa masa baya har zuwa Ikcn idanun Bibo na ƙasa Saida ta fahimci sunyi nisa sannan ta dago idanunta tabi inda suka bi da kallo karaf idanunta ya faɗa cikin na dayan cikin bakaken hakan ya haddasa masa tsayawar da bai shirya ba zuciyarsa na bugawa da ƙarfi yace "Hasbinallahu wa ni'imal wakil........"
Tashin hankali wanda baasa masa rana jin kalamin wannan mutumin yasa Bibo saurin watsa sumarta baya ta zari kallabinta ta zuwa takalmanta ta nemi hanyar tsira da mugun gudu hakanan suma su Lantai suka rufa mata baya.
Sunaji wadannan baƙi na kiransu amma tsoro da tashin hankali ya hanasu juyowa saima ƙarawa gudun su ƙaimi da suke yi.

Baƙuwar kalmar tayi mugun firgita su karma Bibo Sarkin tsoro taji Ibr musamman data tuna sanadin haɗa idanunsu ne yasa shi yin wannan furuci, to me yake nufi? Kodai tsorata yayi da ganin fuskarta kamar yanda da yawan mazan ƙauyensu suke faɗa? Ko kuma dai wannan kalmar ɗin waƙe ne a gareshi?
Batada amsa har suka isa cikin garin basu dakata da gudun ceton ran da suke yi ba inda suka bar waɗannan baƙi da mamaki gami da dariyar yanda suka razana da ganinsu amma banda wannan matashin mai furuci shi a bangarensa zuciyarsa ce tayi masa nauyi tsoro ya mamaye ruhinsa tunani barkatai suka cika masa kansa kardai ya tabbata duk abinda ya gani cikin mafarkinsa saiya zama gaske yayi mafarki zaije wani ƙauye na marasa addini kuma abubuwa da yawa sun faru ciki harda wannan fuskar daya gani yau a saman Tsaunin gawo wadda a lissafin falsafar mafarkinsa itace ƙaddararsa ta zuwa wannan ƙauye.......

“Meye ma'anar hakan?" Ya furta Ikcn da suke isa ga dutsen da suka zo bincike akansa.... Duba na tsanaki Najeeb abokin tafiyarsa yayi masa “sauyin yanayi cikin ƙanƙanin Ikc Abokina meye ne yake faruwa na lura daga kallon fuskar wannan ƴar maguzawan komanka ya canza anya ba gamo mukayi garin kurɗe kurɗenmu na masifa ba?"
Haɗiye wani ɗaci yayi a maƙwallatonsa ya furzar  da iska ta bakinsa ya saita injin narkakakun idanunsa masu zubawa abin kallo kasala kan Najeeb yaja numfashi yace.
“Ba gamo mukayi ba Sarkin Gida ita ce ƙaddarata......" Da sauri ya kalleshi yace “Bamagujiyar Prince Habeeb meye haɗinka da BAMAGUJIYA da har zata zama ƙaddara?" Yarfa hannu yayi cikin halinsa na ko in kula yace “shine nima bansani ba Sarkin Gida gabana yana faduwa zan bar dajin nan na koma cikin gari kuyi duk abinda ya dace"
[3/27, 10:12 PM] AM OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

*Tsokaci*
Labarin BAMAGUJIYA labarine me dauke da manyan darrusa da jigogi masu muhimmanci, zakuji salonsa daban da sauran salo please kuyi hkr kubini a sannu kamar yanda kuka bini a Juhud Gidan Uncle Ruwan jira insha Allahu zan warware muku zare da abawa.

*Jan kunne*
Allah daya bazan dauki zagi cin mutumci a wannan karon ba babu wacce nayiwa dole ta karanta littafin nan bana son shisshigi da katsalandan cikin lamura na domin bana shiga lamarin kowa kowa yasan wannan, harkar gabana nakeyi.

*Gargadi*
Haramun ne wani ko wata ya canzamin littafi ta kowacce siga batare da izinina ba idan

kina/kana ganin bazan iya nemoka na dauka mataki ba akwai Allah yasan duk inda ka boye a fadin duniya Kuma da sannu zai fitarmin da hakkina.

PAGE 2

★★★~~~★★★~~~★★★

Yanda suka shigo garin ya janyo musu kallo gurin jama'ar dake kai kawo kowa mamakin dalilin wannan gudun mara iyaka yakeyi,
Saida suka isa ƙofar gidansu Lantana sannan sukaci birki suna mayar da numfashi daƙyar suka kai ga wani kurutturen itace dake ƙofar gdan wanda da gani kasan an ajiyeshi ne don hutawa.
Sun jima suna sauke numfashi daƙyar Kande ta kawar da shirun da cewa yau naga masifa ke waɗannan bakin anya ba aljanu bane Nifa tunda nagansu gabana ya rinƙa faɗuwa" fasali Bibo ta sauke tace “wlh Nima bakiji yanda suka tsoratani ba ni saida nayi tunanin ma sace mu suka zo zasuyi...."
Kekam da daukowa mutane ɗaukakkiya Ni wannan kyakkyawan ne ya firgitani da surkullen da naji yana ambatawa

Dariya Bibo tayi tace “ke dallah ba surkulle bane addu'arsu ce ta addininsu kwanaki naji da Jimo Ciwake yayi baƙi yan burni sunayi a wannan abar da suke karawa a kunnensu...."
Mgnr ce ta tokareta a maƙoshinta lkcn da sukaga machine ya tsaya a nesa dasu kaɗan idanunta ya sauka kan wannan kyakkyawan inji Lantai da faɗa,
Sauka yayi daga babur ɗin ya zubanta idanu daga nesa yana ƙarasowa garesu sukuma suna ja baya suna ƙara matsar gdan nasu Lantai, takun maza dana mata ba ɗaya ba hakan ne yasa su cimma su juyawa Bibo tayi da sauri zata kwasa da gudu taji numfashinta ya tsaya cak ƙirjinta ya fara lugude ta ɗago da mugun sauri ta tureshi jikinta na rawar mazari ta shiga waige² kawai sai hawaye ya tsiyayo mata tayi ƙasa da sauri tace “Na shiga uku kayi hkr ka yafemin koma laifin meye nayi maka na rantse da uwa me tsarki idan Jimo Ciwake yaji hakuma tazo nemana ruwan wankin zunubi zai jefani shikenan rayuwata ta galgalce...."

Wani ihu ta saki jin ya sake sanya hannunsa ya riƙe ta sosai da sauri ya ɗauke hannunsa daya ya rufe mata baki tare da zaro mata manyan idanunsa.
Motsa bakinsa yayi kamar zaiyi mgn batasan meye ya tuna ba taga ya sake ta yayi gaba sakin

baki tayi da rawar jikinta da taki barinta tasa hannu ta share hawayenta ta koma ta zauna Lantai dake laɓe ta fito dafe da ƙirji tace “Yau naga abinda yasa buzu ture naɗinsa nikam Bibo mutumin nan ba ɗan yankan kai bane kinga fah aradu irinsu ake bamu Ibr suna shigowa jeji da motoci suna satar mutane suna zuwa sunayin kuɗi dasu"
Sharrrr hawaye ya sake zubowa Bibo tace “ni ba wannan bane matsala ta kinga fa har taɓamin jiki yayi nashiga ukuna ya zanyi yanzu Jimo Ciwake ina shiga zaiji warin maza a jikina....." Sai kuwa ta kuma rushewa da kuka zama Lantai tayi itama ta rushe da kuka tace “Nima na gani naji Miki wannan tsoron amma kinsan me? Tashi muje gidanmu in dafa Miki ruwa me zafi kiyi wanka bazaiji ba ai an ce ana watsa ruwa warin yake bajewa"

Wani numfashi ta sauke me nauyi ta mike suka nufi cikin gdan suka ɗebi yayi suka haɗa wuta suka dafa ruwan komai cikin gaggawa suke yinsa saboda kar Kakatu tazo ta tarar dasu,
Man gyaɗa ta shafa suka fita tanata sauke ajiyar zuciya suka isa gidansu Bibo sunata raɓe² Ɗantala ƙanin mahaifinta ya sawo kai ganinsu tsaye cirko² ya dakansu tsawa yace “durun uwarku kukeyi anan da kuka tsaya kuna tsinkawa mutane hanji” zabura sukayi Lantai ta kamo hannun ƙawar tata suka shiga gda sumsum, wuf suka faɗa ɗakin Jumme ta miƙe da sauri sukayi dako² kamar sunwa megari ƙarya da sauri Bibo tace “ba abinda kike tunani bane muna tafiya ta zame ta faɗa dagwalon kwatami shine muka biya gidanmu ta wanke jikinta" riƙe haɓa Jumme tayi tace “anya kuwa Habibah..." Nan suka kama rantse rantse da duk wani abu da zaisa a yarda dasu wannan ya kwantar mata da hankali tace.

“Ai shikenan ga abinci can na ajiye muku a madafi ki dauko muku kuci ki ɗauki kunun zaƙin kikai dandali" zama sukayi suka fara cin abincin kusan Lantai kecin abincin idan taga ta tafi tunani ta zungureta da haka suka gama sukayi kwalliyarsu anan suka dauki bahon kunun zaƙin suka fice suka nemi ɗan dako ya ɗauka.
Ko a dandalin batada wata walwala ɗan wasan da sukeyi da gaɗa duk bata da walwala kowa dake gurin ya fahimci hakan damma Lantai nata tausarta suna zaune ta rafsa uban tagumi wani almajiri ya iso ya tsaya yace “Bibo wai kizo inji Manuwa yana bakin tukuba"
Tsaki tayi ta kalleshi ta watsar Lantai tace “Kai kaje kace tana zuwa" miƙewa tayi ta zari bahon kunun zaƙinta tayi gaba tana cewa “ɗan baƙar jaraba kutumar ubansa zanyi masa ɗan Shegiyar"
Binta Lantai tayi ta riƙeta tace “bai kamata ba abinda kike yi ni banga uwar da Manuwa ya nema ya rasa ba da baki ƙaunarsa kinga fah babansa Sarkin Noma ne...."

Wani uban tsaki taja tayi gaba tana ƙara jan zaninta sama suna tafe Lantai nayi mata mitar

wulaƙancin da takewa Manuwa.
Can nesa sukaga an haskesu basusan sanda suka rungume juna ba tsabar tsoro da firgici, ƙamshin daya gauraye hancinsu ne yasa su buɗe idanunsu a tare suka saukesu kan Najeeb dake tsaye a gabansu yanayi musu kallon wulaƙanta wulakantacce ya dubi Bibo yace “Meye sunanki?"
Ɗagowa tayi me arhar hawayen har idanunta ya kawo ruwa tsawa ya daka mata yace “banason ƙauyanci tambayarki nayi meye sunanki?" Cikin in...ina tace “Ha...bee...bah...." Lumshe idanu Najeeb yayi yace “Da gaske?" Kaɗa kai tayi yaja numfashi yace “ok dama Mun zo wani aiki ne nan shine ubangidana yakeson ƙulla ƙawance dake...." Zaro idanu sukayi sukace “ƙawance?" Ɗaga masu gira yayi yace “wannan shine gsky duk inda mukaje mukanyi ƙawaye Abokina kuma ubangidana baya ƙawa baitaɓa ƙawa ba amma yasoki kasance ƙawarsa kada kice a'a domin wannan abu ne da bazaki iya kaucewa faruwarsa ba"............
[3/30, 7:32 PM] AM OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

*Tsokaci*
Labarin BAMAGUJIYA labarine me dauke da manyan darrusa da jigogi masu muhimmanci, zakuji salonsa daban da sauran salo please kuyi hkr kubini a sannu kamar yanda kuka bini a Juhud Gidan Uncle Ruwan jira insha Allahu zan warware muku zare da abawa.

*Jan kunne*
Allah daya bazan dauki zagi cin mutumci a wannan karon ba babu wacce nayiwa dole ta karanta littafin nan bana son shisshigi da katsalandan cikin lamura na domin bana shiga lamarin kowa kowa yasan wannan, harkar gabana nakeyi.

*Sanarwa*
Kamar yanda kuka sani ne ba wani sabon abu ba littafan OUM HAIRAN na kudine zaifi ki biya ki karanta cikin kwanciyar hankali, bana Miki/maka fatan kaci haƙƙin daba naka ba domin nasan Allah bazai bari ba musamman yanzu da zamu shiga wata me alfarma.
Ki biya ta waɗannan hanyoyin acct details 0255526235 Fauziyya Tasiu gtbank ko ku turo katin waya MTN ta WhatsApp number na kamar haka 09013718241. Normal group 300, Special 700.

*Page 3*

★★★~~~★★★~~~★★★

Tunda ya fara mgnr suke kallonsa yana ida faɗin abinda yake faɗi ya juya yayi tafiyarsa wani kayan takaici wanda akace yana sonta da ƙawancen har yasha kwana yama riga tafintan nasa barin gurin taɓe baki tayi tayi gaba suna tafe babu me cewa wani Saida suka kusa rabuwa Lantai tace.
“Nifa lamarin ƴan birnin nan ya fara bani tsoro musamman akanki Bibo meye kuma ƙawance tsakanin namiji da mace?" Kawar dakai tayi tace “to basai yayi da gyatumarsa ba tunda shi bashi da ɗa'a aiko mahaukaci yasan wannan ba daidai bane"
Shigewa tayi gdansu Lantai ta wucce nasu gdan, tana shiga tayi watsi da komai ta shige dakinsu ta faɗa kan shimfiɗa ta kwanta tare da lumshe idanunta wannan wanne irin mutum ne? Meye yake nufi da ƙawance tsakaninsu? Tambayar data kwana da ita a ranta kenan har wayewar gari tada tashi wanke fuskarta tayi suka gaisa da uwarta ta nufi wajen gyatuminta ta ishe shi zaune yana shan kunu ta zauna suka gaisa tace “inason dama zanje gona ne" dubanta yayi duba irin na tsanaki yace “gona kuma?" Meye zakiyi a gona?" Sunkuyar da kanta tayi ƙasa tace “Sallau jiya yake cewa da Jumme ciyawa ta ɓata yabanyar gonarka idan ba'a cireba zatayi ɓarna wannan tasa naga ya kamata naje nagani koda abinda zan iyayi" jinjina kai yayi yace “shikenan kije Allah ya tsareki"

Ƴar ƙaramar dariya tayi ta miƙe ta fita saboda murna ko sallama batayiwa Jumme ba ta bar gidan ta nufi gonar tanata yan waƙoƙinta.
Tsakanin gonar da cikin gari akwai nisa sosai amma sabo yasa basa ganin nisan haka taci gaba da kurɗawa tayi nisa sosai daidai wata itaciya ta rinƙa jiyo ƙamshi me kwantar da zuciya tana dosarta ƙamshin na ƙaruwa harta isa jikinta, gabanta ya faɗi “Wayyoh!" Tana mgnr tana ja da baya ga mamakinta sai taga yayi murmushi ya taso daga gurin yace “kin tsorata ko?" Wata ajiyar zuciya ta saki me ƙarfi jin dirin saukar muryarsa har cikin lakarta.
Sake matsowa yayi yace “Ina zaki?" Yana mgnr yanakai hannunsa ga buhun dake saɓe a kafadarta, batayi Masa gardama ba ta sakar masa ya fara dubawa yana kallonta Saida ya gama dubawa tsaf koda baisan amfanin kayan ba alama ta nuna masa gona zata hakan yasashi ɗagowa yace “gona?"

Da sauri a ƙoƙarinta na ganin ya barta ta tafi ta ɗagansa kai yaja fasali ya karyar dakai yace “zan iya rakaki inason na iya aikin gona...." Zaro idanu tayi tare da kunshe dariya ya zubanta idanu har Saida ta saita kanta yace “meye ya baki dariya?" Taɓe baki tayi tace “ba haɗi saniya da tallan kilishi" da sauri ya dawo da hankalinsa gareta yace “sabida me?" Gaba tayi taci gaba da tafiyarta tana cewa “ko cikin malalata akwai gwarzo kaikam ko riƙon lauje bazaka iyaba bare noma"
Murmushi yayi yabi bayanta yace “iya magana kamar ƴar mahauta kuma haka zaki koyamin ba"

Tsayawa tayi tare da haɗe fuska tace “Idan muka tafi gona tare zakasha wahala kuma mutanen garin mu zasuje su faɗawa Jimo Ciwake harma su ƙara da sherri ka taimakeni ka barni naje nayi abinda ya fito dani"
Fuzge buhun hannunta yayi yayi gaba batare da ya sake cewa da ita komai ba dole tasa ta rinƙa binsa da sauri tana cewa dashi “bakaji ba kagafa akwai nisa jikinka bai saba da wahala ba banaso kasha wahala....." Tsayawa yayi ta iso gareshi ya kai hannu zai riƙota tayi saurin ja baya tace “Aa haram giya a gdan Mallam kada ka kuma taɓani jiya daka taɓani Saida Jumme ta kusa ganewa da kuwa ta gane da tuni na zama tarihi don jefani za'ayi cikin ruwan wankin zunubi kuma zunubin nan bazai barni na tsira ba"

Zubanta idanu yayi yace “wanne zunubi kenan?" Taɓe baki tayi tace “ai babban zunubi ne namiji ya taɓa jikin mace a nan garin idan har hakan ta faru to duk inda tayi za'a rinka jin warin maza a jikinta kuma zaija mata ƙyama da tsangwama wannan dalilin zaisa taƙi auruwa domin babu wanda zai ɗauki karya yakai gidansa a matsayin uwar ƴaƴansa"
Murmushi Habeeb yayi yace “Al'adarku nada kyau da tsafta kamata yayi ace baku kuke da wannan tsarin ba mu musulmi mune zaifi cancanta da mu kasance a haka domin ubangijinmu ya hanemu da kusantar zina" daga wannan basu kuma mgn ba sukaci gaba da tafiya har suka kai gonar Habeeb ya tsaya yana kallon gonar ba wata babba bace amma tayi kyawun yabanya da ta burge shi.

Tsinkayo muryarta yayi tana cewa “kaje ka zauna ga bishiyar mangwaro can tunda ka nace Saida ka biyoni” miƙa mata kayan hannunsa yayi batare da yayi furuci ba bai kuma bi umarninta ba, ganin abin nasa na yine yasata wuccewa ta fara aikinta tanayi yana kallon yanda take tafiyar da komai yana gane irin ciyawar da take cirewa da haka shima yakai hannu ya fara tayata.

Ba ƙaramin mamaki ta shiga ba da taga ko ita data saba aikin bata kaishi kwazo ba ta ɗago tasa gefen zaninta ta sharce gumi ta zubansa idanu tana mamakin inda ya iya aikin gona da kuma yabawa kyawun surarsa tabbas yakai kyakkyawa na gaske duk da ba fari bane amma yanada wani sihirtaccen kyawu da hasken fata na tsabar hutu da jin daɗi da yake bayyana kwanciyar hankalinsa.

Ɗagowa yayi ya zubanta idanu tayi saurin kawar da kanta tare da basarwa ta sunkuya tana tattare kayan tana cewa "naga abubuwan mamaki a iya yau dana zauna dakai naga kana isa waccan ƙoramar kana wanke jikinka kana dungura goshinka ƙasa meye hakan yake nufi.... " Cikin mugun mamaki Prince Habeeb ya Kalli Bibo tare da kafeta da manyan idanunsa, yanzu ita a nufinta batasan sallah ba? Mamakinsa ya kawar da cewa "koda yake a ina zata sani?" Tayata tattare kayan yayi yace "Kada kiyi gaggawa da sannu kuma a hankali zakisan komai game dani tunda kin yarda da abotarmu" miƙewa tayi da sauri tana girgiza kai tace "Aa Nifa ban yarda da wata ƙawance ba...." Hannu yasa saman bakinta ta ɗago ta dubeshi idanunsa nakan fuskarta yace "kar kija da ƙudurina inason abota dake kuma ta ƙullu daganan har zuwa lkcn da zan bar garin nan naku kiji a ranki a koyaushe kuma a kowanne yanayi zamu kasance a tare Habeeba bana nufin cutarwa gareki saidai ke kin kasance ƙaddarata"

"Ƙaddara" ta faɗa tare da ɗagowa da sauri, bai tsaya bata amsa ba saima gaba da yayi dole tasa ta bi bayansa suka nufi cikin gari duk inda suka wucce hankali akansu yake har suka je ƙofar gidansu taja ta tsaya shima ya tsaya sun jima a tsaye ganin bashida niyyar furuci sai kafeta da yayi da manyan lulu eyes nasa yasata juyawa tana cewa "Na gde ka huta gajiya" Shigewa tayi ciki yabi bayanta da ido abubuwa da yawa na ayyanuwa a ransa waɗanda ya kasa tantance yuwuwarsu ko rashin yuwuwarsu koda yake Hausawa sun ce da tsoro ake cire saa shikam zuciyarsa na rawa akan abubuwa da dama amma dai zai jarabba kalar tashi nasarar yagani idan yanada rabo.
Da wannan tunanin ya isa masaukinsu Najeeb daya gaji da kiran wayarsa har ransa yayi ƙuna ya tareshi da cewa "Ina kaje?" Tambayar ce ta bashi haushi ya zabga masa harara ya nufi cikin gdan gdane me kyau nesa da cikin gari kaɗan ginin zamani dakunansu harda A C ga babban inji da aka sanya musu me bada wuta kowanne lkc sannan duk wata kalar kayan jin dadin rayuwa sun siya sun zuba a gdan a taƙaice dai idan ka shiga gdan bazaka gane a ƙauye kake asalin ƙauye irin Tsaunin gawo ba.

"Habeeb tambayarka nakeyi ina kaje...." Juyowa yayi ya kafeshi da idanunsa wanda ba kowa ke

jure sanya ƙwayar idonsa cikinsu ba ya tako gabansa yace “Ni kamar ni kake tambaya ta ina naje kamai dani wani ƙaramin yaro ne ko kamai dani mahaukaci da kake gadi na?"
Yayi mgnr yana zare ƙafar wandonsa, harara Najeeb ya watsa masa yace “ka kuwa ɗaukowa kanka abinda zai dameka banga uwar da ta ɗauki hankalinka akan wannan yarinyar mara addini ba da har ka zaɓi zubar da mutumcinka akanta....."
Tsawa ya daka masa yace “Wlh tallahi ka ƙara faɗar wata kalma mara kyau akan Habibah saina...."
“Sai kayi me? an faɗa mara addini kayi duk abinda zakayi sakarai da idanunsa yake rufewa idan yaso abu kamar babu wani abu bay....." “Najeeb...." Ya faɗa tare da ɗaga hannu zai daukeshi da mari me kuma ya tuna saiya fasa jikinsa yana tsuma yace “Ficemin daga ɗaki kafin na illataka..."

Hayaniyar tasu ce tayi yawan da har ta fito da James daga ɗakinsa koda bayajin Hausa yasan lallai koga yanayin fuskokinsu ran maza ya ɓaci ganin yanda Habeeb ke tsuma yana ruwan bala'i yana nunawa Najeeb hanya yasa James kama hannu Najeeb suka fice yana cewa “Kuma ka rubuta ka ajiye wlh indai ina raye zamu koma Dutse wlh saina rusa duk wani shirinka baka isa ka auro mana Arniya mara addini ka kawo mana cikin zuri'armu ba wawa kawai da baya lissafa rayuwa wannan abinda kake shirin aikatawa ai ya cika abin kunya ace duk matan da muke dasu a Family saika fito waje wajen ma ka rasa wacce zakaso sai BAMAGUJIYA to saika aura mu gani ai...."
A hassale yace “Idan Allah yayi saika hana ai ɗan hana ruwa gudu kawai Ni na taɓa jin wannan jaraba kun dameni na kawo matar aure na kawo wacce nakeso nakasa samowa yanzu kuma Ikc yayi kwatsam ta faɗo rayuwata amma kaine na farko da zakayimin hassada to barima kaji Ni kuma naci alwashin ko zan rabu da kowa da komai saina auri Habeeba....."
[3/31, 7:39 PM] AM OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

*Tsokaci*
Labarin BAMAGUJIYA labarine me dauke da manyan darrusa da jigogi masu muhimmanci, zakuji salonsa daban da sauran salo please kuyi hkr kubini a sannu kamar yanda kuka bini a Juhud Gidan Uncle Ruwan jira insha Allahu zan warware muku zare da abawa.

*Jan kunne*
Allah daya bazan dauki zagi cin mutumci a wannan karon ba babu wacce nayiwa dole ta karanta littafin nan bana son shisshigi da katsalandan cikin lamura na domin bana shiga lamarin kowa kowa yasan wannan, harkar gabana nakeyi.

*Sanarwa*
Kamar yanda kuka sani ne ba wani sabon abu ba littafan OUM HAIRAN na kudine zaifi ki biya ki karanta cikin kwanciyar hankali, bana Miki/maka fatan kaci haƙƙin daba naka ba domin nasan Allah bazai bari ba musamman yanzu da zamu shiga wata me alfarma.
Ki biya ta waɗannan hanyoyin acct details 0255526235 Fauziyya Tasiu gtbank ko ku turo katin waya MTN ta WhatsApp number na kamar haka 09013718241. Normal group 300, Special 700.

*Page 4*

★★★~~~★★★~~~★★★

Tsaki Najeeb yayi yana huci kamar kububuwa ya fice daga gdan gabadaya shikuma ya nemi guri gefen katifarsa ya zauna shima yana fitar da iska me zafi sosai kalaman Najeeb sun taɓa zuciyarsa kwafa yayi ya miƙe ya shige bayi ya watso ruwa.
Ba ƙaramar gajiya yayi ba ashe haka manoma sukeshan wuya lallai dole a gaida manoma sallar magrib yayi domin yasan ba kiran sallah zaiji ba Saida yayi Isha yayi shafa'i da wuturi sannan ya haɗa tea yasha dake shi ba ma'abocin abinci me nauyi bane indai da shayi to Ify lau ne.

Tunda ya kwanta yake sakawa da warwarewa majigin hoton Habeeba yanayi masa gizo a idanunsa, tashi yayi ya zauna baisan meye ya tafi da ruhinsa gareta ba ba kowacce mace tafi komai ba ganinta kwana ɗaya yanajin kamar yayi shekara guda da ita baiji zai iya rabuwa da ita ba, saidai abubuwa biyu suna mugun kada masa hantar cikinsa baisan da yaya Sarki Khalil da Hajiya Kilishi mahaifiyarsa dama sauran danginsa na gdan sarautar dutse zasu karɓi wannan zabi nasa ba.
Karfafawa kansa gwiwa yayi da sama kansa ƙumajin nasara tabbas zaiyi duk mai yiwuwa ya kafa kansa a wajen Habibah da iyayenta duk da suma a yanda suke da tsattsauran ra'ayi yasan za'aja daga kafin su bashi damar auren ƴarsu.
Numfashi ya sauke ya koma ya kwanta daidai lokacin da wayarsa ta ɗauki ruri, gabansa ya faɗi

ya mike ya ɗauki wayar numfashi yaja me ƙarfi ganin sunan mahaifiyarsa na yawo a saman sensor ɗin.

Cikin mutuwar jiki ya kara wayar a kunnensa ta sauke ajiyar zuciya tace "Autan Mama kaji daɗin garin arna ka manta dani ko kiran ma da kakemin tun jiya da safe banjika ba ince dai Ify kake?" Wani wahalallen numfashi ya sauke ya shafa sumarsa yace "sorry My love wlh abubuwa ne sukayi min yawa shiyasa lissafin komai ya kwace min ya kike ya Mai martaba da sauran ƴan gida ina Hajiya da Inna duk ince dai suna Ify?" Lfy Alhmdllh ya jikin naka ina labarin surukata...." Wani damm ƙirjinsa ya bayar da sauri ya basar da cewa "Ohhh Mama wai nikam na dameki ne duk kunbi kun damu sai kun ɗora min nauyi nawa nake ne har yanzu ban rufa 30 years ba" katseshi tayi da cew.

"Kai ar ɗan ƙaniyar uwa to so kake sai kakai ka wucce duk mazan gdan nan waye yayi girmanka babu aure? Faɗamin shi haba ubana shi aure ai ƙima ne kuma garkuwa ne ga ɗa namiji nikam gsky nima inason ganin  ƴaƴan auta na kada ka manta fah  ku biyu gareni maza daga babban yayanku sai kai yan uwanku duk mata ne ai Yakamata ku karɓi girman tunda wataran kune iyayensu duk girman mace ƙasan namiji take domin raunin mu faɗaɗɗe daga bakin ubangijinmu...."
Wa'azin nata yaji zaiyi tsayi yace "Is ok Mama kin kusa samun suruka indai suruka ce very soon kinji" murmushi tayi tace "Ubana kenan Sarkin daɗin baki shikenan Allah ya kawo mana rabonmu na alkhairi" ajiye wayar yayi yana murmushi Hajiya Kilishi kenan kullum maganarta Habibunta yayi aure zaidai yi auren nan ko ta sake masa mara yayi fitsarinsa a nutse.

******

Ɗagowa tayi jikinta a mace tace "Na rantse da abar dogaro ba Rabe bane ya rakani gona baƙo ne ɗan birni muka haɗu dashi a hanya shine yace yanaso ya koyi noma Jumme saida nace karya bini yaki ji to ya zanyi masa tunda kince babu kyau jayayya da babba"
Shiru ce ta ratsa gurin Jimo Ciwake ya ɗago yace "Shikenan amma dai banason wannan tarayyar taku saboda ƴan birni basu da gsky idan kin sake haduwa dashi ki faɗa masa nine nace banason alakarku ya nemi wata abokiyar bandake wannan sakarcin da shashancin shashatau ɗin baza ayisa dani ba"
Jinjina kai tayi tace "Na gde zan kiyaye" miƙewa tayi ta koma ɗaki tayi tagumi a haka Kande da Lantai suka shigo suka ishe ta Lantai ce ta sanya hannu ta cire mata tagumin tace "yo yau naga

watsiyar watsewa Jimo ne ya mutu ko Jumme da zaki rafsawa mutane tagumi haka?"

Numfasawa tayi ta ɗago idanunta ya ciko da kwalla tace “yauma shine ya aiko ku?" Zama Kande tayi ta kama hannunta tace “Na rasa wannan wacce irin masifa ce kwana ukun nan kullum sai yazo dandali yasa an kiramu ya tambayemu meye yasa bakya fitowa? Munce masa baki da Ify to yau dai sakomu yayi a gaba wai sai mun rakosa munyi masa iso ya dubaki...." Dafe kirji tayi tace “Na shiga uku kada ku barshi ya shigo kuje kuce masa na tafi hayin badarawa gdan kakata kuma ba'a bin hanyar da dare saboda akwai wata mahaukaciyar damusa da take kashe mutane....." Zaro idanu sukayi.
Lantai ta matso tace “Tabɗi bakisan yanda mutumin nan yake da naci ba ai na rantse da abar dogaro cewa zaiyi mu rakashi garama kiyima su Jumme wayo muje ku gaisa saiki dawo...." Motsin shigowar Jumme ne yasa su miƙewa cikin zaurancensu na ƴammata tayi musu nuni da suje su jashi bayan gidansu.

Jumme ce ta dubeta tayi ƙasa dakai tace “don darajar Baba Tsauri uwarki kibarni yau naje dandali da Lawai me kura ake wasa inason wasansa" murmushi Jumme tayi tace “kin gamani da ƙarshen daraja jeki saikin dawo Allah ya tsareki" tsalle tayi ta saki ihun murna ta fice da gudu.
Bayan gdan nasu tayi da sauri ta nufeshi duk wata gaɓa ta jikinta tana rawa ta baza gashin nan nata me taushi da aka ƙawatashi da kitso kananu iyakar gaban bayan aka barshi duguzunzun rigarta iya ƙirjinta ta rufe cikakku tsayayyu masu faɗin tushe da ɗaukar hankali ta killace su ɗamɗam cikin rigar saƙin.
Cibiyar ta a waje take shafaffen cikin nan zanen tatu  na kibiya anyi mata zanen flower me ɗaukar hankali ƙugun nan yaci uwar jigida kusan naɗi kusan hawa talatin ta cika mata faffaɗan ƙugun nan zaninta iyakar gwiwarta tukatukin ƙafar nan an ƙawata su da nadin duwatsu.

Tunda ta taho ya zubanta manyan idanunsa da suke lumshewa fari tas yake jin zuciyarsa tana isowa ta tsugunna a gabansa ta kama ƙafarsa ta ɗaga ƙafarsa ta ɗora tafin ƙafarsa a tafin hannunta ta ɗago kyakkyawar fuskarta ta sakar masa murmushi da yaja dimple dinta ya lotsa Jan lips dinta suka baje a fuskarta tace “Aminci da nasara su tabbata gareka mutumin birni inata kewarka banganka ba banjika ba har rashin Ify nayi da Jimo Ciwake ya hanani fitowa saboda ka rakani gona...."
Hannunsa yasa tsakanin ƙirjinta da hammatarta ya ɗagota suka fuskanci juna damdam haka ƙirjinta yake bugawa inda shima yake jin wata muguwar faduwar gaba ƙamshin wani turare daya kasa tantance wanne irine yana tashi a jikinta ya hadu da sanyin yanayin damunar ya saukar masa da wata sihirtacciyar kasala baisan sanda ya hadeta da jikinsa ba yasa hannunsa

biyu saman ƙugunta ya kwantar da kansa a saman nata ya sauke wata mahaukaciyar ajiyar zuciya da baitaɓa jin fitar irinta a cikin rayuwarsa ba.
[4/2, 2:43 PM] AM OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

https://youtube.com/channel/UCZ5Vt2--iGyJfTwItSzAnGg

*Ramadan promo*
Kamar yanda kuka sani ne ba wani sabon abu ba littafan OUM HAIRAN na kudine zaifi ki biya ki karanta cikin kwanciyar hankali, bana Miki/maka fatan kaci haƙƙin daba naka ba domin nasan Allah bazai bari ba musamman yanzu da zamu shiga wata me alfarma wannan tasa nayi muku discount nrml group 300 ya koma 200 PC 700 ya koma 500, wannan garaɓasar ta iya satin farko na Ramadan ne
Ki biya ta waɗannan hanyoyin acct details 0255526235 Fauziyya Tasiu gtbank ko ku turo katin waya MTN ta WhatsApp number na kamar haka 09013718241.

*Sanarwa*

Maganar tsarin post da kuke tambaya ta insha Allahu na tsara shi yanda bazai shafi ibadarmu ba zan rinƙa post kullum 9:30pm wato tara da rabi na kowanne dare.

*Page 5*

★★★~~~★★★~~~★★★

Ɓambare jikinta tayi daga nasa ta ɗago manyan idanunta suka shiga cikin nasa hawayen da batasan sun taho ba suka gangaro kan kuncinta, gabadaya ilahirin jikinta rawa yakeyi saboda tsoro da tashin hankali.
Juyawa tayi tana kokarin kwasa da gudu tare da toshe bakinta da kukan yake kokarin fin

karfinta, riƙe hannunta yayi da himmarsa cikin tashin hankali yace “ya Allah Habeebah me nayi Miki meye yasaki kukan ko bakiyi murna da ganina ba?"
Durƙushewa tayi ta turmutsa hannunta cikin ƙasa ta rushe da kuka me ban tausayi da ɗaga hankali, zama yayi da sauri yakai hannunsa don ɗago fuskarta ta tureshi da ƙarfi tace “ni nace ka daina taɓani ɗan birni na shiga uku so kakeyi sai an kasheni a garin mu yanzu idan wani yaga yanda ka kwaƙumani da jikinka zuwa za'ayi a faɗawa Jimo Ciwake kuma na tabbata kasheni zaiyi nima da wannan abin kunyar gara ya kasheni na huta kowa ya huta, duk jikina nasan yanzun warin maza yake...."

Rufe mata bakin yayi da hannunsa yace “Ke bafa haka bane tsoratar daku sukeyi amma babu wani warin maza da ake ji a jikin mace don namiji ya taɓata amma tunda bakiso shikenan yi hƙr nayi alƙawarin bazan ƙara taɓaki ba amma fah inada sharaɗina nima in kin yarda"
Da sauri ta ɗago tace “Wanne?" Lumshe idanunsa yayi ya ɗora habarsa kan tafin hannunsa ya buɗesu akanta ya motsa ƙaramin bakinsa a hankali yace “Wannan shigar zaki daina ki rinƙa killace jikinki kinga ita wannan shigar idan wani namijin yaganki da ita sako zai ɗarsu a zuciyarsa idan ya ɗarsu kuma zaiyi ƙoƙarin ya aiwatar aiwatarwar kuwa itace babban tashin hankali don zai rabaki da ƙimarki" sake kallonsa tayi tace “kamar ya?"
Miƙewa yayi zaune yace “Zaiyi yunkurin keta alfarmarki ta hanyar sanin ki ɗiya mace ma'ana a gwari² zaiyi Miki fyade....." Miƙewa tayi a kiɗime ta dafe ƙirji tace “na shiga uku fyade irin wanda aka yiwa Tani ta mutu?" Jinjina mata kai yayi cikin jin daɗin yanda ya samu nasara cikin sauki yace “Wace Tani?"

Hawaye ta goge ta kama hannunsa suka nufi wani kurutturen ice suka zauna ta sake goge hawayenta ta ɗago ta dubeshi shima ita yake kallo tayi ƙasa da kanta tace.
“Tani yayace a gurina ƴa ce a wajen wan babana wato Baba Uda, ta girmeni amma soyayyar da take min tasa muka zama kamar ƙawaye komi namu tare mukeyi karshe ma Ni kusan a gdansu Tani na girma saboda gidansu akwai wadar yara abokan wasa nikuma gidanmu Ni kaɗai Jumme da Jimo suka haifa.
Tare muke zuwa gona tare muke zuwa tallen kunun zaƙi baban Tani Uda yana dafa Burkutu tare muke ɗauka mukai gurin bauta mu siyar, wata rana da bana mantawa ana bikin kamun kifi baƙi daga gari² sunzo domin ganin wannan bikin gwaninta da akeyi duk shekara domin kaf yankin nan a garin nan ne kawai akeyi kuma shi dama wannan ruwan na bayan gari da muke kira ruwan tsarkakewa tun tale² baa kamun kifi a cikinsa sai shekara shekara wannan tasa duk kifin da aka kamo zaka sameshi narkeke to wanda yafi kowa gwanintar kamun kifi a wannan shekara shine zai auri sarauniyar ƴammata ta wannan shekara.

Za'a ɗaukeshi a kaishi gdan Sarki aje a ɗauko sarauniyar matan shekara a kawo ta a daura musu aure kuma babu ruwan wannan bikin da cewa baƙone kai ko ɗan gari haka za'a bawa me Sa'a matarsa ya tafi da ita.
Kasan meye ya jawa Tani faɗawar azal?" Numfashi yaja ya girgiza kai ta sunkuyar da kanta tace “Kyau ɗan birni mu kininmu muna da wani irin kyawu da bansan ta ina muka sameshi ba bawai zallar kyawun fuska ba a'a direwar halitta ga kuma wani farin jini da kakanninmu suka roka mana abar dogaro ta bamu, Tani kyakkyawa ce ta wucce misali don duk kyawun nan nawa da ake faɗa ni banfi rabinta ba saidai fatar mu iri ɗaya ce wankan tarwaɗa, hakan yaja mata cincirindon masoya daga cikin garinmu da makota harma da ƴan birninku da suke zuwa kallon ajabin da aka halitta a wannan ƙauye namu, amma taƙi tsaida gwaninta.
Kwatsam sai Wannan shekara abar dogaro ta nunata matsayin sarauniyar ƴammatan shekara aikuwa maza suka rinƙa murna domin kowanne jarumi gani yake nasarar samun Tani tasace.

Haka muka dukufa shirye-shiryen wannan biki mukayi alibidi yafi kala goma Baba Uda da mahaifina Jimo har awaki da toron agwagi suka yanka mana dake haka al'adar take a gidan su sarauniyar ƴammata za'ayi girkin bawa gwarzon shekara.
Munata kaiwa da komowa munata hidima ranmu fes karma ni naji labari don ko hutawa banayi nakai na kawo ina tsokanar yaya Tani, abin dana fahimta saidai tayimin murmushi kawai idan na matsa mata sai ta kama hawaye inna tambayeta dalilin kukanta sai tacemin kawai tanajin tsoron a dauketa daga gari a kaita wani garin itadai tafiso mu kasance tare.
Idan ta fadi haka nima sai jikina yayi sanyi naji zuciyata ta karye mu hadu muyita kuka har sai Lamunde uwar Tani ta fatattakemu, ranar Wannan babban biki na al'ada daya zame mana idinmu mukayi kwalliya ta bam mamaki muka zauna a gda sai yamma muka nufi bakin kogi don mu ganewa idanunmu gwarzon mu muna tafe muna rera ƴan wakokin yabo ga abar dogaro domin gareta muke neman sa'ar wannan aure na ƴar'uwata Tani.

Tun a hanyarmu ta zuwa naji gabana yana faɗuwa  nadai dake ban faɗawa kowa ba bayan mun isa mun zauna gurin da aka tanada domin mu ina riƙe da hannun yaya Tani ina mammatsa matashi naji taja ajiyar zuciya tace “Habibah" na ɗago da sauri don tunda nake da ita bata taɓa kiran sunana ba saidai tace  dani Ƙanwa.
Idanunta naga yana zubar hawaye nayi saurin kai hannuna ina share mata ina girgiza mata kai ta riƙe hannu na tace “gabana yanata faɗuwa Habibah inajin kamar wani abu zai faru a gurin nan saboda jiya Liti ya rako Jamilu wannan ɗan birnin shine Jamilu  yake cemin bai iya su ba domin bai gada ba kuma har yanzu yananan akan bakansa na aurena babu ruwansa da kafirci na indai zan aureshi domin shima ba ibadar ya damu da itaba, yace naje na faɗawa su Baba Uda kada su bari a fara wasan nan tun a daren jiya su ɗaura mana aure idan kuwa sukaƙi to

shakka babu zaiyi kiran abokansa ƴan daba na Birni su ƙaddamar min ya rantse da Allansu abin dogaronsu indai ba'a bashi niba saiya barwa Tsaunin gawo tabon da har abada bazai goge ba" Sosai kalaman sun girgiza duniyata amma saboda son kwantar mata da hankali sai nace "kayya yaya Tani kinada sanya abu a ranki kada kibar wannan soki burutsun haukan nasa ya dameki babu abinda ya isa yayi Saida sahalewar abar dogaro kuma inada yaƙinin bazata wulaƙantamu ba"

Numfasawa tayi ta girgiza kanta tace "Hakane amma fa nikam na tsorata" da haka na rinƙa kwantar mata da hankali har zuwa wani lkc da aka buga tambarin nasara guri ya bushe da iface iface da kaɗe kaɗe da bushe bushe.
Kwatsam saijin ihun mutane muka rinƙayi ƙura ta tashi muna ganin yanda mutane suke runtumawa da gudu su kuma makasan suna ihu suna ina Amaryar yau sai sun kasheta... Ai bangama jin hakan ba na mike na kama hannun yaya Tani itama ta rikeni muka runtuma da gudu muka nitsa cikin daji ashe dama Mun san abinda muka tunkara da munyi tsaiwarmu a can kilan abar dogaro ta bamu kariya.
Muna gudu muna haki duk mun sassoke da kaya jikinmu ya kakkarce muka iso wata sarƙaƙiyar duhuwa muka tsaya muna mayar da numfashi, can mukaji motsi ta bayanmu yaya Tani ta rikoni don na sake ta na nufi wata magudanar ruwa zan ɗebo mata kasancewar nasan bata jurewa ƙishirwa, naji tace "Habibah da mutum anan mu gudu...." Bata ƙarasa ba suka bazar da ita a gurin ta saki ƙara nima na saki Jami ya diro daga kan wata itaceyar mangwaro muna ganinsa muka zaro idanu Tani harda ajiyar zuciya tayi tunanin me cetonmu ne nayi saurin kwacewa daga hannun wanda ya riƙeni na nufesa ina sauke numfashi nace "Yawwa Jami kayi mana rai kada su kashemu mun......"

Wata mahangurɓa ya sakarmin a baki yace "Shegiya kin ɗauka cetonku nazo kafiran banza kafiran wofi uwarme zan ceta a icen jahannama kalidina fiha abada Nima rabona nazo ɗiba na rama cin amanar da kuka yimin kuma agabanki zanyi komai kije ki faɗawa manyan kafiran nine Jamilun Alh Kabirun Auta muga wanda karansa yakai tsaikon da zaija damu a fadin ƙauyen nan...."
Yana faɗin haka ya dakawa wasu samari uku tsawa yace me kuke jirane kuyi aikinku" kafin na Ankara sun kamani sun ɗaure sun sanya wani tsumma sun rufemin baki sun watsar dani a karkashin bishiyar kusa da yaya Tani.
Yaya Tani ta fara yunkurin tashi Jami yasa ƙafarsa ya taka ƙirjinta ta saki wata kara da nima bansan sanda na saki ba duk da bakina a daure yake don nasan ta azaba ce"
Zamewa tayi ƙasa daga kan icen ta rushe da kuka shima ya sauko idanunsa sun kaɗa sunyi jawur jikinsa har rawa yakeyi yakai hannu zai taɓata sai kuma ya tuna ya janye yace "So....sorry please inajinki Habibah kinga dare ya fara" ɗagowa tayi ta sanya hannu ta riƙo hannunsa tace

“A gabana akan idanuna ɗan birni suka ketawa yar'uwata haddi suka keta alfarmarta sukayi mata kaca² su biyar ƙarata akanta ita kaɗai tana kuka tana Nishi tana gunjin azaba amma roƙonsu takeyi kada su taɓani kada su cutar dani, nima kuka nakeyi inata kokarin kwance kaina amma na kasa Saida suka gama abinda zasuyi Ikcn ta gama galabaita sannan suka kwanceni na angajesu da ƙarfin da bansan ina dashi ba na isa gareta ina kiran sunanta ina jijjigata suka tsallake mu sukayi tafiyarsu sunata ƙyaƙyala mana dariya.

Na jima ina jijjigata sannan dabara ta fadomin na cire kallabina na nufi wannan gulbin dana nufa dazu na jikoshi nazo ina danna mata a jikinta sai kuwa taja ajiyar zuciya ta fara buɗe idanunta daidai lokacin da samarin garinmu suka shigo jejin suna nemanmu ashe wani manomi yaga duk abinda ya faru ya bazama gdan sarki ya faɗa, hannunta ta ɗaga ta kamo nawa ta ɗora a saman ƙirjinta ta sake buɗe idanunta akaina taja wata ajiyar zuciya me ƙarfi shikenan jikinta ya saki ashe tafiyar kenan.
Tafiyar kenan ɗan birni tafiyar da ba'a dawowa tun daga wannan lokaci  na kamu da wata irin jinya da Saida na cinye wata bakwai ina kwance ba uhm ba uhm² saidai a kwantar a tayar haka akayita Shari'a akan wannan abin da ya faru amma babu nasara saboda baban Jamilu ya tsaya masa kasancewar shi kaɗai ya haifa kuma me kuɗin birni wannan dalilin yasa kwata² a cikin danginmu Bama ƙaunar mutanen birni ko kaɗan wlh ba ƙaramar wahala nasha ba da akace da Baba Uda anganni da ɗan birni cewa yayi ma da a ƙara bar musu mugun tabon da mutuwarsu ce zata rabasu dashi gara su su kasheni suji a ransu sune suka barranta kansu dani".............
[4/5, 9:11 PM] AM OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

https://youtube.com/channel/UCZ5Vt2--iGyJfTwItSzAnGg

Kamar yanda kuka sani ne ba wani sabon abu ba littafan OUM HAIRAN na kudine zaifi ki biya ki karanta cikin kwanciyar hankali, bana Miki/maka fatan kaci haƙƙin daba naka ba domin nasan Allah bazai bari ba musamman yanzu da zamu shiga wata me alfarma.
Ki biya ta waɗannan hanyoyin acct details 0255526235 Fauziyya Tasiu gtbank ko ku turo katin waya MTN ta WhatsApp number na kamar haka 09013718241. Normal group 300, Special 700.

*Page 6*

★★★~~~★★★~~~★★★

Tashi yayi daga tsugunnon da yayi yana sauke wata ajiyar zuciya me ƙarfi ya juya ya nufi hanyar da zata sadashi da masaukinsu, Saida yayi nisa sannan ya juyo yaga ta miƙe tsaye tana me binsa da kallo,
Juyowa yayi ya dawo ya tsaya a gabanta ya zubanta idanu tare da numfasawa ya kira sunanta da wata irin murya da tasa ƙirjinta bugawa da ƙarfi ta ɗago idanunta da suke tsiyayar da hawaye yasa hannu ya kama fuskarta yana goge mata idanun ya buɗe bakinsa da yayi masa nauyi yace “zaki auren....." Janyewa tayi dukan ƙirjinta na ƙaruwa tace “Aure...." Matsowa yayi gabanta ya damƙi hannunta yace “Yeah Beebah Aure zaki aureni koda danginki duka basu amince ba koda nima nawa bazasu amince ba kiji a ranki ke matata ce soon"
Sakin hannun nata yayi ya juya da sauri yabarta da sakakkiyar gwiwa data kasa turata ta kaita ko ƙofar gdansu saima guri data samu ta zauna ta zabga uban tagumi hannu biyu tanaci gaba da sharar hawayenta.

Ji tayi an daka mata tsawa ta zabura ta miƙe da sauri jikinta ya dauki rawa ganin Baba Uda tsaye a kanta taja baya da sauri ya kuwa tusota yana surfa mata ashar yana cewa “wato ke kunnen ƙashi ke gareki bakijin mgn ko to muje gdan uban naki naji daga inda kika samu ɗaurin gindin kula wannan ɗan iskan yaron me siffar munafukai"
Da gudu ta shiga gdan kamar an jefota Jumme da Jimo dukkansu suka miƙe ganin Baba Uda yasa Jumme shigewa ɗaki yaci gaba da sababinsa yanata kundume² ashariya.

Cikin girmamawa Jima ya ɗago ya dubesa yace “Nifa yaya ban fahimci abinda kake nufi ba" “Eh ai dama bazaka gane ba nasani bazaka gane ba Jimo ka saki yarinyar nan sasakai abinda taga dama shine takeyi kaƙi matsa mata ta fitar da miji bare batun aure yanzu gashi garin sakacinka taje ta janyo mana abinda zai kashem" da bayannaniyar rashin fahimta Jimo yace “menene Yaya ka sanar dani" numfasawa yayi yace “wai har gida akaje akace min yarinyar nan Bibo anganta ita da ɗaya cikin bakin nan da dagaci yasa akayi shelar zuwansu ƙauyen nan haƙar ma'adanai...."
Tafa hannuwa Baba Jimo ya shigayi yana girgiza kai kawai sai yayi wuf ya cafko Habibah ya rufe ta da duka ta saki ihun daya janyo hankalin mutanen da suke wuccewa gidan ya cika da

mutane daƙyar aka kwaceta hannun Baba Jimo yana haki yace “Ni zaki tozarta Habibatu kwana huɗun can nayi Miki kashedi akan wannan yaron da labari yazo min yana binki gona shine ya sake canza salon yaudararsa to na rantse da abar dogaro kasheki zanyi Habibah yankaki zanyi da wuƙa na jefaki a rijiyar jeji domin bazaki zamemin haihuwar asara ba...."

Kuka takeyi tana matsawa daga inda take tsaye tana shirin fita Baba Uda ya cafko ta ta rushe da kuka tace “kada ku kasheni bansan meye yasa bana iya bijire masa ba yana kalaminsa da hankali kalaminsa na nutsuwa ne komansa a nutse yake bashi da hayaniya ku fahimceshi da gaske ba irin Jami...." Zubewa tayi ƙasa hancinta da bakinta suna zubar da jini tsallaketa sukayi suka bar gurin dukkansu da bayyananniyar damuwa a fuskarsu kai tsaye gdan dagaci suka nufa idan ka gansu zaka zata korarru ne.
A ƙofar gida sukaga dagaci tare da baƙi suka tsaya a nesa dashi suna tattaunawa bayan dagaci ya gama sallamar baƙinsa ya ƙarasa garesu suka gaisa yayi musu iso zuwa fadarsa ya dubesu yace “yanayi ya nuna kuna cikin damuwa meye yake tafe daku?"
Numfasawa Uda yayi yace “damuwa babba ma kuwa ranka shi daɗe wato tun farko Saida mukace bamasan sauke baƙi a garin nan aka nuna mana bamu isa ba saboda baku abin yake shafa ba yanzu ga abinda hakan yake neman haifar wa wani a cikinsu yana neman lalata mana tarbiyyar ƴar wajen ɗan'uwana Bibo nasan dai kasan Bibo...."

Nan suka kwashe duk abinda aka faɗa musu ƙarya da gaskiya suka zayyane masa ya jinjina abin yayi shiru yana tunanin mafita can ya ɗago ya dubesu yace “yanzu dai zamu kira yaron gobe da safe jimo Uda kuje gda zamu nemeku"
Miƙewa sukayi sukayi bankwana suka tafi ranar kwana sukayi suna saƙa irin matakin da zasu ɗauka akan Habeeb.
Kwana tayi jikinta yana ciwo tana kuka Jumme nayi mata faɗan dalilin da yasa bataji kashedin da iyayen nata sukayi mata ba, cikin kukan tace “Nifa bani nace yazo ba kuma bani nake kulashi ba shine yake kulani sannan Jumme kece kike cemin babu kyau wulakanta mutum bare sh....." Katseta tayi da cewa “naji banason ji nidai na faɗa Miki indai kinason naci gaba da sanya Miki albarka to ki fita daga harkar wannan ɗan birni ba sonki yakeba cutar ki zaiyi ina me tabbatar Miki duk dariyar da ɗan birni zaiyiwa na ƙauye cutarsa zaiyi saboda haka ki kula da kanki”

******

Washegari da safe a fada Baba Uda ya miƙe ya zabgawa Habeeb Mari Najeeb ya miƙe da sauri yayo kansa Habeeb ya riƙe shi da sauri, nunashi Baba Uda yayi yace "Ƙarya kakeyi yaro baka isaba kayi kaɗan ka koma gurin munafukan da suka turoka ka faɗa musu kaidai baka isa mu baka aure ba kai bakai ba wani ma da yafika kama da galihu muddin daga birni ya fito bai isa mu ɗauki jininmu mu bashi ba haba! haba!! Yaro aikai tawayar ma tayi maka yawa gaka musulmi kuma a zuri'ar mu kaje ka nema dai a wani gurin Habeeba tafi ƙarfinka"
Ɗagowa Habeeb yayi ya dubi Uda yace "kayi hƙr Baba bani na jarabci kaina da son Beebah ba Allah ne ya jarabceni inasonta kuma itama alama ta nuna ta karɓeni duk abinda kuke tunani bazaku sameshi daga gareni ba"
Dariya Uda yayi yace "ƙaryar banza to bazamu bayar ba son ya kasheka in yana kisa mune sai muka haifi Habeeba munce bazamu bayar ba"

Miƙewa sukayi suka fice daga fadar suna ƙunkuni suna Harbin iska suna zuwa gdan kuwa suka gindaya mata sharruɗa tare da sanya mata sarka a ƙafarta gabadaya sun haramta mata fita daga gda hakan bai wani dameta ba tayi jinyar jikinta kwana biyu ta warke kullum saidai su Kande suzo su bata lbrn abinda ya faru a dandali da kuma halin da Habeeb yake ciki na irin damuwar da yayi da rashinta saidai tayi murmushi kawai ta share don tasan ajalinta ne kawai zaisa tayi karambanin fita daga wannan gida.
Kullum sai Habeeb yazo ƙofar gidansu Bibo haka Baba Uda da Baba Jimo zasuyi masa korar kare gashi da baƙin naci yaƙi hƙr haka yayita zarya tsakanin masaukinsu da gdansu amma ganinta yafi ƙarfinsa saidai ya gaji da aikensa da magiyarsa ya hƙr ya koma ya zama kamar wani zautacce cikin abinda bai rufa wata guda ba ƴa macen da yake ɗauka ba'a bakin komai ba macen da abaya yake ganin bazai iya sanyata cikin rayuwarsa ba sai gashi cikin lkcn da bai shirya ba bai tsammata ba ta faɗo rayuwarsa tana sauya masa taswirar rayuwa.

Sosai Najeeb ya mayar dashi mahaukaci baya bawa duk wani abu daya shafi Habeeba muhimmanci ko zama sukayi suna tattaunawa abinka da abinda ya damu ruhin mutum indai Habeeb zai sako shafin Beebah cikin hirar to zata ƙare domin Najeeb zai kama faɗar maganganun da in yayi wasa ranar ko ɗaki ɗaya bazasu kwana da Habeeb ba wannan tasa suka raba tsaki da Najeeb mgn ma sai ta zama dole Habeeb ke tsayawa suyi da Najeeb haka dai lkc yayita tafiya duk wata hanya da yake ganin zata zame masa me sauƙi wajen haɗuwa da Habeeba ya rasa dole yaja ya dangana da gdan hakimi da rasa masa kuka yana roƙonsa ko nawa sukeso kome sukeso matsayin sadakin Habeeba a sanar dashi zai bayar kuma yayi alƙawarin matukar ba ita taso musulunci ba bazai rabata da addininta ba.
A zahiri Mati Dagaci yaji matukar tausayin Habeeb musamman dake yana yawan kawo masa gaisuwa yasanshi yana lura da yanda ya susuce ko aikin daya kawo shi garin ya dainayi shikenan daga ka sameshi a bakin kogi ya zubawa ruwa idanu saidai ace anganshi a jeji a zaune ko kuma yana gda yana karanta wasiƙar jaki.
Ɗagowa Mati Dagaci yayi yace "Yaro hakikanin gaskiya duk da bambanci addini naji tausayinka

matuƙa domin so mugun ciwo ne da bashida magani sai saidai samun abinda zuciya ta kwaɗaitu dashi Habibu banida maganin matsalarka na rantse da Allanku da Bibo ƴata ce nice na haife ta a yau bazaka bar gurin nan ba saina bawa Limamin Hayin Fulani damar ɗaura muku aure bisa tsarin addininku amma kash banida wannan damar”
Numfasawa Dagaci Mati yayi ya sake duban Habeeb da idanunsa suka rine suka koma jajaye yace “duk da haka bazan kashe maka gwiwa ba kaje kaci gaba da addu'ar kasa malaman addininku su tayaka Habeebu inda rai da rabo"

Miƙewa yayi cikin mutuwar jiki yace “Shikenan Baba Dagaci na gde amma bazan iya ci gaba da zama a garin nan ba zan koma Garinmu saidai inason kafin na tafi kayimin alfarma ɗaya” da sigar tausayi Dagaci yace “Wacce iri ce Habeebu" sunkuyar da kansa yayi yace “Ka aika a kira Habeebah nasan idan Baba Jimo yaji kiran nakane zai barta ta fito inason magana da ita kalma ɗaya tak nakeson ji daga gareta wlh indai har Habeebah tace bata sona zan hƙr da ita domin nasan ƙaddarar sai soyayyarta ta wahalar dani ce tasa na zaɓi wannan garin matsayin inda zanzo idan kuwa ta amsa min tanasona to ko duk dangina da nata zasu ƙare saina mallaketa domin itaɗin mahaɗin raina ce"
Shiru Dagaci yayi yana jinjina kalaman can ya ɗago yace “shikenan Sarkin zagi tashi kaje ka sanar munason ganin Bibo yanzu a gabanmu" babu ɓata lkc sai gata tun daga nesa ya kafeta da manyan idanunsa da suka rine da damuwa itama shi take kallo ganin ya zabura ya miƙe yasata tsayawa a inda take jikinta ya ɗauki ɓari saboda tuna mugun kashedin da Baba Uda yayi mata.
Ji takeyi kamar ta juya amma batada ƙarfin gwiwar hakan domin Zuciyarta tana kwaɗayin ganin ɗan birni ko ba komai tasan zata samu sauƙin abinda take ji a ƙasan ruhinta.
Takowa yayi gabanta ya tsaya ta gyara tsayuwarta cikin dakiyar zuciya ta dubesa kafin yayi mgn ta rigashi da cewa “Dan birni meye ya sameka ka rame kamar kayi jinya?" Tana mgnr tanakai hannunta fuskarsa ta shafa ƙasumbarsa da ta kwana biyu bai gyarata ba hakan yasashi lumshe idanunsa ya kamo hannun nata yayi kissing nasa yace “Ha... Habee..bah kina iya rayuwa me daɗi batare da kinsan halin da nake ciki ba?" Da rashin fahimta ta dubesa zatayi mgn ya ɗora yatsansa a saman bakinta yace zo muje inason tambayarki ne a gaban Dagaci duk amsar da kika bani ita ce zatayi aiki wajen sama mana mafita Ni dake baki ɗaya"

Kama hannunta yayi suka isa gaban Dagaci suka zauna Dagaci ya dubeta yace “Habeebah kwana biyu kin ɓuya ɗan goron ma da ake siyowa a kawomin na toshi an daina kodai an daina auren dani ne?" Murmushi tayi tayi ƙasa da kanta tace “Aa su Baba ne suka tsareni suka hanani fit...." Girgiza kai yayi yace “to ai shikenan dama Habeebu ne yakeson ganinki zai koma garinsu yanaso kuyi sallama" ɗagowa tayi tace “Habeeb!"
Ɗagowa yayi tare da jinjina mata kai yace “Sunanan kenan Habeeba don Allah ki nutsu ki bani

amsa ɗaya tak ita kaɗai nake buƙata daga gareki kada ki cutar da kanki ki faɗa min iyakar gskyr abinda ke ranki game dani Habeebah kinaso na?"

Ɗagowa tayi da sauri ta kalleshi shima itan yake kallo cikin tsoro ta kawar dakai gabanta na faduwa ta miƙe ya riƙe Rigarta ta baya yace “Wlh bazaki bar gurin nan ba saikin amsa min tambayar nan don itace hadafin mafita ta Habibah kalma ɗaya ce eh ko a'a zata cireni a zullumi sannan zata ƙarfafamin gwiwa Please ki faɗamin matsayin da kika ajeni kinasona zaki aureni ko baki sona?" Ido ta zubawa Baba Uda sake shigowa zauren majalisar dagacin shima ya kafeta da idanu yana nufosu tana ƙoƙarin ture Habeeb ta kasa saima riƙon tsauri daya ƙara yima damtsanta wata ƙara kakeji kau... Kau... Abinda yasata saurin sauke idanunta kan babanta Jimo dake tsaye da wani yaro Lanti ya zare wuƙa yayi kan Habeeb Najeeb ya taso da gudu ya nufosu ya riƙe wuƙar ta yanke shi hakan yasa ya saki ya sake nufar Bibo da Habeeb ya ɗaga wuƙar zai cakawa Habeeb Bibo tayi hanzarin tureshi wuƙar ta soke ta a gefen cikinta take ta saki wata ƙara me nuni da irin azabar da taji hakan yasa Habeeb juyowa don shi kwata² baima lura da dalilin tureshin da tayi ba.

Ganinta a ƙasa a zube cikin jini yasashi sakin ihu da dira kanta ya ɗagota yana jijjigata yana kiran sunanta yana cewa “Habeebah wayyoh matata don Allah kada ki mutu bamu cika burinmu ba wlh in kika mutu nima mutuwa zanyi....." Sunkutarta Najeeb yayi suka fice da ita da mugun gudu suka nufi gdansu Dagaci yana biye dasu saboda haukan iyayen Habibah ya wucce tunaninsa baitaɓa tunanin da gaske sukeyi zasu iya kashe ƴarsu da hannunsu ba.
Tun a hanya suka rinƙa kiran James dake babban likita ne shine yake kula da lfyrsu suna zuwa ya dira akanta ya fara treatment nata sai bayan ya gama sannan su Jimo suka shigo Jumme ta shiga ɗakin da sauri ta faɗa kan Habeebah da take farfaɗo wa yanzu tana faɗin shikenan nikam rayuwata ta lalace Jimo zaka kashe mana ƴarmu ɗaya tilo akan wani bare meye yasa kukeson kubawa zuciya dama ta barku da nadama...."
Ajiyar zuciyar da Bibo ta sauke ce ta sanya Habeeb saurin tashi daga inda yake ya nufeta ta kuwa buɗe idanunta akansa ya riƙe hannunta yana jera mata sannu ta sake ƙanƙame hannunsa cikin kuka da Muryar jinya da wahala tace “Meye ribata idan banbi wanda naji a raina zan iya sadaukar da rayuwata don kare tasa ba? Habeeb bazan zauna dasu Baba Uda ba inka tafi kasheni zasuyi ka tafi dani garinku na amince zan aureka ina sonk....." Tsalle Jimo yayi ya haye ruwan cikinta ya naushi bakinta jini yayi tsartuwa zuwa sama ........
[4/7, 9:16 PM] AM OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

https://youtube.com/channel/UCZ5Vt2--iGyJfTwItSzAnGg

*Paid book*
Ki biya ta waɗannan hanyoyin acct details 0255526235 Fauziyya Tasiu gtbank ko ku turo katin waya MTN ta WhatsApp number na kamar haka 09013718241. Normal group 300, Special 700.

*Free Page 7*

★★★~~~★★★~~~★★★

Ya wankewa Habeeb fuska da yake ta kokarin daga Jimo a kan cikinta daƙyar aka ƙwaceta don cewa yayi kasheta zaiyi ya huta da baƙin ciki ya furta da haihuwar Habibah Gara ɓarinta yafi sau ba adadi, Jumme banda kuka babu abinda takeyi saboda tunda take a rayuwarta bata taɓa hasaso tashin hankali kwatankwacin wannan ba, rayuwa sukeyi me daɗi wacce ta cika da kwanciyar hankali da rufin asiri sunason junansu da ƙaunar farin cikin juna.
Yau gashi rana a tsaka komai ya goce tabbas Habibah takai mahaifinta ƙarshe don kuwa a tarihin rayuwa bai taɓa yi mata irin bugun mutuwar da yayi mata yau ba bare kuma har a halin jinya ita wannan wacce irin ƙiyayya suke yiwa mutanen birni da har suka zabi kashe tasu akansa? Tambayoyin da suke ta yawo a ranta kenan batada me bata amsa don zuwa yanzu ta rayuwar Habibah akeyi da ta shiga wani yanayi na buƙatar agajin gaggawa, a wannan yanayin James ya dubi Habeeb da jikinsa ya keta rawa tabbas badon Jimo haihuwar Beebah yayi ba da babu abinda zai hanashi rama mata wannan dukan zalumcin da yayi mata.

Hararar juna kawai akeyi tsakaninsa da Najeeb duk da cewa Najeeb ya fara saukowa yana ɗan tausaya masa akan wannan soyayya ta masifa daya faɗa ciki amma abubuwan da suka faru yau yasa yaji ya ƙara tsanar Habiba da garin Tsaunin gawo sukam wanne lefin sukayiwa Allah ya jefosu wannan gari na arna marasa imani waɗanda suke jin a ransu zasu iya kashe jininsu don wani dalili nasu mara kan gado? Ya rasa wacce jaraba Habeeb ya liƙewa jikin yarinyar duk da yasan ta fita babu algus ta zanu ba ƙarya amma a tunaninsa sai yaga batakai yayi wannan haukacewar akanta ba meye ma abinso a mutum mara gamsasshiyar nasaba?

Wannan tunanin yasashi yin tsaki ya fice daga ɗakin daidai lokacin da Jimo shima ya hassalo ya matsa zai sunkuci Beebah Habeeb yayi saurin dakatar dashi ta hanyar dafe ƙirjinsa suka kalli juna cikin mugun bacin rai yace “karka taɓata na rantse da Allah idan ka taɓata sai nasa an ɗaureka" baƙauyen mutum da tsoron tozarcin hukuma hakan tasa Jimo da Uda komawa gefe suna huci kamar wasu mayunwatan zakoki.

Da haka aka samu ta dawo cikin nutsuwarta ta sauke ajiyar zuciya tare da buɗe idanunta Jumme ta matso gabanta da sauri tace “Bibo kin tashi sannu..." Juyowa tayi ta kama hannu Jumme ta kafe Habeeb da ido shima ita yake kallo ya sakar mata wani tsadadden murmushi daya sanya jikinta mutuwa ya tako ya sunkuyo kanta yace “Inane yake ciwo?" Lumshe idanunta tayi ta kawar dakai yaja numfashi yace “karki damu komai zai hucce soon Ni kaina nasan akwai yaki a gabana amma zan jure don ke Beebah indai zan sameki wlh duk wata wahala zan ɗauketa"

Fincikota Uda yayi ta zube a ƙasa baya ko tunanin ciwon dake cikinta wannan abun ya hassala Dagaci ya daka masa tsawa yace “Wai meye yake damunku ne ko an faɗa muku ƙiyayya haukace da zaku nemi kashe yarinyar nan meye laifinta akan abinda ba ita ta dasawa kanta ba to wlh ku dawo hayyacinku ku kiyayeni idan kuka fusatani tsaf zan yanke hukuncin da bazai muku daɗi ba sakarkaru"
Sakinta sukayi sarai sun san halin Mati idan suka fusatashi babu abinda bazai iya yi ba shiyasa suke shayinsa, miƙewa tayi ta nufi Jumme ta faɗa jikinta ta rungumeta tana kuka tace “Jumme kema baki sonsa" ajiyar numfashi tayi tace “Inasonsa mana tunda kina sonsa Uwata nidai nafison kiyiwa iyayenki biyayya bazasu cutar dake ba ki cire komai a ranki bakida gatan da yafisu" ɗagowa tayi taga idanunsa akanta tayi ƙasa da nata ya matso ya riƙo hannunta yace “Kada ki sanya damuwa a ranki ki kulamin da kanki nabar amanarki gurin Dagaci zan dawo bada jimawa ba zamu mallaki juna soon insha Allahu"

Janye hannunta tayi daga nasa Dagaci ya kamata suka fice ya nufi gidansa yanata faɗa kamar zai ari baki, suna shiga ya fara ƙwalawa uwargidansa kira ta fito daga Madafi tace “gani Mati meye yakar buzu da ranar Allah?" Mika mata Bibo yayi yace “Marka ga Habiba nan ki bata kulawa da tsaro daganan zuwa lkcn da ƙura zata lafa nan ya kwashe lbrn komai ya sanar mata ta tafa hannu tace “To banda abinsu shi wannan lamari ai abin asa idanu aga ikon me sama ne yaran nan ba wanda ya haɗasu su suka haɗa kansu Inma mutum yace zai raba saidai yasha wahala bare ma meye laifin Habibu yaron kirki da hayaniyar ma ba damunsa tayi ba kagani fa Mati tunda suka zo garinnan kullum sai yazo ya gaisheni da ɗan alkhairinsa to maji ma gani wai an binne rayayye"

Kama hannu Bibo tayi suka shiga daki ta nufi madafin ta haɗa ruwa me ɗumi ta kamata suka nufi bayi da kanta ta rinƙa gasa mata jikinta tun tana wash$^{2}$ har ta dawo tanajin daɗin ruwan.

Suna zaune Marka na shafe mata ƙafafu da mai me gurguwa ya shigo da sallamarsa babu wanda ya amsa sai maraba da Marka tayi masa suka gaisa tace “Habibu ɗan makaranta ashe kuma haka abu ya faru babu daɗi sai hƙr kasan mutanen namu ne sai shiru sai saurare basuda dadin sha'anin akan abinda suka jahilta musamman irin gidan Sarkin Noma Nomau tsaurinsu akan ra'ayinsu yayi yawa"

Murmushinsa yayi me daraja idanunsa akan Beebah data daga kanta sama tazuba idanunta akan rufin azarar dake ɗakin yace “Zai wucce kamar ma ba'ayin ba Baba Marka nidai roƙona ki kulamin da ita kafin na dawo ba jimawa zanyi ba inason naje na shirya komai ne ayi a wucce gurin idan na ɗauke ta dai inace shikenan?”

“Shikenan kuwa yaro” Marka ta faɗa ya janyo ledojin daya shigo dasu ya miƙawa Marka yace “magungunanta ne Dagaci yasan yanda ake amfani dasu Baba Marka a kula wajen shansu, naga nan kunada service ga waya nan ƙarama nasa layi ta rike a hannunta saboda in rinƙajin lfyrta kafin na dawo ba jimawa zanyi insha Allahu"

Buɗe ɗaya ledar yayi tsire ne sai tiriri yakeyi duk ya cika dakin da ƙamshi ya ɗauka ya kai mata bakinta.

Kautar dakai tayi ta kalli Marka itama kau dakai tayi ta miƙe ta fice musu daga ɗakin yayi murmushinsa me cike da isa yace “Bazakici ba?" Daga masa kai tayi ya sake ɗaukowa yakai bakinsa ya tauna yace “kuma kinga sai kinci tunda kikace kina sona" miƙewa yayi ya zagaya bayanta batayi aune ba kawai sai jinta tayi kwance a ƙirjinsa ya daga kanta ya riƙe sosai yanda bazata iya ƙwacewa ba ya sanya bakinsa cikin nata ta kuwa rintse idonta da ƙarfi cikin wata masifaffiyar faɗuwar gaba da tashin hankali ta rinƙa kiciniyar ƙwacewa shi kuma ya matseta ya lumshe idanunsa yana sake saƙalo harshen ta me masifar zaƙi yana fitar da wani numfashi me wuyar fahimta yana kusa sake shigar da ita jikinsa ya saki fuskarta don yasan yayiwa bakinta riƙon da bazata iya ƙwacewa ba ya sanya hannunsa tsakanin ƙirjinta da cikinta shafaffe wanda zaka iya rantse wa bata sanya masa komai.

Yawo yake da hannun a hankali tsakanin cibiyarta da ƙirjinta yana son kaishi ga kyakkyawar dukiyar fulaninta dake tsaye kam kamar zasu tsonewa mutum idanu duk da bata taɓa sanya musu bra ba a tsayin shekarunta sha bakwai a duniya amma hakan baisa sunyi komi ba.....

Wata zabura yaji tayi tare da shiɗewa Ikcn da ya ɗora hannunsa kan yar ƙaramar rigar data rufe su dasu hakan yasashi saurin janye hannunsa ya cire bakinsa daga nata yana sharce gumi

gabadaya jikinsa ya mutu murus sai zufa dake karyo masa ta ƙofofin gashin jikinsa, wata ajiyar zuciya yaja me ƙarfi yana arowa kansa juriya yana sawa kansa ya sake ta ta janye  jikinta sai rawar mazari yake ƙirjinta kuwa banda bugawa babu abinda yakeyi ta zabura ta miƙe zata runtuma da gudu yayi saurin riƙota ta zame ta rushe masa da kuka yayi saurin zama yace "Nikam banason kuka wlh Beebah meye na kukan?" Tureshi tayi da ƙafarta tace "na daina sonka tunda kaima irinsu Jami ne haka sukayita sa nonon Tani a bakinsu suna matsa mata shi da hannunsu shine kaima zakayimin to banasonka...."
Da sauri ya rufe mata baki yace "Ya isa Ni ba irinsu bane Beebah na daina kiyi shiru karki faɗawa kowa muje kici abincin yau banga sanda kikaci abinci ba" noƙe kafada shima noƙewa yayi ta rufe idanunta tana dariya, dariyar tata ta sashi dariya ya cafko hannunta ya zauna da ita da lallami ya samu taci tsoka uku ganin taƙi sakewa taci a gabansa ya sashi karkacewa ya zaro kuɗi yan ɗari biyu rafa guda ya bata yace "ki riƙe a hannun ki saboda sa kati ban yarda a kira kowa ba bayan Ni" zaro wayar yayi da kwalayen turare ya aje mata ya miƙe ya kama hannunta ya sumbata ya fice da sauri saboda ganin idanunta ya kawo ruwa yasan tsaf zata karya masa gwiwa gara karma ya tsaya domin tafiyar tasa tafi zamansa muhimmanci........

*Share please*
[4/9, 6:25 PM] AM OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

https://youtube.com/channel/UCZ5Vt2--iGyJfTwItSzAnGg

*Paid book*
Ki biya ta waɗannan hanyoyin acct details 0255526235 Fauziyya Tasiu gtbank ko ku turo katin waya MTN ta WhatsApp number na kamar haka 09013718241. Normal group 300, Special 700.

*Free Page 8*

★★★~~~★★★~~~★★★

Koda ya fito tsakar gdan Saida ya bawa Marka kasonta sannan ya ƙara mata wasu masu tsoka da zata kula masa da habibansa kafin ya dawo duk da ya ƙudurce a ransa bazai daɗe ba hakan bai hanashi jin kewar abar ƙaunar tasa ba,
Cikin ƙaramin Ikc yayi sabo da ita sabon da yake jin zagawarta a cikin jininsa yanajin zuciyarta na bugawa daidai da bugun tasa zuciyar, yana shiga masauki jakar kayansa kawai ya ɗauka drivern campanyn simintin na mahaifinsa ya ɗauke su suka ɗauki hanyar Dutse tsakanin Tsaunin gawo da Birnin Dutse tafiya ce ta gaske kasancewar Tsaunin gawo cikin ƙasar Kano take a rankin wata babbar ƙaramar hukuma.
Sun gajiya Ikcn da suka shiga Dutse dare yayi nisa wannan tasa ba kowa ne yasan da dawowarsu ba, kai tsaye sashinsa ya nufa ya watsa ruwa yayi sallar magrib da Isha ya kwanta yana hucce gajiya amma zuciyarsa taki barinsa a Jigawa ta ɗauke shi ta mayar dashi Tsaunin gawo, hakanan ya wanzu yanata murmushi yana tunano irin wani yanayi da ya tsinci kansa ɗazu da yana kissing kyakkyawan bakin Beebansa tabbas akwai nutsuwa a cikin kasancewa da abinda zuci take muradi dole yayi bakin kokarinsa yaga ya mallaki Beebah bada jimawa ba ko ya samu zuciyarsa ta samu salama.

Da waɗannan tunane² bacci ya ɗauke shi me sihirtaccen daɗi cike da mafarkin abar ƙaunarsa cikin kyakkyawan yanayi wanda ya sanyashi jin shauƙin kasancewarsu tare aikam yana tashi da asuba ya watsa ruwa ya sanya doguwar riga ya nufi masallacin cikin gdan sarautar sai Ikcn ƴan'uwa barori da kuyangi suka fahimci ashe autan Kilishi ya dawo Auta me dakawa maza gumbar wuya a hannu.
Kaffatan duk wani ma'aikaci dake cikin wannan gda yana masifar shayinsa bawai don tsabar zalumcinsa ba a'a saidai don masifar kwarjininsa ko kusa baya ɗaukar raini da wargi tun ma yana ƙarami bare yanzu da yake jinsa sama da kowa a duniya.
Bayan idar da sallah kamar yanda al'adar gdan take Saida suka gama gaisawa da juna ƴan'uwansa sunata yi masa sannu da zuwa yanata jin daɗi duk da kacokan hankalinsa yanaga Mai martaba domin shine dalilin zamansa so yakeyi ya samu damar magana dashi a yau ɗin nan.
Shi a burinsa ma baya fatan maganar aurensa da Beebah ta wucce wata guda saboda ji yakeyi kamar zai iya zautuwa idan bai sameta ba.

Mai martaba yana karɓar gaisuwa fiye da rabi na hankalinsa yanakan Habeeb tabbas da yanayi ya fahimci ɗan nasa yana cikin damuwa domin ya rame sosai ga wani duhu da yayi kamar wanda ya tashi daga jinya, Saida Sarki Khalil ya sallami kowa sannan yayi gyaran murya yace “Habibullahi an dawo lfy ya aikin muna fatan komai ya tafi yanda muka tsara?"

Ƙasa yayi da kansa yace “Muna fatan hakan Allah yaja kwananka..." Shiru ce ta ɗan ratsa har yanzu mai martaba kallonsa yakeyi can ya numfasa yace “Kayi rashin Ify ne?" Da sauri ya ɗago yana duban kansa ashe dai da gaske Najeeb yakeyi ya rame ɗin shi rabonsa da duba madubi har ya manta bare yaga yanayinsa.
“Muna sauraronka Habibullah" abinda mai martaba ya faɗa kenan hakan ya bawa Habeeb damar karkacewa cike da faɗuwar gaba ya lankwashe kafa kamar me neman gafara yace “Allah ya taimakeka dama mgnr da kuka daɗe kunayi min ce ta taso game da aure...." Sai kuma yayi shiru kamar me jin tsoron furtawa, murmushi Mai martaba Khalil yayi yace “Masha Allah ai dama hakan muke fata Habibu naji daɗin wannan labari a ina take, ya sunanta kuma ƴar waye a ƙasar nan sannan meye matakin karatun ta ɓangaren Islama da boko?......"

Dam gabansa ya buga kwata² ya manta da dokar gidan nasu na cewa macen aure sai saukakkiya wacce ta karanta ƙur'ani kuma ta haddace koda uzufi talatin ne a kanta matakin karatun boko degree sannan ba ƴar kowanne mutum ake kawowa gdannan ba sai wanda aka san sunansa a ƙasar, itako Beebah batada komai gata ba ƴar kowa ba gata ba musulma ba bare ayi maganar karatun Kur'ani  boko kuwa ba itaba duk garinsu ma baiga wanda yayi ko gaba da primary ba.
Wani gwauron numfashi ya sauke lkcn da mai martaba ya katseshi da cewa “ka samu a gaba kayi mana shiru ko abin faɗarka ya ƙare ne?" “Ba musulma bace....." Ya faɗa cikin son arowa kansa dakiya, wannan kalma ta sanya mai martaba saurin ɗagowa yace “Wht? Ya Salam subhanallah Habeeb wannan ai zancen banza da wofi ne da bazai yiwu ba kafira kuma kakeso zaka auro mana cikin zuri'armu don taɓewa da lalacewa...."

Da sauri ya ɗago kalmar kafirar nan na mugun taɓa zuciyarsa miƙewa Mai martaba yayi ya saɓa babbar rigarsa ya nufi hanyar da zata fitar dashi daga masallacin Habeeb yayi saurin miƙewa yasha gabansa ya zube yace “Kayimin rai ka fahimceni wlh Mai martaba inason Habeebah itama tanasona nasan zata iyayin komai donni bana ko tantama zata musuluntа duk abinda ake nema zata samu nidai burina ku yarda na aurota Allah ya taimakeka ka taimaka min wajen wannan jihadin wlh saboda Ni Beebah har gdan iyayenta ta bari yanzu haka tana gdan Sarkin garinsu....."
Ɗaukeshi da mari Mai martaba yayi ya nunashi da yatsa zaiyi mgn takaici da bakin ciki ya hanashi iya cewa komai ya fice da sauri daga masallacin ya sake binsa yana masa magiya bai saurareshi ba ya shige sashinsa ya datso ƙofarsa take Habeeb ya zube a gurin zuciyarsa na tafasa tabbas wannan shine ake cewa yaƙi saida uwa shikam baiga laifinsa ba cikin son farantawa zuciyarsa na auren Beebah ba kuma baiga dalilin da zaisashi janyewa daga ra'ayinsa a faɗin duniyar nan ba.
Da wannan ya juya ya koma ɗakinsa ya rinka zagayashi yana dukan iska zuciyarsa tana masa

wani mugun tuƙuƙi daya kasa samawa sassauci.

Wanka yayi ya sanya kayansa ya nufi cikin gdan fuskar nan kamar hadari saboda damuwar dake danƙare a ƙasanta Saida ya shiga ko ina suka gaisa yanayinsa yasa babu wanda ya tankasa sunsan yanzun rai zai ɓaci, ɓangaren Kilishi ya nufa ya ƙwankwasa ƙofar tana zaune saman sallaya da ƙur'ani me tsarki a hannunta tana muraja ya shigo ya samu guri ya zauna ta dubeshi ta mayar da hankalinta ga karatun ta.
Saida ta ida inda takeson tsayawa sannan ta ɗago ta dubeshi tace "Autan maza Ina ka shiga ne tun jiya naji Ibrn dawowarka sabanin ko yaushe baka zomin ba" ajiyar zuciya yayi ya ɗago idanunsa sun kaɗa sunyi jawur ya sauke ajiyar zuciya da tasa gaban Hajiya Kilishi faɗuwa tace "naga ta kaina Ni Ummusalma Habibu na meye ya sameka ne naganka a ɗefare a lalace kamar kayi jinya?"
Sunkuyar da kansa yayi yana wasa da yatsansa ta kafesa da idanunta tana mamakin ramar ɗan nata tace "Habibu! Ɗagowa yayi ga mamakinta sai taga hawaye sharrrr a idanunsa gabanta ya faɗi tace "Ina dalilin hawayen?" Numfasawa yayi taja fasali tace "to tashi kaje bazakazo ka tayarmin da hankali ba bayan bankai sanin damuwarka ba...." Saurin ɗagowa yayi yace "Ba haka bane Hajiya kawai dai ina tsoron kema kada kiƙi fahimtata kamar yanda mai martaba yaƙi tsayawa ya fahimceni ne!"

Murmushinta na Dattaku tayi tace "Habibu kenan ai indai kaga ban fahimceka ba to yanayin da kazo dashi ne baiyi daidai da a fahimceka ba maza ina sauraronka" numfashi ya sauke nan ya zayyane mata komai taja wata ajiyar zuciya me ƙarfin gaske tayi kasaƙe tana tunana wannan gingimemen aikin da Habib ya kinkimo duk da bataji taƙi abin a ranta ba duba da dalilin daya zayyana mata amma ta hango hargitsi na gaske a tafiyar tabbas kafin aci Zomo sai anci gudu tunda mai martaba yaki fahimtar Habeeb to batasan kuma waye zai samu nasarar fahimtar dashi ba, tunda yaki wannan lamari bataga wanda zaisa yasoshi ba saidai in Allah yayi to ikonsa sai yasa ya rusuna yabi ko bayaso.
Sosai jikin Habeeb ya ƙara sanyi lakwas yace "Hajiya kinyi shiru don Allah kice kuma kisa albarka da bakinki me albarka inada tabbacin indai kika yarda kuma kika bani goyon baya Allah zai amince kuma zamu samu lada in har Habeebah ta yarda ta karbi addinin Musulunci Hajiya ki duba ladan da zaki samu ki aminta ki cire kokwanto"

Taguminta ta janye ta ɗago ta zubansa idanunta tayi masa murmushi na karfafa gwiwa tace "Na baka goyon baya Habib kaje ka nemi auren Habibah ka aurota ku rayu cikin aminci amma fah ina horon ka da kabi komai a hankali Kuma kayiwa mahaifinka biyayya shine kawai zaisa

nasarar ka ta ɗore"
Numfashi yaja cikin jin daɗin wannan nasara daya samu gurin mahaifiyarsa yayi mata gdy yanajin wani haske ji yake yama samu Habeebah ya gama, da wannan ya miƙe ya fice daga gdan ya nufi gdan babban yayansu da yake da yakinin idan ya samu Mai martaba da mgnr zai ɗauketa seriously ya ishe shi yana shirin fita gurin aiki suka gaisa tare da nufar office din tare suna tattaunawa akan abinda ya shafi fam ɗin nasu.
Bayan sun huta komai ya lafa ne Alh Ahmad ya dubi Habeeb yace “Kace kanada mgn dani Habeeb ina sauraronka" sosa kansa yayi sannan yayi masa bayanin komai Alh Ahmad ya ɗago yanayi masa kallon bashida hankali yace “Wannan shine tabbatar da har yanzu lissafinka ba daidai yake ba tunaninka ya goce nikam bazan iya shiga maganar nan mara yiwuwa ba mai martaba yaci mutuncina gara kai dama kaine ka siyawa kanka da kanka, Habeeb idan shawara kake nema nikam ina baka shawarar ka hƙr da wannan aure da kakeson yi kazo ka zaɓa a matan Fam ga ƴammata nan duk sun gama karatu wasu ma daga wasu ƙasashen suka dawo amma kai kasan ba'a fara ba kuma bazaa fara akanka ba Bamagujiya Habeeb haba wannan faɗuwar daraja tayi yawa da yawa to ka a musulmi Mai martaba baya aminta da ƴar talaka bare kuma ƴar maguzawa......"
Miƙewa yayi ya dauki wayoyinsa ya zuba a aljihunsa ya fice daga office ɗin da takaicin meye yasa ma zuciyarsa ta raya masa yazo gurinsa bayan ba mafita zai bashi ba? Tsaki yaja ya nufi inda yayi parking motarsa ya shiga yaja ya fice daga harabar ma'aikatar.

*Share please*
[4/11, 7:44 PM] AM OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

https://youtube.com/channel/UCZ5Vt2--iGyJfTwItSzAnGg

*Paid book*
Ki biya ta waɗannan hanyoyin acct details 0255526235 Fauziyya Tasiu gtbank ko ku turo katin waya MTN ta WhatsApp number na kamar haka 09013718241. Normal group 300, Special 700.

*Last Free Page 9-10*

★★★~~~★★★~~~★★★

Bai koma gda ba sai yamma koda ya fito daga ma'aikatar yayan nasa tasu ma'aikatar ya nufa amma abin arziki ya kasa hassalawa sai juyi da yake a kan kujera wayar Beebah yaketa kira taki tafiya duk damuwa tabi ta cunkushe masa zuciya sai bayan magrib ya nufi gdan babu wani karfi a jikinsa saina imani wanka yayi yana shirin fita Masallaci sallar Isha wayarsa tayi ruri ya ganin number Mai martaba yasashi haɗa nutsuwarsa ya daga Mai martaba yace “in ka dawo kazo inason ganinka" amsawa yayi tare da fita yaje yayi Sallah sannan ya nufi kiran na Mai martaba ya shiga da sallamarsa yana zaune saman shimfiɗun Kilishi da farin tabarau a idanunsa ya amsa sallamar Habeeb ya nemi guri ya zauna yace.
“Allah yaja kwana gamu mun amsa kira" ɗagowa yayi yayi masa murmushi ya miƙe ya saita zamansa yace “Am dama wani babban uzurine ya taso munason zamu haɗa gwiwa da wani campany dake Japan domin haɓakar masana'antunmu" jinjina kai Habeeb yayi yace “hakan yayi Allah ya taimakeka hakan zai kawo ci gaba ƙwarai" murmushi Mai martaba yayi yace “shiyasa nakeson ka Habibullah to dama ba komai bane yasa na kiraka campanyn sun buƙaci a tura mutum ɗaya daganan domin yaje yayi course na yanda ayyukan suke kasancewa kamar yanda suma zasu turo nasu wakilan don faɗaɗawa juna fasaha.
Na duba naga babu wanda ya dace da wannan tafiya saikai duba da kwazonka da basirar ka saboda haka kaje ka fara shiri nan da sati biyu zaka tafi in Allah ya yarda...."

Tunda Habeeb yaji ƙudurin Mai martaba gumi yake karyo masa yasan tabbas da manufa cikin wannan shiri, a sanyaye ya ɗago ya buɗe baki zaiyi mgn Mai martaba ya ɗaga masa hannu yace “banason kace komai kaje Allah yayi maka albarka shekara ɗaya ne babu yawa idan Allah ya amince kafin Ikcn zan sama maka matar data dace dakai na aura maka na turota tunda na fahimci yanzu hankalinka ya hadu kana buƙatar auren" a kasalce yace “Habeeban fah ranka ya daɗe...." Shiru mai martaba yayi masa shi kuma ya kasa tashi jikinsa har rawa yake saboda tashin hankali bai iya jurewa ba yace “Na rantse da Allah bazan iya zama da duk wacce zaka aura min ba Allah ya taimake ka indai bazaka amince nayi jahadin janyo Habeebah daga duhun kafirci zuwa hasken musulunci ba idan bazaka amince min na rayu da abinda raina da zuciyata suke muradi ba to ina roƙonka da kayi hkr ka barni na ƙarasa rayuwata ni kadai kamar yanda na shirya yinta a baya...."

Tsawa Mai martaba ya daka masa yana huci yace “Ni Habeeb Nine nake faɗa kake faɗa harma na zartar da hukunci kace baka amince ba lallai ya tabbata ka girma kakai shiyasa har kake jayayya dani akan kafira, to na rantse da Allah kaji dai kuma ka sani bana saurin rantsuwa akan lamarin rayuwa to nayi akan wannan yarinyar indai kaga ka aureta to kodai ka canza uba ko kuma bana numfasawa, tashi ka ficemin a daki kafin na nakasaka"
Tsuma jikin Habeeb yakeyi saboda ɗimuwa da gigita rantsuwar mahaifinsa tayi mugun girgiza shi Shikenan ta faru ta ƙare Mai martaba ya gama yanke hukunci yanzu babu bakin da zai iya fahimtar dashi ya gane...."

Sashin Hajiya Kilishi ya nufa da ƙannensa biyu mata da suke ciki ɗaya da sauran matan gdan duk suna babban falon suna kallo yazo ya shigesu ya nufi ɗakin mahaifiyarsa ya faɗa kan gadonta saboda mugun sanyin da yaji yana keta ƙashinsa yaja bargo ya rufa.
Kallon kallo sukayi Hajiya Zulai ta dubi Hajiya Kilishi da Hajiya Hauwa tace “Salma?" Dubansu Kilishi tayi tace “Naam Zulai" Hajiya Hauwa ce tace “Soja ƙalau kuwa?" Numfasawa tayi tace “da alamun ba ƙalau ba wato ɗebowa yayi da zafi aure yakeson zaiyi kuma ba musulma bace yarinyar da yakeson aure, nikam na fahimceshi kuma na bashi goyon baya to amma fah tunda mai martaba bai fahimta ba babu wanda ya isa ya fahimtar dashi"
Miƙewa Hajiya Zulai tayi ta nufi ɗakin tace “Babana komansa daban banda rigima irinta tarar aradu daka inashi ina kafira matsayin mata...." Tana faɗin haka ta bude dakin ta shiga yanda taji gadon na rawa yasata nufarsa da sauri ta yaye bargo tace “Innanillahi Ni Zulaihatu Babana meye hakan kuka kamar wani ƙaramin yaro...."
Tashi yayi zaune ya kama hannunta yace “Don Allah ku ceci rayuwata ku faɗawa mai martaba zanje Japan ɗin amma ya barni na auri Beebah Hajiyan soro bazan iya taɓuka masa komai ba indai ya rabani da Beebah nasan itama bazata iya rayuwa babu Ni ba"

Numfashi taja tace “Akan mace kakeson kashe kanka dubi fa yanda kake rawar sanyi Habeeb yanzu waye kake tunanin zai iya tunkarar mahaifinku yace zai fahimtar dashi?"
Hajiya Kilishi ce ta cafe da cewa “kaje inda ya umarce ka kayi masa biyayya insha Allahu zaka dace idan kace zakaja yaja kaine zaka faɗi ƙasa" zama sukayi sunata rarrashinsa shikam banda zafin jiki ma babu abinda suke ƙara masa kafin wane wannan zazzaɓi me zafin gaske ya lulluɓeshi Hajiya Kilishi ta shiga damuwa tabbas bada wasa Autan mazan nata ya ɗauki lamarin ba da gaske yakeyi don duk abinda yasa a ransa har yakai masa jinya to ya isa kallo.

Ranar sai ɗakin tabar masa bayan likita ya duba shi baccin wahala ya ɗauke shi zuciyarsa taƙi

samun sukuni
Washegari da asuba ya duba wayarsa ya zabura ya tashi zaune yana latsa wayar bugu biyu ta daga cikin muryarta me cike da gajiya da kasala tace “Tunda ka tafi nake kiran ka naji ko kun sauka Ify bana samu ɗan birni ina fatan Ify kake..." Wata gwauruwar ajiyar zuciya ya sauke yace “kamar bakida Ify meye yake damunki?" Kukan da ta kwana ta nayi shine ya dawo mata sabo tace “banasonsa wlh tsohone idan suka auramin shi kashe kaina zaiyi ɗan birni kai nakeso...." “Wa?" Ya faɗa da ƙarfi yana miƙewa daga gadon cikin kuka tace “Sarkin Mahauta...."

Miƙewa yayi daga gadon yace “Wa...waye yace zai bashi ke waye...." Kashe wayar tayi yayi bin duniya ta kasa ɗagawa aikuwa ba'a wayi gari dashi a gdan ba ya nufi tasha ya hau mota saboda bazai iya tuƙi ba shata ya ɗauka har garin Tsaunin gawo bai zame ko inaba sai gdan Dagaci a ƙofar gida ya tarar dashi sunashan hantsi ya mike da sauri ya tareshi suka gaggaisa yace “Ina Beebah?" Sunkuyar dakai Dagaci yayi cikin kunya yace “Tana ciki wani abu ta faɗa maka?" Iska ya furzar yace “waye wanda suka bawa ita?" Gabansa ne ya faɗi yace “Mai Tukuba ne nasan kasanshi a zaman da kayi a garin nan don ko zaman yini ɗaya kayi a garin nan indai ka shiga cikin mutanen garin nan zagaji sunan me tukuba ɗaiɗai yarinyar data zama bazawara a garin nan da bashine ya mayar da itaba a yanzu haka matansa na aure sha tara a gidansa Bibo itace ta Ashirin yau da yamma yace zai kawo komai na aure a ɗaura zai ɗauketa su tafi rani nayi iya yina na kasa yanada manya a karamar hukumar nan yanada bokaye sannan yanada kuɗi kaga dole na sakar masa iko...."

Numfasawa yayi ya dubi agogon hannunsa 12:12pm ya dago jajayen idanunsa yace “akwai masallaci a garin nan?" Girgiza kai Dagaci yayi yace “Saidai Hayin Fulani" ajiyar zuciya yayi yace muje ka rakani"
Babu musu suka nufi hanyar da zata kaisu Hayin Fulani suna zuwa suka tarar anyi shimfiɗu a ɗan ƙaramin masallacin juma'ar Liman ɗin dakansa ya fito ya taresu yana kallon Habeeb da mamakin abinda ya kawo shi musamman da yaji ance shine baƙon.
Karkacewa yayi masa bayanin komai da uzurinsa liman ya kalli na'ibi suka jinjina sukace “kaiko ɗannan miye naka da auren ɗiyarga ta Jimo kaje ka nemi wata mana ko a rugar nan ne baka mukayi"
Girgiza kai yayi yace “ita nakeso liman taimakon ta zanyi bayan soyayya akwai tausayi kanaganin wanda sukeso subawa aurenta yarinya ƙarama nawa Habeebah take wlh Kona aureta saina raineta kafin ta gama haɗa hankalinta sone yayi mana gaggawa, liman ka yankan sadaki na biya a ɗaura bisa tsarin addinin musulunci"

Ɗagowa Liman yayi yace “Duk da inajin tsoro bazanƙi ɗaurawa ba amma hanzari kace ita yarinyar ba musulma bace kaga kenan akwai jumurɗa abinda zaifi indai ta amince zata aureka to ta yarda ta musulunta auren zaifi sauki..."
Gumi ya share yace “zata musulunta daga baya nidai a ɗaura ɗin shine me wuyar" baƙin nacinsa yasa dole Dagaci ya karbi waliccin Bibo na'ibi ya karɓi na Habeeb aka ɗaura wannan rikitaccen aure akan sadaki saniya biyu kamar yanda al'adar Waliyyin angon take.
Wayyoh zo kuga murna gurin Habeeb har sujjada yayima ubangiji na cika masa burinsa da yayi, ya manta da duk wata kwantacciyar ƙura da ɗaura wannan aure zai tayar ya manta da rantsuwar mahaifinsa ya manta da alwashin da yaci akansa muddin ya auri Habeeba, ya manta da ƙudurin Mahaifanta da sukaci alwashin saisun kasheshi sun kashe Bibo muddin ya matsa akan aurenta......
Sai a Ikcn abubuwa suke ta dawo masa yayi zugum zuciyarsa ta kasu biyu wani sashi farin ciki wani sashi ɗinbin damuwa, Dagaci ne ya katse shirun da cewa “Mal Balaji tunda dai wannan aure ya ɗauru Habeebah matar Habibu ce to zaifi ya ɗauke matarsa subar garin nan don tabbas maganar zata fasu kuma indai har ta fasu batare da yabar ƙauyen nan namu ba to kuwa ko zai fita zai fita cikin rashin hayyac...."
“Kwarai kuwa munafiki zai fita cikin rashin hayyaci domin kuwa bazamu bawa abar dogaro kunya ba kamar yanda muka alƙawarta zamu kasheshi mu kasheta sayi auren a lahira na rantse indai nine Buba Sarkin Noma to yau saina raba wannan yaron da rayuwarsa bai isa ya auri jikanya ta ba macuci masu shanye jinin bil'adama......"

Wani sara ya kaiwa Habeeb daidai lokacin da Habiba ta kwace daga riƙon da yayi mata ta hankaɗe Habeeb suka zube can baya tare sai gashi a ƙasa ita kuma tana kwance a samanshi. Idanunta ta buɗe cikin idonsa ya sakar mata wani murmushi yasa hannunsa ya riƙe weast ɗinta ta kwantar da kanta luf a ƙirjinsa dagashi har ita wata nutsuwa ce take kwarara a ƙasan zukatansu....
Babu wanda yasan meye yake faruwa saida sukaji Liman yana cewa “Buba Aure ne mun riga mun ɗaurashi Habiba ta tabbata matarsa kada kuja da ikon Allah shine ya hukunta wannan aure kuma babu wanda yasan rabon dake tsakani wannan....
Dakata nace ka dakata Mal Liman kun hana mu taɓashi amma fah ka sani idan har kukaga yabar ƙauyen nan to warware auren nan kukayi...." Janyewa Habiba tayi a jikinsa zatayi magana Uda ya kai mata bugu Mal Liman ya janye ta ya turata gdansa ya dubi Habeeb yace shiga ciki akwai zauren baƙi ka jirani"

Zaku iya samun littafin nan ta website na arewabooks ku karanta cikin sauƙi ga waɗanda karatu keyi musu wuya a WhatsApp, ko kuma ku sauke app na arewabooks a wayoyin hannunku ga link ɗin domin shiga ta website ku biya ku karanta cikin aminci👇🏼

https://arewabooks.com

*Share please*
[4/13, 8:45 PM] AM OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

https://youtube.com/channel/UCZ5Vt2--iGyJfTwItSzAnGg

*Paid book*
Kunata cewa promo ɗin dana baku yayi kaɗan to gashi nan na ƙara daganan zuwa jibi zaku sameshi a 200 PC 500
Ki biya ta waɗannan hanyoyin acct details 0255526235 Fauziyya Tasiu gtbank ko ku turo katin waya MTN ta WhatsApp number na kamar haka 09013718241 ƴan Niger kuma zaku tuntuɓi wannan number don biyan kuɗinku +227 95 04 58 22.

*Free Page 11-12*

★★★~~~★★★~~~★★★

Ankai ruwa rana kafin su fita daga Hayin Fulanin Saida aka shigar da jami'an tsaro sannan suka samu suka fita da Habeeb daga garin da sharraɗin Habeebah zata zauna a gdan Liman zuwa wasu kwanaki kafin mijinta ya dawo ya ɗauketa.
Inda su Jimo sukaci alwashin muddin suna raye wannan aure bazashi ko inaba shidai Habeeb bai bawa mgnrsu muhimmanci ba yaja ƙafafunsa suka bar ƙauyen cike da kewa shauƙi da ƙaunar matarsa.
Itako Habeebah Ikcn da taji hukuncin da aka yanke da kuma furucin da mahaifinta yayi akan

aurenta sai duka jikinta yayi sanyi bataso aurenta ya kasance a haka ba bataso ace ta samu matsala da iyayenta ta dalilin aurenta ba Shikenan sun sallamata babu su babu ita saboda Habeeb?"
Hawaye ne ya sulalo mata ta zauna a shimfiɗar da Hajjo matar Liman tayi mata ta zuba uban tagumi hawaye wani nabin wani zuciyarta tayi ƙunci duniyarta tayi duhu.
Tunda ta taso takejin iyaye mata suna cewa duk matar data ɗauki namiji uba saita mutu marainiya! Yanzu ita meye ribar da zata samu data amince tayi baram baram da iyayenta akansa? Waye shi??Meye yake ma nufi da aurenta??? Meye yasa ya tsallake matan dake birni yace sai ita?.

Tambayoyi barkatai marasa amsa tunanin Jumme ya faɗo mata ta kuwa rushe da kuka me gigita tunani da taɓa zuciya yanzu Shikenan bazata sake ganin Jumme ba? Ta rabu da mahaifiyarta me ƙaunarta da ƙaunar farin cikinta har abada?
Kuka takeyi sosai me taɓa zuciya, a haka Hajjo ta ishe ta ta tafa hannu tana salati tace "Haba yarinya Meye kuma abin kukan ai gdy ya kamata kiyiwa Allah daya baki mijinki me sonki da tausayinki gashi Allah ya ɗaga darajar ki zaki tafi birni"
Ɗagowa tayi ta dubi Hajjo fuskarta taf da hawaye tace "Waye Allah?" Da sauri Hajjo ta kalleta da mamaki tace "Allan ne baki sani ba ƴar nan tab to wannan wanne irin aure ne shi mijinki naga ai musulmi ne...."
Har yanzu idanunta nakan Hajjo ta kuma cewa "shima kina nufin yasan Allah?" Jinjina mata kai tayi tace "tabbas yasan Allah domin kuwa alama ta nuna bayan sanin Allah har tsoron azabarsa yanaji Habeebah kinason sanin Allah?" Saurin ɗaga mata kai tayi tayi murmushinta ta dafa kanta tace "Zakisan Allah harma ki bauta masa yanzu Meye abin da kike bautawa?" Sunkuyar da kanta tayi tace "Uwa me tsarki ita nake bautawa kuma ita ce abar dogaro na itace take bani nasara akan komai nawa sannan yanzu itace tayi fushi dani harma tasa iyayena sukayi fushi dani yanzu Shikenan rayuwata bazatayi albarka ba....."

Murmushin tausayinta Hajjo tayi ta mike ta zari buta tace "bari naje nayi sallar magaruba sai mu zauna" nan ta zauna tana kallon yanda Hajjo take sallarta kamar yanda ta taba ganin ɗan birni yanayi, bayan Hajjo ta idar ta sako musu tuwo da man shanu suna ci Hajjo na bata labaru masu ban dariya sai gashi ta saki jiki tana ta dariyarta da haka Liman ya shigo ya taddasu yaji daɗin yanda ya samu Habeebah tanata dariyarta abin ya matukar faranta masa rai ya mika mata wayar hannunsa yace.
"Mijinki ne yakeson mgn dake" ƙasa tayi da kanta cike da kunya Hajjo ta karɓi wayar tace "kekam da a cikinmu akayiki bansan irin halin da zakiyi ba kawai daga mijinki na kira sai kiyi ƙasa dakai to ko yaranmu ai sun daina wannan kunyar"
Tana mgnr tana kara mata wayar a kunnenta tayi shiru tana jinsa yanata mgn taki cewa komai

har ya kashe ya sake kira Hajjo ta tashi ta nufi garken shanu hakan ya bata damar cewa "Ɗan birni...." Ajiyar zuciya yayi yace "har yaushe zaki daina cemin ɗan birni kike kirana da sunana Beebah?" Ajiyar zuciya tayi tace "kaje gdane?" Gyara kwanciya yayi yace "ina kwance a gadona inajin dama kina kusa dani da kin ragemin kewa ko tausa kyayi min...."

Wani gwauron numfashi ta sauke daya sanyashi tambayarta "Meye" a kunyace tace "Kunya kabani ai babu kyau sashi ya rinƙa taɓa sashi" dariya sosai mgnrta ta sanyashi yace "Har yanzu?" Ɗaga kai tayi tace "Eh" murmushi yayi yace "idan nazo ɗaukanki nan da sati biyu zaki maimaita min am kinsan me?"
Girgiza masa kai tayi tace "Aa" yaja fasali yace "Hajiyata tana gaisheki na sanar da ita komai daya faru ta sanyawa aurenmu albarka sosai tayi mana fatan alkhairi" dariya tayi tace "Hajiyanka mahaifiyarka kenan?" Jinjina kai yayi yace "Eh tayi murna da samuwarki cikin alhinta Habeebah mahaifina Sarki ne a garinmu Sarki Khalil na ƙasar Dutse shine ya haifeni mahaifiyata kuwa Hajiya Kilishi wato Ummusalma haifaffiyar Masarautar Daura ce mu bakwai mahaifiyarmu ta haifa maza biyar mata biyu nine ƙarami a maza a dakinmu sai mata biyu da suke ƙanne a gurina matan mahaifina uku Hajiya Zulai wato Hajiyan soro tanada ya'ya Hudu uku mata ɗaya namiji Nasir kenan sa'anni muke dashi sai Hajiya Hauwa Hajiyan ƙofa yaranta biyu dukka maza Fahat da Salim gidanmu bamuda matsalar ƴan ubanci duk da dai ba'a rasa shi ko yaya ne tunda ya shiga gidan Annabi ma bare mu bayin Allah, abu ɗaya ne matsalar family ɗina munada ƙabilanci duk wata mace da yayyuna suka aura to ta fito ne daga tsatsonmu haka matan ma ba'a kaisu ga waje a cikin dangi akan auraddasu kasancewar mahaifinmu da ƴan uwansa sunada yawa sannan suna ƙyamar talauci wannan yasa musu gudun bare saboda sunce daga bare za'a samu musu musakai a gwamutsa musu zuri'a da datti"
Numfashi yaja ya sauke yaci gaba da cewa "Habeebah nasan zaki fuskanci ƙalubale zama da zuri'armu domin kece kika fara shigowa wannan zuri'a tamu matsayin mata kuma kika zo a wani yanayi da mai ƙaramar ƙwaƙwalwa bazai mawa rayuwa uzuri ba"

Numfashi ta sauke hawaye ya zubo mata tabbas wannan shine an gudu ba'a tsira ba anyi gudun wuya an haikewa wuya har ta fara kukan tausayin kanta na kasancewa matar Habeeb tun yanzu wannan wanne irin dangi ne da basa ƙaunar bare?
Muryarsa ce ta katseta da cewa "kiyi hƙr da yanayin da zamu ɗan samu kanmu nasan zamu fita babu wani yanayi da yake dawwama Beebah da wasa nake Miki bazan iya barinki kiyi dogon Zama a garin nan ba zuciyata bazata nutsu ba gobe xansa Azo a tafi dake" zaro ido tayi tace "gobe?" Murmushi yayi yace "ko baki shirya ba?" Sunkuyar dakai tayi tace "Amm...." "Shetttt" yace mata sannan yace "amma me? Banson jayayya karki fara kinji?" "to" ta amsa da ita sannan yaci gaba da janta da hira tana ƴar dariyarta har zuwa wani lokaci sukayi sallama Hajjo ta nuna mata makwanci ta kwanta bacci ya ɗauke ta cike da mafarkan Ɗan birni.

Washegari da wuri batama tashi daga kwanciyar safe ba Liman yazo yace  tazo tanada baƙi taja ajiyar zuciya ta miƙe ta ɗauki hijjab ɗin da Hajjo ta bata jiya tasa ta fito tun daga nesa ya kafeta da manyan idanunsa tayi masa kyau da shigar Muslim women  sai yaji ta ƙara shiga ransa ta ƙarasa gabansa kanta a ƙasa ta tsugunna tace “barka da hanya" numfasawa yayi ya sanya hannu ya ɗagota ya sanya hannu ya lakaci hancinta yace “Sannu matar Prince Habeeb kina Ify?" Sake sunne kanta tayi tana ajiyar zuciya yajata ya shigar da ita motar yaja suka bar gurin a guje.

Yanda ta ɗago da alamun firgici yasashi kallonta yayi mata murmushi yace “zaki koma rayuwa a inda aka halicce ki don gurin" nandanan jikinta yayi sanyi ta mayar da idanunta ta lumshe tare da kwantar da kanta a kujerar wani zazzafan hawaye ya zubo mata yabita da kallo hakanan yaji ta bashi tausayi.
Sun jima suna tafiya tana rera kukanta batare daya ce mata ƙala ba bawai don kukan baya damunsa ba sai don bashi da kalmar dazai iya rarrashinta da ita, dole tayi kuka rabuwa da dangi ƙawaye da garinka rabuwa ta har abada batare daka shirya ba dole ne ya taɓa zuciya da gangar jiki.
Bai nufi gdansu da ita ba wani Unguwa ya nufa yayi parking ya fito ya buɗe get na gdan ya shiga da motarsa yayi parking sannan ya kamo hannunta yaja fasali yace.
“Kiyi hƙr Beebah nasan kinajin ciwon rabuwa da makusantanki ne wlh ban rabaki da danginki don cutarwa ko zalumci a gareki ba sai don hakan shine yayi daidai da tsarin rayuwarki,
Dukkan wata mace a duniya a ƙarƙashin haka take ko yanzu ko gobe ko jibi sai kinbar gdanku kin tafi gidan aure so ki kwantar da hankalinki insha Allahu nayi alƙawarin baki kulawa saikin zama abar alfahari ga danginki baki ɗaya"

Hannunsa yasa ya share mata hawayen yace “kukan ya isa haka muje na baki ruwa kiyi wanka ki canza kaya ki bani Ibrn kuruciyarki"
Fitar da ita yayi a motar suka nufi ƙofa ya buɗe suka shiga ta tsaya tana ƙarewa falon kallo sake da baki da kuma bayyanannan tsoro ta dubeshi yayi murmushi ya sake riƙe hannunta yakai bakinsa ya sumbata ya ɗago idanunsa da suke lumshewa kamar me jin bacci ya zubasu akan fuskarta yana ayyana abubuwa da yawa a ransa saidai shi kansa baya ƙarfafawa zuciyarsa gwiwa wajen aiwatar da abinda take muradi.
Zubewa yayi a kujera kallon Beebah na saukar masa da wata kasala me narka lakar jiki ya miƙa mata hannu da nufin tazo gareshi ta noƙe cike da tsoro yayi wata miƙa ya miƙe yace “ok muje bamuda lkc" batayi masa musu ba suka nufi wata ƙofa ta buɗe ɗakine harda gado kato na alfarma ta kuwa lalace a kallon gadon bataji sanda ya zare mata hijjab dinta ba saijin hannunsa tayi a ƙirjinta ya sanyata cikin jikinsa ya rungumeta da wani salo me narkar da cikakkiyar mace, itakam Beebah yanda taji yana sama da hannunsa saman ƙirjinta yasa ƙirjin nata dukan uku²

tayi saurin juya masa baya ya kasance ƙirjin nata ya koma ƙirjinsa hakan ma daɗi yayi masa yasa hannu ya tallafi mazaunanta.
Nan take jikinta ya ƙara ɗaukar rawa ta janye da sauri zatayi mgn yasa hannunsa kan bakinta ya lumshe idanunsa da suka kada sukayi jawur yace “Mijinki ne ni Beebah akwai bambanci da irin mazan da kike tsoro muje na nuna Miki yanda zakiyi wanka bamuda lkc na faɗawa Hajiya na daukoki idan munje don Allah kada ki bani kunya duk abinda kikaji na faɗa a matan gda da Mai martaba ki gasƙata hakan kinji?"

Ɗagansa kai tayi ya jata suka shiga bathroom ɗin dake batada duhun kai batasha wahalar gane komai ba ya fita ya barta tayi wankanta dama jiya da dare Hajjo ta tsefe mata gashinta tasa klin ta wankeshi tas gashinta yanada muguwar cika ga tsayi ta sharceshi da matajin data gani a gurin ta sake shi ta fito sanye da hijjab ɗinta yana kwance a gado ya rungume hannunsa a ƙirjinsa ya lula sama jannati yaji ta shafa fuskarsa ya sauke ajiyar zuciya me ƙarfi ya sauke idanunsa akanta tayi masa murmushi tace “Tunanin me kakeyi?" Tashi yayi zaune ya kuranta ido har Saida ta tsargu sannan ya janyo ta ta zauna kusa dashi karon farko data fara zama a abu me laushi dangin katifa ya tallafi fuskarta yace “A matsayin ƴar aiki zan kaiki gdanmu...." Wani kallo tayi masa na sosai tace “Ƴar aiki baiwa fah kenan?" Numfashi ya sauke yace “Hakane zaki tsaya iya bangaren mahaifiyata Hajiyata tasan matsayinki a gurina Habeebah bawai don kaskanci ba a'a saidon kareki daga duk wani abu da ka iya faɗowa bayan bananan zan kaiki matsayin ƴar aikina karki damu shekara ɗaya kawai zanyi na dawo kasar nan gabaɗaya nayi ƙoƙarin tafiya dake na hasaso asirina zai tonu domin babu wanda yasan da aurena dake sai Hajiyata nabarki gurinta amana kuma zanyiwa Khalisa da Hudah kashedi akanki bazaki samu matsala da kowa ba kiyi hƙr kinji....."

*share please*
[4/16, 7:49 PM] AM OUM HAIRAN: *BAMAGUJIYA*
*(HOT LOVE AND DESTINY)*

NA

*FAUZIYYA TASIU UMAR*
*OUM HAIRAN*

https://youtube.com/channel/UCZ5Vt2--iGyJfTwItSzAnGg

*Paid book*
Kunata cewa promo ɗin dana baku yayi kaɗan to gashi nan na ƙara daganan zuwa jibi zaku sameshi a 200 PC 500
Ki biya ta waɗannan hanyoyin acct details 0255526235 Fauziyya Tasiu gtbank ko ku turo katin waya MTN ta WhatsApp number na kamar haka 09013718241 ƴan Niger kuma zaku tuntuɓi wannan number don biyan kuɗinku +227 95 04 58 22.

*Free Page 13-14*

★★★~~~★★★~~~★★

Zubansa idanu tayi zuciyarta na hantsilowa a rayuwarta bata juri ƙasƙanci ba duk da kasancewarsu ba wasu shahararrun masu dukiya ba amma girma ake bawa gdansu a ƙauyensu yau wai ita ce zaakai wani gida da sunan ƴar aiki.....
Hannunsa taji yasa ya ɗauke mata hawayen da ya sulalo daga kwarmin idanunta ya girgiza mata kai ta dauki rigarta daya ɗauko mata doguwa ta zura tana cewa "Bazanyi maka musu ba ba kuma zan baka kunya ba" tana mgnr muryarta na rawa alama da take nuna kukan takeson haɗiyewa zubanta idanu yayi cikin mutuwar jiki yace "Hakan baiyi Miki ba ko Beebah?" Girgiza masa kai tayi tace "yayi" daga haka ta nufi ƙofa zata fita ya riƙota ya haɗata da jikinsa.
Hannunsa yasa ya zuge zip na rigar ya saukar da ita ƙasa tayi saurin haɗe hannunta a ƙirjinta ya kawar dakai ya buɗe cikin wata jaka da suka shigo da ita ya zaro bra ya sake janyota bataso yake taɓata tsoro takeji saidai bata isa hanashi ba tanajinsa ya saƙala mata wani abu a ƙirjinta ya mayar mata da rigarta ya  kama hannunta suka fice yasata a mota shima ya shiga suka fice itadai ƙirjinta sai dukan tara² yakeyi taga sun ɗauke hanya sunbi wata hanya da take da yawaitar mutane da alama cikin gari suka shigo Beebah banda rarraba idanu babu abinda takeyi haka suka isa ƙofar gdan sarautar ya rinƙa buga horn ana bashi hanya ana ɗaga masa hannu wani ya ɗaga wani kuma ya share har suka isa harabar inda motoci suke.

Parking yayi ya fito ya buɗe mata itama ta fito tanabin gidan da kallo dukkan wasu shika-shikai na tsoro sun gama bayyana a tattare da ita ji takeyi kamar ta runtuma da gudu wannan duniya wacce iri ce ya ɗaukota ya kawota ciki,
Bata lura da inda suke takawa ba da kuma yawan mutanen da suke kallonsu har suka isa harabar gidan inda bangarorin matan gidan yake ya saki hannunta yace "biyoni" batare da ya tsaya ba haka ta rinƙa binsa kamar raƙumi da akala a daidai wani corridor sukaci karo da wasu

kyawawan ƴan mata biyu da bazasu wucce tararrakin Beebah ba suka rusuna cikin ladabi sukace “Barka da dawowa Bro" dagansu hannu yayi suka miƙe tare da bin bayansu da kallo itama Habeebah su take kallo har tana tuntuɓe suka shiga sashin Hajiya Kilishi bata falo alamar da take nuna masa kodai tana sashin mai martaba ko kuma tana ɗakinta.
Wata Cikin hadiman sashin ya duba yace “Ina Kilishi?" Cikin ladabi tayi ƙasa tace “Allah ya taimakeka tana ɗakin hutawa tayi izinin kada abar kowa ya shiga saboda tana buƙatar kaɗaici"

Bai tsaya ba saima nufar matakalar benen da yayi ya haura saman yana cewa da Beebah ta biyosa Ita dai data kalli tsayin gurin taga yanda yake takawa sai taji bazata iya hawa ba kawai sai ta samu guri ta zauna a step na farko na benen tana kallon yanda hadiman suketa kai kawo a falon.
Sun ɗan jima sannan taji Muryar dattijuwa tana fitowa tana cewa “kuma shine kabarta a ƙasa don sakarcinka" kallo ɗaya tayiwa kyakkyawar dattijuwar tayi ƙasa da kanta cikin ladabi da kunya ta durƙushe a ƙasa tace “Ina yini" murmushi Kilishi tayi ta rusuna ta kama hannunta tace “Habeebah sannu da zuwa muje ciki kinji" tana mgnr tanajan hannunta zuwa saman ta rinƙa takawa a tsorace yana kallonta wani ɗaki Hajiya Kilishi ta buɗe suka shiga mamaki ya cika Habeebah ganin irin ƙawar da aka kashewa ɗakin gadone six by seven sai wardrobe nasu dake maƙale a jikin bango madubin ma ya cinye rabin bango sai wata ƙofa a gefe da take a rufe ga freezer nan madaidaiciya sannan gefe ga Despenser nan itama an dora Mata gorar ruwa akai.

Zaunar da ita Hajiya Kilishi tayi a gefen gadon ta zauna a gefenta ta kamo hannunta tace “Duk da shigowar ki family ɗin mu tazo da yanayin da banson ki shigo a haka ba Habeebatullah inayi Miki murnar zama mata gurin Autan maza ina fatan kamar jajircewarsa wajen ganin ya mallakeki kada ta zame masa kaico a gaba kiyi rayuwa cikin aminci da sirri.
Habeebah Nice surukarki ma'ana mahaifiyar mijinki na karɓeki a matsayin suruka amma da sharraɗin wasu dalilai zasu sanya ki zauna a ɓoye zaki rayu anan batare da kowa yasan wace ke ba zamu faɗawa duniya keɗin ƴar aiki ce da muka ɗaukoki domin wasu aikace-aikace nawa Ni kaina bazan jingina ki da mijinki ba domin kusancinku idan yayi yawa zaisa kokwanto a zukata saboda haka ki zauna da nutsuwa watarana komai zai wucce"
Tunda Kilishi ta fara mgnr idanun Beebah ke zubar da hawaye data rasa na Meye ne, Hajiya Kilishi irin matan nan ne da basa ƙaunar ganin wani na ƙasansu cikin damuwa hakan yasata dafa kanta tace “ko hukuncin dana yanke dan gujewa faɗawarki cikin takura da tsangwamar gdannan baiyi Miki bane Habeebah?"
Saurin girgiza kai tayi tace “badon shi bane inayin kuka ne saboda rashin sanin halin da Jumme take ciki...." Kilishi kallon Habeeb tayi ya shafa kansa ya juya ya fice daga ɗakin tasan halinsa da miskilanci amsar bawa matar tasa ya rasa shine yasashi ficewa haka ta kirkiro murmushi tace “inaji a raina kowa yana cikin amincin Allah Haby ki saki jikinki a gdannan kada ki tsangwami kanki hakan zai sama maki kusanci da jama'ar cikinsa wanda kusancinki dasu shine

matakin nasarar aikin dake gabanmu"

Nuna mata komai ta rinƙayi tace “Wannan ɗakin wata hadima ta ce Sakina da Allah yayiwa rasuwa zakigansa kusa da ɗakina itan amintacciya ce gareni tana kula da dukkan lamuran da suka jiɓanceni shiyasa ban yarda tayi nesa dani, can kuma ɗakunan ƙannenki ne Huda da Khalisa yanzu suka fita sunje makaranta" jinjina kai tayi Hajiya Kilishi ta juya tace “zanje ƙasa zan Turo a kawo Miki abinci kici sosai kafin zuwa anjima na gabatar dake a gurin mutanen gidan"
Fitar Kilishi ya bata damar ƙarewa ɗakin kallo tana ayyana abubuwa da yawa a ranta bayan mamaki itakam harda tsoro ace wannan ɗakin a ciki zata rinƙa kwana ita kaɗai tasaba gdansu ita da Jumme da Jimo suke kwana ɗaki daya tunda Tani ta mutu.
Da wannan tunanin taji an buɗe ƙofar ta dago kanta wata mata ce tazo ta ajiye mata kayan abinci ta zuba mata shinkafa ce da miya miyar taji kifi banda sai farfesun naman zabo a gefe sai lemo kala² sai sinasir da yaji miya duk ta zuba mata itadai batace komai ba har ta gama ta ɗago tace “Yarima Habeebu yace na tabbatar kinci abinci sannan ya damƙa amanarki a hannuna duk abinda ya dace zanke nuna Miki"

Gdy tayi cikin ladabi Larai ta miƙa mata abincin da takurawarta taci shinkafar sosai tana yabawa da daɗinta tunda take bata taɓa cin abinci mai daɗin wannan ba haka ta yagi naman zabin ta ture Larai na kallonta tana mamakin zubin sirrin ɓoyayyen jyawun yarinyar zallar ƙuruciyar ta bayyana akan fuska da jikinta babban abinda yafi ɗaukar hankalin Larai wata suma lufluf kwance a jikinta me ban sha'awa, hakanan Larai taji yarinyar ta shiga ranta fiye da yanda tayi tunani.
Haɗe kayan Larai tayi ta fara ɗebewa Habeeba babu ƙyuya itama ta fara diban kayan suna fita dashi sai gashi cikin yinin sun samu wata shaƙuwa da Beebah da Larai kamar dama sunsan juna hakan yayima Kilishi daɗi sosai duk da ta lura Beebah irin yaran nan ne masu kunya taƙi sakin jiki da ita sannan bata bari ko idanu su haɗa ko magana takeyi da taganta zatayi shiru ta fara ƙasa dakai.
Sai dare Khalisa da Hudah suka dawo suka ishe Beebah dake sunada son mutane kuma Kilishi ta faɗa musu zatayi baƙuwa batason raini batason kyara ko tsangwama tsakaninsu itama matsayine da ita a gurinta kamar su shine yasasu janta a jika tsakanin yammar da daren sai gashi sunyi wata shaƙuwa ta ban mamaki da ƙannen mijin nata.

Sune suka rinƙa janta lungu da sako na gidan suna zagawa da ita sune har gaban Mai martaba suka kaita matsayin baƙuwa da tazo daga Daura dangin Kilishi kenan aikuwa ya jima yana

kallon yarinyar nutsuwarta ta burge shi da kuma yanda ta saki jiki da komai na gidan.
Abu ɗaya ne ya basu mamaki idan suka tashi zasuyi sallah saidai suga tanata kallonsu har suyi su gama su dawo suci gaba da harkokinsu sai gashi da akazo kwanciya rigima ta sarke Kilishi tace taje ɗakinta ta kwanta su kuma sunce saidai su kwana ɗaki daya da ita, kan dole Kilishi ta barsu saboda ta lura itama tafi son shiga cikinsu.
Kwanciyar ma Saida akayi rigima wannan tana cewa a gadonta zata kwana wannan tana a gadonta zata kwana itadai kallonsu kawai takeyi ƙarshe ma tayi shimfida a ƙasa tace ita tafijin daɗin kwanciya a ƙasa.
Kwanciyarta tayi a ƙasa Saida Kilishi ta lekosu taganta a ƙasa ta kuwa rufesu da faɗa dole ta koma gadon Hudah ta kwanta baccinta na yau dabanne dana koyaushe daɗinsa ma dabanne donma sanyin A C ya hanata sakat saijan bargo takeyi tana kudunduna.

Haka sukaci gaba da rayuwa sati guda ta wucce sukaga bata sallah saidai tayita kallonsu hakan yasasu tambayarta Meye yasa bata sallah ta dubesu tace bata san ya akeyi ba  sun cika da mamaki nan Khalisa taje ta fadawa Kilishi Kilishi tasa aka kirata da hikima da komai suka rinƙa cusa mata son addinin Musulunci cikin satin biyun kafin yabar ƙasar Saida ta karbi kalmar shahada yayi murna sosai duk da ba shiga harkar su yakeyi ba ko Itan baya sauraro saboda gudun tonuwar asirinsa hakanan yake daurewa saidai kawai duk inda yagansu zaune yakan yawaita zagaya gurin wani lkcn har idanu suke haɗawa ya kawar dakai itama sai ta koyi shareshi duk da a farko abin yayi mata bambarakwai amma dataji yanda ƴan uwansa suke tsoronsa kuma suke fadin miskilancinsa sai tasawa zuciyarta dangana ta mayar da hankalinta wajen ɗaukar darasinta gurin Kilishi data ware mata makaranta islamiyya take koyar da ita duk wani abu daya kamata ta sani a matsayinta Na baliga.

Ana gobe zai tafi da dare wajen takwas da rabi dukkan yaran gidan suna babban falon suna kallo ita kam ba ma'abociyar kallo bace tana kwance a dakinsu dake tayi kaura daga nata ɗakin bata kwana a ciki saidai yini ko daukar kaya ke kaita Larai ta shigo tace “Beebah kije inji Yarima yana ɗakinki" wani ras taji gabanta ya faɗi saboda cikin kwana biyun hakanan taji itama tana tsoronsa kamar yanda ƙannensa da sauran hadiman gidan suke tsoronsa.
Juyawa Larai tayi zata fice Beebah ta miƙe tabi bayanta ta jima tsaye bakin ƙofar ɗakin kafin tayi ƙarfin halin buɗewa yana tsaye a tsakiyar ɗakin goye da hannunsa a bayansa ta tsaya jikin ƙofar ya juyo ya zubanta idanu tayi ƙasa da kanta ya tako ya tsaya a gabanta tayi ƙasa zata durƙushe ya riƙota tayi baya kamar zata fadi yasa hannunsa ɗaya ya tallafi bayanta ya dago fuskarta ya zuba idanunsa a kanta tayi saurin lumshe nata yaja numfashi ya haɗata da jikinsa yana sauke ajiyar zuciya ya ɗora lips nasa a wuyanta ya sauke mata kisa me kashe jiki hakan yasata jan fasali itama tana ƙoƙarin janyawa yajata zuwa gefen gadon ya zaunar da ita yana saita nutsuwarsa ya sauke numfashi me ƙarfi yace “Habeebah!"

Yanda ya kirata da karsashi yasata saurin buɗe idanunta suka shiga cikin nasa yayi mata murmushi tare da lakace mata kumatu yace “ke yarinya ce ƙarama me ƙarancin lissafi wato dana kawoki nan Ni na gama amfani a gurinki kin manta da wayeni a gurinki kawai harkar gabanki kikeyi babu ruwan ki da mijinki ko?"

Sunkuyar da kanta tayi tace “To ba kaina ba sai ka rinƙa hahhaɗemin fuska nikuma tsoronka nakeji" zubanta idanu yayi yanda take sarrafa harshenta wajen furucin ya bashi nishadi yaja numfashi yace “Ok yanzu na sake Miki me zaki bani gobe zan tafi...."
Da sauri ta ɗago tace “Gobe?" Jinjina mata kai yayi yace “Banason tafiyar nan kawai babu yanda zanyi ne ta kamani dole Beebah kinsan dai matsayin da kike kai yanzu, ke ba daidai kike dasu Hudah da Khalisa  ba bare Amna da Khaulat ke matar aure ce kada rashin ganina yasa kiyimin wasa da igiyar aurena dake hannunki Beebah amanar kanki na hannunki shekara ɗaya tanada tsayi amma kamar yau ne insha Allahu zan dawo ina fatan kafin dawowata komai ya daidaita mu fara rayuwar ƴanci kamar kowanne ma'aurata"
Jikinta ya mutu ta kasa cewa masa komai Saida tajita kwance flat a gadon yayi mata rumfa gabanta yabada wata irin muguwar faɗuwa data sanyata rintse idonta da ƙarfi zuciyarta nabada wani sauti dam² musamman lkcn da taji dumin lips ɗinsa a saman  bakinta, wannan yanayi ya sanyata tsumar jiki data zuci wacce ta sabbaba mata neman sume masa lkcn da ya ɗora hannunsa a ƙirjinta ya zurasu cikin rigarta ya zuge zip ɗin ya fito da dukiyar fulaninta ya damƙe a hannunsa.
Azabar da taji da kuma firgicin data shiga yasata sakin ƙarar da yayi saurin toshe mata baki da hannunsa ya sanya lips ɗinsa ya kama nipples ɗinta da bakinsa....
Tuni firgicinta ya sake bayyana ta shiɗe masa tare da ƙanƙameshi numfashinta na shirin ɗauke wa hakan ya sanyashi saurin sake mata boobs ɗinta ya miƙe a kasalce ya zubanta idanunsa da suka kaɗa sukayi jawur, ga mamakinsa sai yaga ashe bama ta numfashi wani yawu ya haɗiye yana ƙoƙarin saita nutsuwarsa ya buɗe freezer ya dauko ruwa me sanye ya ɓalle murfin bottle ɗin ya tsiyaya a hannunsa ya shafa mata a fuskarta, babu jimawa taja ajiyar zuciya ta fara shure² tana kai masa duka yayi saurin riƙe hannunta yace “Ya isa matsoraciyar matata na hƙr akwai lkc".........

*Sanarwa*
Daga wannan paging na gama free indai kin ganshi a waje to na haramun ne sannan promo ɗina ya ƙare daga yau on 15 12:00am indai yakai gobe to saidai ki/ka biya 300 ɗinka PC Kuma 700.

*share please*

[4/17, 10:22 AM] AM OUM HAIRAN: BMGJY

KIYIWA GIRMAN ALLAH KI BIYANI HAƘƘINA KAFIN KI KARANTA NORMAL 300 PC 600, KI BIYA TA WANNAN HANYOYIN ACCT DETAILS 0255526235 FAUZIYYA TASIU GTBANK KO KATIN WAYA MTN TA WHATSAPP NUMBER NA 09013718242 ƳAN NIGER ZAKU TURA KATIN AIRTEL 400CF TA WANNAN NUMBER +227 95 04 58 22 SAIKU TUROMIN SCREENSHOT NA SHAIDAR KUN TURA MATA NIKUMA NASAKU A GROUP.

*15-16*

★★★~~~★★★~~~★★★

Yana faɗin haka ya saki hannunta ya miƙe yana cewa “ki kula da kanki" ajiyar zuciya ta sauke tabisa da kallo hakanan zuciyarta tayi mata babu daɗi ta tsinci kanta da kewarsa da tunanin makomarta idan bayanan da wannan ta koma ta kwanta a gadon zuciyarta nayi mata babu daɗi hawaye na bin gefen idanunta tana sharewa taji an buɗe ƙofar an shigo bata ɗago ba Khalisa ta zauna a gefenta tace “Beebah faɗa wannan masifaffen yayi Miki ko?" Numfashi ta sauke ta tashi zaune tana gyara rigarta tace “Wa kenan?" Tana binta da kallo tace “Bro mana naga ya fita a dakin nan yanzun kuma nasan idan ba masifarsa ce ta ciyoshi ba baya shiga ɗakin mu bare kuma naki" ƙasa tayi da kanta tace “to Meye laifi Inma faɗan yayimin ai ya isane bakiji abinda manya suke cewa ba “yaro yi kuka in ka rasa me maka faɗa” saboda haka Ni daɗi ma naji da yasan da zamana har yaji a ransa na cancanci yayimin tsawa akan rayuwata"
Jinjina kai Khalisa tayi tace “hakane Allah yasa mu dace amma nikam haushi nakeji idan anamin faɗa saboda wani abin ma bai kai laifi ba yanzu ranar nan da akasa babban Yaya ya zane Amna da Khaulat laifin baifa kai ba wai kawai don sunyi video sun ɗora a TikTok shine akayi kamar za'a kashesu wlh yaran Saida suka bani tausayi"
Sauya akalar mgnr tayi da cewa “yaushe zaki fara yimin lesson na turancin" don batamasan Meye TikTok ɗin ba.

Murmushi Khaly tayi tace “toni yanzu Beebah ta ina zan fara a koya Miki turanci Ni abinda naga yafi kuma zan shawarci Kilishi a nema Miki makaranta ki shiga sai a rinƙa yi Miki lesson a gda tunda da alama ƙwanyarki tana ja zaki gane komai a hankali" kallonta tayi tace “Khaly nayi fah karatu a ƙauyenmu nida Yaya Tani ne kawai mukayi makarantar primary da secondary aji uku daga wasu ƙauyukan ma idan aka rubuto sako aka aiko kiranmu akeyi mu karanta mutuwar yaya Tani ne tasa aka dakatar da karatuna" daɗi ne ya cika Khaly tace “kay alhmdllh amma naji

daɗi yanzu muje gurin Kilishi ai ba wani girma kikayi ba kawai a sama Miki Form ki juya senior secondary inyaso ma a saki a tamu tunda muma bamu gama ba sauranmu 1 years tashi muje hakama za'ayi"
Hakan kuwa akayi suna zuwa suka sanarwa Kilishi tayi murna da hakan tace “Zan kira Mas'ud zaiyi mata Screening indai takai za asan yanda za'ayi" Beebah tayi gdy sukaje suka kwanta sunata murna tama manta da lissafin tafiyar Habeeb.

Washegari kuma da safe Hajiya Kilishi tasa aka ɗebe su a mota aka kaisu gyaran gashi wannan tasa basuyi sallama ba hakan baiyi masa daɗi ba yaso yaganta suyi sallama amma hakan ya faskara da zai tafi ne ya shiga ɗakinta ya ajiye mata wani tsadadden card a gefen kayanta sai wani ƙaramin akwatu da ATM card da wasu takardu.
Sai yamma liƙis suka dawo sun kuwa yi muguwar gajiya suka zube a parlourn suna mayar da numfashi kowacce ta jefar da mayafin itakam Beebah kwanciya tayi saboda sosai tafi kowa gajiya Gara su sun saba da komai da akayi musu ita kuwa komai sabo ne a gurinta hakance tasa jikinta ya gaji zuciyarta ta gaji brain nata shima ya gaji ta baje a parlourn tana juyi gashin nan yasha gyara sai kyalli yake abin ba'a cewa komai gashi an gyara musu farcensu harda jan lalle ya zauna das a fatarta tayi wani sihirtaccen kyau na ban mamaki Kilishi da kanta satar kallon surukar tata takeyi duk da yammatan nata ma ba baya ba amma sun samu uwarsu a fannin kyau hasken fata kawai zasu faɗa mata sai murjewa itama kuma fatar tata me karɓar sauyi ce cikin sati biyun har wani glowing takeyi.
Gyaran murya Kilishi tayi tace “nayi magana da Dr Mas'ud da dare zai zo Habeebah ki zama ready" cikin ɗoki tace “Ok Hajiya"

Miƙewa tayi ta nufi ɗakinta ta cire kayanta ta ɗaura towel ta faɗa wanka dake tana fashin sallah alwala kawai ta ɗaura kamar yanda Kilishi ta koyar da ita zama da alwala a kowanne lokaci ta dawo ta zauna saman dressing stool ta gyara gashinta ta ɗaure da ribbon a tsakiya ya sauka har tsakiyar bayanta ta shafa powder ita kanta tasan tayi kyau na mamaki ta tsaya tana ƙarewa kanta kallo taji an buɗe ƙofar ta madubi taga yanda suke kallonta Hudah tace “Barakallahu ahsanal kaliƙin Beebah wlh koni mace ban gajiya da kallonki saima boko ta ratsaki tukunna" murmushi tayi ta zauna tace.
“Yunwa nakeji Wlh" dariya sukayi sukace “waima kekam wanne irin cikine dake zakuwa ki iya azumin Ramadan gashinan yana tahowa saura wata biyu?" Harararsu tayi ta miƙe tana cewa “in kukayi wasa ma saina fiku yi" tana mgnr tana rankwashinsu suka kuwa zuba a guje ta zille musu ta nufi ɗakin hutawar Kilishi ta shige bayanta ta ƙanƙameta tana dariya itama sun bata dariya tace.
“Dama haka kukeso mala'ikin naku ya tafi zaku addabeni zakuyi bayani rubuta duk kalar rashin jinku zankeyi a littafi in yazo na bashi" zaro ido Beebah tayi tace “na shiga uku an fasa aurena

Kilishi Wlh idan kika haɗamu da Bro kisa ne kawai nikam na nutsu na daina kai taking care Wlh Bro zai hukunta ku babu ruwana"

Hudah ce tace “ai kafin ya dawo ta manta yauwa Kilishi wannan karon wacce ƙasa zamuje siyan kayan sallah?" Harararsu tayi tace “Aifa nice marainiyar wayon ku to kuje ku tambayi Mai martaba mana ko kuma ku kira Babban Yaya ku tambayeshi" Iangwabar dakai Khaly tayi tace “Ai ko Ya Naseer bamu isa mu tambaya ba yanzu asamu gwale$^2$ Hajiya kece dai zaki faɗa mana inda zamu Ni dama zaki yarda Allah banson azumi a kasar nan Dubai nakeson muje muyi azumi ko Saudi" Hajiya Kilishi akwai son farantawa yaranta hakanan tace “Shikenan zansa ayima Habeebah passport saiku tafi Saudiyya tunda ita bata taɓayin Umrah ba in yaso dagacan in kunyi sati biyu saiku wucce Dubai ɗin" wani tsalle sukayi suka rungumeta itakam Beebah jikinta ne ya mutu komai ya kwace mata zuciyarta tayi rauni “to wannan wanne irin family ne Habeeb ya koka mata matsaloli haka Hajiya Kilishi ranar da aka kawota amma ita har yanzu bata fara ganin matsalar ba ya kawota matsayin ƴar aiki amma mahaifiyarsa ta ɗaga darajar ta ta mayar da ita ƴa a gurinta Bama ta jinginata da aikin in har ba'a gaban sauran mutanen gidan bane, su kansu mutanen gidan cewa suke Hajiya wannan yarinyar tamafi Sakina samun fada a gurinki" saidai tayi murmushi tace “to ai kowa da kalar baiwarsa wai yau ita Habiba bamagujiya ita ce zata tafi ƙasa me tsarki ta gana da ubangijinta data sanshi ta fahimceshi kwanan nan?" Saurin share hawayenta tayi saboda tasan sarai Kilishi batason kuka ta miƙe zata fita ta riƙota tace “Akwai damuwa ne Habeebatullah?" Girgiza kai tayi ta rusuna ta kama hannun Kilishi tace “a duk lkcn da kukayimin wani abin alkhairi nakanji bankai nan ba yaushe matsayina yakai aimin haka sannan shine sila kuma tunanin mahaifiyata da Babana yakan bijiromin irin rabuwar da mukayi dasu dutsi a hannun riga dominsa....."

Rufe mata baki tayi lkcn da Hajiyan soro take shigowa tace “Shikenan Habeebah Sarkin rigima bazaa kuma ba ku tashi kuje" miƙewa sukayi dukkansu Hajiyan soro tabi Habeeba da harara bata daina hararарta ba Saida suka fice ita kanta Beebah ta fahimci Hajiyan soro da Hajiyan ƙofa basa sonta saboda kullum cikin hararарta suke wannan tasa bata fiye shiga sharafinsu da ƴaƴansu ba komanta tafi yinsa a inda aka ajeta wai a haka ma gara Hajiyan soro ita Hajiyan ƙofa yaranta ma ta hanasu mu'amala da Habeebah a cewar ta ita kawai yarinyar batayi mata ba har tana cewa garin yakabe$^2$n Kilishi saita ɗauko musu ajalinsu sauƙin ma da take samu dake ana shayin Kilishi da ƴaƴanta tunda sune manya kuma sune masu faɗa aji a gidan shine kawai yasa take shanyarta a inda takeso.
Kilishi ce ta katse shirun da cewa “Soro ya akayi ne?" Hankalinta ta dawo dashi ga Kilishi tace “Gulma ajali Hausawa sunce in baayi ba a mutu yanzu na fito daga gurin Mai martaba ina turakarsa yana Parlour naji Wannan makirin Lukman ya shigo yana cewa wai akwai wani abu da aka rufe a gdannan da ya kasa gane menene amma tabbas bincike yana nuna masa akwai

wata rufaffiyar ƙura da take shirin tashi a gdannan, to kinsan Mai martaba bai fiye sauraron shirme nan ya dagansa tsawa yace baison shiririta, shine suka koma mgnr ƴaƴan nan shine Alh Lukman ɗin yake cewa tunda an samu Habeeb ɗin ya tafi yanzu ayi maganar aurensa da Khausar shi kuma Naseer za'a haɗashi da Mufeedah Yassir da Hanifah su kuma matan Khaulatu da Aliyu Amna da Bashir Khalisa da Ibrahim Hudah da Isma'il kuma Mai martaba yace dukkan auren za'ayi su ne nanda shekara ɗaya...."

Gumi ne ya karyowa Kilishi tayi saurin tashi zaune tace "Habibu da Khausar Mai martaba ya manta yanada wadda yakeso bayan nan ma ya manta cewa kaf wannan family ɗin babu yarinyar da Habeeb ya tsana irin Khausar kayy ina gsky a sake lale nikam inajin tsoron lamarin Habeeb irin kafiyar mahaifinsa gareshi" taɓe baki Hajiyan soro tayi tace "Yo tunda bashi ya haifi kansa ba haihuwarsa akayi ai dole ya haƙura kamar yanda kowa ya hkr Ni Wlh nama ɗauka ya hkr da yarinyar nan daya sheƙa yaga babu ƙwayar"
Miƙewa Kilishi tayi tace "Shi Allah Sarkin daidai ne amma Wlh nima ban karɓi Khausar matsayin suruka ba haba koda dai naka sai naka amma ai kowacce ƙwarya tanada abokin burmi Meye Habeebu zaiyi da Khausar kawai saboda yaro bashi da ƴanci shine za'a koramin shi Japan sannan ayi masa tukuici da wannan fitsararriyar yarinyar da iyayenta suka jiƙa suka lalata to wallahi da sake dadai abawa me kaza kai gara a bashi romon koda bread ya lasa"

Riƙe haɓa Hajiyan soro tayi tace "Ni Zulaihatu to banda abinki Ummusalma wannan hukunci ai kinsan kamar da ƙasa tabbatuwarsa inji me ciwon ido tunda suka shiga suka kulle da wannan makirin ƙanin nasa bare dama ku ya daɗe yana haƙonku kada ki manta tun akan Hisham babban Yaya yaso haɗashi da kanwar Hajiya Indo Safiyya kuka zille dole aka barta to yanzu kuma kema kinsan ba ƙaramin shiri zakiyi na rusa wannan shiri ba domin kuwa Khausar ƴarsa ce ta cikinsa daga ita sai Aliyu ya haifa kinsan kuwa ko duniya zata tashi saidai ta watse don kuwa me hana auren nan sai ƙudurar Allah babba"
Sosuwar da zuciyar Hajiya Kilishi tayi ta sanyata barin dakin hutun ta nufi ɗakinta tana kaiwa da kawowa saboda ba Habeeb ba ita kanta Allah ya sani bata kaunar jinin Hajiya Indo ganin shaiɗan yanata yimata ayyane ayyane yasata dauro alwala ta tayar da sallah tana roƙon Allah ya bawa Habeeb mafita cikin wannan cukurkuɗaɗɗen lamari na rayuwarsa gabaɗaya sai taji tana tausayinsu dagashi har Habeebah ta shaida ta haƙiƙance Habeebah nason mijinta so na gaske shima kuma son kyautar rai yakeyiwa matarsa batajin akwai wani dalili da zaisa Habeeb ya iya hkr da Habeebatullah matuƙar ba mutuwa ba.

_IDAN KIKA KARANTAR LITTAFI BAKI BIYANI BA BAN YAFE BA._

[4/18, 1:30 PM] AM OUM HAIRAN: BMGJY

KIYIWA GIRMAN ALLAH KI BIYANI HAƘƘINA KAFIN KI KARANTA NORMAL 300 PC 600, KI BIYA TA WANNAN HANYOYIN ACCT DETAILS 0255526235 FAUZIYYA TASIU GTBANK KO KATIN WAYA MTN TA WHATSAPP NUMBER NA 09013718242 ƳAN NIGER ZAKU TURA KATIN AIRTEL 400CF TA WANNAN NUMBER +227 95 04 58 22 SAIKU TUROMIN SCREENSHOT NA SHAIDAR KUN TURA MATA NIKUMA NASAKU A GROUP.

*17-18*

★★★~~~★★★~~~★★★

Zaman kusan awa biyu tayi kan sallayar ta rasa tudun dafawa hakanan gwiwa a sage ta tashi ta fita dinning ta tarar masu kula da ɓangaren abincin har sun shirya komai na dinner ta zauna ta buɗe tuwon shinkafa miyar zogale ta dauki mazubi zata zuba Beebah ta fito da sauri tana cewa "Ayyah Hajiyanmu yau kin manta nice zan haɗa Miki abinci tun dazun naketa leken jiran fitowarki"
Murmushi tayi ta gyara zama tace "To Beeban auta a haɗamin" kunya Hajiya ta bata ta juya zata gudu taji an riƙeta ta ƙyalkyale da dariya tace "Allah Hajiya kunya kike bani in kince Beeban auta dinnan waima kunyi waya dashi kuwa ya sauka ko har yanzun suna saman gajimare"
Tana mgnr tana langwabewa salon shagwaɓa Hajiya ta harareta tace "ai kin fini kusa dashi ba mijinki bane ki kirashi mana kiji Ifyrsa" shiru Habeebatullah tayi  da mgnr don batada kalmar ƙarawa itadai tasan yanda tsoron Bro ya ɗarsu a ranta bazata iya haike masa ba gara ma idan shine ya kira.....

Ƙirrr wayar Kilishi ta fara ruri bayan ta gama haɗa mata abincin suka kalli wayar a tare "Autana" sunan da Hajiya tayi saving numbersa dashi kenan suka haɗa idanu da Hajiya tayi saurin juyawa zata bar gurin Kilishi tace.
"Kai kajini da kitifaffiyar yarinya yanzun ki titsiyeni kina tambayata mijinki sannan ya amsa ya kira ki gudu" Turo baki tayi tace "Kayy Kilishi bafa niba ke yakeson jin...." Rankwashi ta zuba mata tace "Kaniyar me gardama ɗauki Ni kibani guri" ɗaukar wayar tayi ta danna accepted ta nufi ɗakinta ta kulle ta kara a kunnenta ya sauke numfashi yace "Matar da bata damu da ya mijinta yake ba" lumshe idanunta tayi tace "ya akayi kasan nice?" Wani gwauron numfashi ya sauke yace "zuciyata ce ta amshi saƙon mahaɗinta anya Beebah zan iya rayuwa Ni kaɗai a

ƙasar nan Wlh ina cikin yanayi bansan Meye ke damuna ba nikam tunda aka sarƙamin rigar girma aka ɗaureni da igiyoyinki uku na fara fuskantar canji inajin kamar bazan iya cika alkawarin dana ɗaukar wa zuciyata akanki ba"
Abinka da ƙuruciya bata fahimci komai ba cikin kalamansa saima kwantar dakai da tayi tace "cikin kane yauma yake ciwo?" Fasali yaja yace kusan hakane gashi ina buƙatar bargo me taushi wanda yake numfashi kamar Ni Beebahta garin akwai sanyi waither ɗin su zata wahalar dani...."

Dariyarta ce ta katse masa furucin tace "Wai bargo me numfashi to a ina ake samun bargo me numfashi koda yake rayuwarku ta birni babu abinda bazaku iya samarwa ba ɗan birni nikam ina ganin tunda bazaifi ƙarfinka ba ka siya kada sanyin yayi maka illa" takaici ne ya sashi yin ƙwafa yace "shidai yaro kawai sunansa yaro bayan wanda nake dashi ƙarfi da yaji yafi ƙarfina kawai ki tayani addu'a kuma kiyi fatan kada a dawo Miki da gawar mijink....."
Da sauri tace "Bari don Allah Bro banaso Wlh ina tsoron mutuwa saboda itace Ummul aba'isin komai na lalurar rayuwata na tabbata da ace yaya Tani bata mutu ba da yanzu aurena dakai bai zama silar tuɓe rigar albarkar iyayena ba Bro inasonka fiye da yanda nakejin kaina a zuciyata amma ina tsoron irin abinda kayimin jiya don Allah karka ƙara banaso Nima na mutu banga ƴaƴana ba....."
Sosai kalmar ta ta ƙarshe ta bashi dariya yayi me isarsa sannan yace "is very funny My wyf kinajin tsoron matakin farko har kina roƙona karna ƙara sannan kuma kinason zuwa matakin ƙarshe to ta yaya wannan shirmen naki zai yiwu?"
Biye mata yayi sukayita shirmensu ko ba komai yana samun nutsuwa da muryarta sun ɗauki dogon lkc suna hira kafin suyi sallama yace ta kaiwa Kilishi ta fito takai mata a kunyace ta karɓa suka gaisa tanayi masa tsiyar yanzu tunda yabar zuciyarsa a gida ai ta rinƙa jinsa kullum.....

Itadai sulalewa tayi ta nufi dakin baccinsu ta tarar duk sun kwanta suna latsa waya taja bargo ta kwanta tana karanto addu'ar data sawwaƙa bacci yayi gaba da ita, sai asuba suka farka tayi wanka kamar yanda taga al'adar su Khaly da Hudah ta koma tana gyara musu ɗakin kasancewar itan ba sallah zatayi ba bayan ta gama ta nufi kitchen shegen karambani ne da ita Habeebatullah komai da ruwan ka kowa ya santa kuku har nemota yakeyi in zaiyi aiki saboda tace masa itama girki takeson koya har tana cewa ko ruwan tea ya dafa bai kirata ba wuta balbal aikuwa ranar Hajiya Kilishi da sauran yaran gidan sunci dariya wai wuta balbal shida aikinsa.
Dake tanada fahimta sosai babu wani abu da yake bata wahala indai taji a ranta zatayishi a wannan taƙin ne kuma Hajiya Kilishi tayi ruwa tai tsaki aka mayar da ita makaranta Dr Mas'ud yayi mamakin kwanyar yarinyar da akace masa daga kauye take SS one yasata sai gashi tana neman fin yan SS one ɗin ganewa saboda lesson ɗin da takesha a gida Hajiya Kilishi tayi mata

Hudah da Khalisa suyi mata shima mijin ɓoyen idan ta saci jiki ta saci wayar Kilishi ta ƙule ɗaki yayi mata sukayi jarabawar zangon karatu na ƙarshe dake dama karshen shekara aka kaita da ƙyar bayan ankai ruwa rana ta samu na biyu don badon maths data samu matsalar maki ƙalilan ba ita zata karbe kambun first class aikuwa Ashe tun kafin ma a bayyana musu sakamakon Habeeb ya sani don result na Habeebatullah Habeeb ya jima a wayarsa.
Kowa Saida ta burge shi a wannan rana hatta Hajiyan soro dake lecturer ce Saida taji Habeebatullah ta mugun shiga ranta kyauta kuwa harda Mai martaba a bata gift gift na ban mamaki Mai martaba ya bata zoben gold da agogo yasa Hajiyan soro ta siyo mata masu kyau da tsadar gaske familyn yan boko sarakai kuma masu tashen hatimin nasara a Afrika ma ba iya Nigeria ba Allah ya jarabci wannan family da son mutum gifted yanzu darajar ka zata ɗaga.
Itakam Hajiyan soro ɗan kunnen gold ta siya mata babba, Habeebatullah banda hawaye babu abinda takeyi wai yau ita bamagujiya wacce take yawo tsirara² mara galihu wacce ake ƙyamata itace kowa keson gani da kuma ɗaukar hoto da ita.

Allah kenan tabbas idan ka rikeshi zai isar maka amma fah idan ta tuna ɓoyayyen matsayinta a gidan da kuma tsohuwar aƙidar mutanen family ɗin jikinta ya kanyi sanyi harta kasa katabus, Ranar haka ta yini tulus babban tashin hankalinta yanda Mufeed yayan Rasheedah Turaki class met ɗinta Kuma ƙawarta ɗaya da tayi a ajinsu ya takura mata da kallo da hotuna duk inda tabi haskata yakeyi idan suka haɗa idanu yayi mata murmushi itakam tsoronsa ma takeji Mufeed Turaki Soja ne hutu yazo ya ishe bikin canjin ajin na ƙanwarsa rabon haɗuwa da ƙaddararsa yasashi jin shauƙin kasancewa a gurin.

Yaukam jinsa yakeyi kamar shine sarki Khalid saboda yanda zuciyarsa take haske yanajin tabbas yayi matar aure, hakanan taro ya watse suka nufi gda a motar Kilishi ita da kanta ke jansu Saida takaisu wani Gidan gyaran jiki aka gyara mata ƴammatan nata tayi musu siyayya sannan suka wucce gida suna zuwa Habeebah ko wanka ƙi tayi ta nufi dinning ta zuba abinci tanaci hanu baka hannu ƙwarya saboda yunwa sunata yi mata dariya Kawai jikinta ya bata ana kallonta ta daga kanta gabanta ya faɗi ta zaro idanu waje tace “Lahhhh Kilishi ya dawo....." Bata gama isar da saƙon ba ta kwasa da mugun gudu ta haye saman ta ruƙunƙumeshi tana kissing nashi ta ko ina tana cewa “I miss you My Bro double miss you....."
Mamaki ne ya cika Hudah da Khalisa ganin yanda ya wani lumshe idanu yana shafa bayanta da alama ma ya manta da akwai mutane a ƙasan ya ɗago fuskarta ya ɗora harshensa a lips ɗin ta ya sauke mata wani irin kiss me hucin bayyana sirrin zuciya ya janye ya ɗaga idanunsa da suke wani lumshewa kamar me jin bacci yace “Really My Wyf kinyi miss ɗina kamar yanda nayi naki?"
Dubanta takai ƙasa inda Mai martaba yake tsaye gabanta ya faɗi tayi saurin janyewa daga jikinsa ta nufi hanyar ɗakinta ya bita da kallo yana haɗiye wani mugun yawu gabaɗaya cikin

watanni shida tayi mugun canzawa kamar ba Beeban sa ba wata ajiyar zuciya ya sauke ya fara taka step na benen ya sauko ya rusuna cikin ladabi da girmamawa ya gaishe da Mai martaba Sarki Khalil bai wani dami zuciyarsa da tunanin wani abu ba saboda yariga yasan dabi'ar family ɗin nasu da mazansu da matansu duk jinsu sukeyi abu ɗaya musamman Beebah yarinya me tsayawa a rai duk ɓacin ran da kake ciki indai tazo guri saita sanyaka dariya shiyasa bai damu da yanayin daya gansu da Habeeb ba.

Dafa kansa yayi yace “Autan Kilishi Meye ya dawo dakai ne wata uku na ɗauka sai kayi shekarar?" Shafa sajensa yayi yace “Allah ya taimakeka wani uzuri ne ya dawo dani amma ba daɗewa zanyi ba bazan wucce 2 weeks ba" murmushi yayi yace “Wato dakai zamu fara azumi kenan" shima murmushin yayi yace “Allah ya taimakeka mun sameku lfy?" Amsawa yayi yana fita yace “Dama kuwa inason mgn dakai da na bari sai bayan sallah idan nazo ziyarar aiki zamu tattauna to tunda ka dawo idan ka huta sai kazo inason ganinka"
Duk da gabansa ya faɗi hakan bai hanashi gdy ba suka gaisa da Kilishi da rashin kunyarsu ta sanyata daskarewa a zaune su Hudah ma da suka kasa gane lamarinsa da Beebah suka gaisheshi ya amsa musu babu wani annuri suka tashi sumsum suka fice daga parlourn ya matsa kusa da Kilishi ya ɗora kansa a cinyarta cikin shagwaɓa irin ta sangartattun yarannan yace “Hajiyata Help me please!"
Da rashin fahimta ta dubeshi tace “Name kuma Autan maza nayi zaton dai Beebah ce kuma gata taka ce" iska ya furzar ya shafa kansa yace “Hakane Kilishi amma...." Sai yayi shiru ta zubansa idanu gabanta na faduwa tace “Amma me?" Ƙasa yayi da kansa yace “Hajiya tun lkcn da jikina da ruhina suka karɓi canjin suna daga saurayi zuwa magidanci me iyali komai nawa ya sauya a baya bana wani damuwa da kaɗaici ko rashin abokiyar rayuwa, yanzun kam Wlh na fara gazawa ina buƙatar matata a kusa dani...."

Yanda Hajiya Kilishi ta tsura masa idanu ne yasashi haɗiye mgnr can ya nisa yace “Ki...ki fahimceni Hajiya wannan lamarin yamin tsauri ko bazaki bani itan ba ki amince min daga lkc zuwa lkc nake samun nutsuwa da it....."
Dagansa hannu tayi tace “Ya isa Habeeb kul baka kiyayeni ba ban amince ba nace ban yarda ba kaje kaci gaba da hƙr da kuma azumin da kakeyi na nafila a baya zaifi maka amma gsky bazan baka Habeebatullah a wannan ritsin ba ko zan baka matarka sai komai ya daidaita banason son zuciya kaje ka jefa yarinya a matsala danginka da son kai babu me ganin laifinka"
Ya tabbatar Kilishi bazata fahimceshi ba tunda har taki fahimta hakan yasashi miƙewa yace “shikenan Kilishi idan na mutu kin huta...." Bata kulashi ba ta miƙe ta nufi sama ta shiga ɗakinta tayi wanka tayi sallar magrib tayi shirin kwanciya sannan suka fito dinner, harda Habeeb Beebah na ganinsa taji gabanta ya faɗi kamar ta juya babu dama ya kafeta da ido kwata² ta shafa'a da yana gidan rigar jikinta ta bacci ce airmles iya gwiwa ta kame gashin nan ta daureshi

da ribbon tayi masa manyan tuka guda biyu ta sake shi a baya.

Ji tayi ranta yana faɗa mata ta juya ta ɗauko hijjab saboda zuwa yanzu tasan darajar suturta jikinta, kafin ta juya taga ya miƙe yace “ki kawomin coffee da cake"
Kallon Kilishi tayi itama itan ta kafe da idanu shikam bai jira me zatace ba yayi tafiyarsa ɗakinsa dakin da batamasan inda zata nemosa ba saboda tunda tazo gidan bata taɓayin bangaren da dakin samarin gidan yake ba.
Khaly ce ta miƙe tana cewa “shi Bro ya cika takura yanzun kuma ke ta gangano Wlh ya cika sa aiki bari nakai masa" harararta Hudah tayi tace “Allah yasa ya ɓalle miki ƙafa kazallaha ai yaganmu tun kafin ta fito baice mukai masa ba Saida ta fito ke nifa yau yanayin Bro tsoro yake bani tunda ya dawo sai wani kumbura yake kamar yiss" zama ta nemi guri zatayi Kilishi ta sauke fasali Allah ya sani batason shiga tsakanin mace da mijinta amma hakan shine maslaharsu ta lura idanun Habeeb rufewa sukayi ya manta abinda hakan ka iya haifarwa yanzu abin tsautsayi ba'a tara sani da lamarin ubangiji idan yaje yayi mata ciki kuma ya zasuyi?"

_IDAN KIKA KARANTAMIN LITTAFI BAKI BIYANI BA BAN YAFE BA._
[4/19, 9:14 PM] AM OUM HAIRAN: BMGJY

KIYIWA GIRMAN ALLAH KI BIYANI HAƘƘINA KAFIN KI KARANTA NORMAL 300 PC 600, KI BIYA TA WANNAN HANYOYIN ACCT DETAILS 0255526235 FAUZIYYA TASIU GTBANK KO KATIN WAYA MTN TA WHATSAPP NUMBER NA 09013718242 ƳAN NIGER ZAKU TURA KATIN AIRTEL 400CF TA WANNAN NUMBER +227 95 04 58 22 SAIKU TUROMIN SCREENSHOT NA SHAIDAR KUN TURA MATA NIKUMA NASAKU A GROUP.

*19-20*

★★★~~~★★★~~~★★★

Bata ida wannan tunanin ba taji wayarta tayi ring tana dubawa taga saƙo ya Turo mata wai ta haɗo masa da peppersoup na naman rago.
Takaici ne yasa Hajiya Kilishi duban Beebah tace “kije ki daukar masa abinda yakeso Hudah ki rakata takai masa kuma karki daɗe zamuyi lesson so naki kuyi WAEC tare da ƴan uwanki"

shauƙin jin ance zatayi WAEC yasata farin ciki ta nufi kitchen ta haɗa masa duk abinda yace yanaso ta ɗauko hijjab tasa ta Hudah ta rakata har ƙofar ɗakin sannan ta juya tana cewa “kada ki ƙwankwasa saina tafi don Allah Ni tsoron tujararsa nakeyi"
Itakam Beebah tura ƙofar tayi tajita a buɗe ta shiga tare da furta sallama cikakkiya da ta maƙale a ganɗarta ta juya da sauri zata fice ƙirjinta na lugude taji yace “Habeebatullah karki fita...."
Ƙamewa tayi ƙam a gurin zuciyarta na harbawa musamman Ikcn da taji takunsa a bayanta ya zagayo ya karɓi kayan hannunta ya aje saman wani ɗan Glass table dake gaban gadonsa ya dawo ya tsaya a gabanta yana shafa gargasar ƙirjinsa yakai ɗayan hannunsa ya riƙo hannunta ya dagashi zuwa ƙirjinsa hakan yasata sulalewa ƙasa tana gwama numfashinta.

Firgici bayyane a kan fuskarta ya nemi guri kusa da ita ya zauna ta yanda bata isa tayi motsi ba bare tunanin gudu yazo mata ya ɗauki ƙaramin glass cup ya zuba coffee ɗin itama ya zuba mata ya mika mata kanta na ƙasa ta girgiza masa kai alamar batasha.
Ajewa yayi ya fara kurɓar nasa yana sake ware injin idanunsa akanta yau ganinta yake kamar wata sarauniya, yau tafi masa kullum kyawu da kwarjini yau jinsa yake cikakken namiji shikam a yau yanajin kamar bazai iya hana kansa samun nutsuwa da nutsuwarsa ba.
Da wannan hasashen ya ja abinda ta zubo masa peppersoup ɗin ya fara kaiwa bakinsa ya lumshe idanunsa ya buɗe akanta har yanzu kanta yana ƙasa ta kasa iya ɗagowa su haɗa idanu saboda Allah ya sani ganinsa takeji kamar wani dodo ace sangamemen ƙato kamar Habeeb ya zauna dagashi sai gajeren wando shima wandon irin me kama jikin nan duk wani shati na halittarsa ana gani.

Tashi yayi ya shiga bayi ya wanke hannunsa yayi brush ya fito ya tsaya a nesa da ita ya lumshe idanunsa ya kira sunanta cikin wata irin karayayyiyar murya data sanya jikinta karɓar wani saƙo na yarrr da batasan ta inda ya ɗarsu ba, kafin ta gama dawowa da nutsuwarta ya ɗagota ya zubanta idanu yana fitar da wani huci akai akai tana shirin ƙwacewa ya narke mata kai yace “Habeebah Please ina buƙatar taimakonki don Allah kada ki yarda ki zama sila Wlh abinda ya dawo dani kenan nakasa jurewa idan na cika takurawa zamana a Japan zan iya faɗawa zina itako zina ko a baya kinsan haramun ce Beebah ki taimaki mijinki don Allah kada ki bari na cutu banida wani gata daya wucceki idan kika gujeni a wannan lokacin bansan ina zani ba...."
Duk da yanda yake ƙara matsarta yana ƙoƙarin zamar da hijjab ɗinta hakan baisa ta fahimci kalamansa ba saida taji ya jefar da hijjab ɗin ya janyota ya haɗe gaf ɗin dake tsakaninsu ya mata muguwar matsa kamar zai mayar da ita cikinsa.
Wannan yanayin ya tabbatar mata da nufinsa da ita a yau hankalinta ya tashi zuciyarta ta karye tsoronta ya nunku gata a ɗakinsa yau waye zai ceceta? Hawaye ne ya zubo daga idanunta zirrrr ƙirjinta yaci gaba da dukan tambarin da yakeyi tanaso tayi wani yunƙuri amma riƙon tsaurin da yayi mata ya hanata samun damar motsa koda ƙaramin yatsanta ne saima ƙara narkewa da

tayi a jikinsa.
Shi kansa yanajin yanda jikinta da zuciyarta ke rawa saidai ya fahimci ba iya tsoron rashin sabo bane yasa take shiga wannan yanayin harda tunanin irin yanda taga anyi ma ƴar uwarta Tani a kan idanunta da kuma mutuwar da Tani tayi ita har yanzu tunaninta yana bata indai yasanta ɗiya mace itama mutuwa zatayi wannan ne yake ƙara rura wutar tsoronta a cikin ruhinta.

Ɗagata yayi cak ya dorata saman dressing stool ya tsugunna a ƙasa ya sanya hannunsa cikin rigarta ya ɗora saman nipples ɗin ta yana ƙoƙarin kamawa tayi saurin buɗe idanunta tare da riƙe hannun nasa da ƙarfi tace “Don Allah...." Saurin lumshe idonsa yayi tare da haɗe bakinsu yayi baya da ita ya miƙe tsayi ya ɗan ranƙwafa kanta kaɗan yana tsotsar harshen nata da wani salo na narkar da zuciya itakam tata zuciyar neman tarwatsewa takeyi saboda razani batasan sanda hawaye ya ƙwace mata ba saijin harshensa tayi saman fuskarta yana lashewa tare da sanya ɗayan hannunsa yana shafa ginshikin nononta yanayin sama a hankali yana shafo nipples ɗinta kamar maiyi mata susa.
Ana gobe zai tafi dagashi har Beebah kamar waɗanda akayiwa mutuwa haka suka kasance babu walwala don ma Khausar na amfani da kirsarta da shekaru da tafi Beebah tana ɗauke mata hankali a fakaice tana nuna mata ai cigabansu ne gabaɗaya da wannan Beebah ta ɗan saki jikinta, tare da Khausar suka haɗa masa kayansa suka shirya masa a jakar da zai tafi da ita har cincin da cake da donut suka shirya masa kayan snacks kala-kala harda na banza duk suka haɗa masa dake ranar ba'a ɗakin Beebah zai kwana ba haka ya kwana kamar Maraya Khausar tayi iya yinta taga ya saki jiki da ita amma fir yaƙi kwana yayi yana zagaya ɗakin shikam badon yasan Beebah bazata taɓa bashi hadin kai ba da ya tafi yaje ya samu nutsuwa da ita.

Tsarin tafiyarsa ta safe ce tun asuba da sukaci gaba da shirye-shiryensu yakebin Beebah a gindi a gindi duk inda tasa ƙafarta shima sama yakeyi, sarai Khausar ta lura da yanayinsa koda yanayin yanda doguwar rigar jallabiyar jikinsa take a ɗage saitin Sandar majalisar sa.

Itako Beebah dake ba abinda yake gabanta kenan ba kuma hankalin ma sama² ne yasa batama fahimci halin da yake ciki ba sai lokacin da Khausar ta matso saitin kunnenta tace “Ki bawa Hero ɗinki tallafi jin dadin namu zata ɓalle a jikinsa fah....." Sai lokacin ta lura aikuwa gabanta ya faɗi cikinta bayason sex ko kaɗan indai Habeeb ya kusance ta yini zatayi mararta na ciwo gashi ta fahimci irin kallon da yake binta dashi na jiran damarsa ne kawai.

Miƙewa Khausar tayi ta ɗauki ruwa a freegde ta fice musu daga kitchen ɗin, kamar me jira haka ya nufota ta miƙe da sauri har mararta na amsawa ta ɗan ja baya ya riƙo hannunta da sauri yace.

“Please Wyf karkimin haka tafiya zanyi ki bani nutsuwa don Allah" noƙe kafada tayi ta turo baki tace “Ni meye yasa kake damuna ne naga da mace ka kwana Hero kake fahimtar uzurina wlh wahala...." Rufe mata baki yayi ya matso da bakinsa saitin fuskarta yace “nasani a hankali zan biki Please....." Yanayinsa ne ya kashenta jiki tasani kome zatace masa ba sauraronta zaiyi ba don tabbatar shiɗin daban ne a kitchen ya rareta tas taso hanawa taga ya jima da nisawa hakanan tayi masa doggie yayi abinda zai yi ya samu gamsasshiyar nutsuwa ya kwantar da ƙirjinsa a bayanta ta zame tayi ƙasa tana dafe cikinta daya dunƙule mata waje ɗaya.
Hannunsa yasa ya shafo cikinta yayi murmushi yace “Very soon zan dawo bby kayi hkr nasan zakayi missing Dad ɗinka" janyewa tayi ta sanya kayanta ta nufi ƙofar ta buɗe ta baya ta nufi part ɗinta ta faɗa wanka tana wankan taji shigowarsa ɗakinsa ya shiga yayi wanka ya fara shirinsa ta fito ta tayashi shiryawa.

Sallama yayi musu me kyau suka rakashi airport Najeeb ne yake drivern ɗin yana tsokanar Habeebah dake itan ba ma'abociyar son hayaniya bace saidai tayi murmushi wani kuma abin khausar ta rama mata, ita kewar mijinta kawai itane ta dameta musamman da sukaje airport ya matso ya riƙe hannunta ya zubanta manyan idanunsa.

Ya jima da fahimtar yanayinta hakan yasashi ɗago kanta yayi kissing lips nata yace “ko mutuwa nayi kiji a ranki ni nakine Wyf bare ina raye rabuwa ce ta ɗan lokaci, amana nabar Miki kanki da Bbyna da duk abinda ya shafeni ki kulamin da kanki!...." Hawaye ta share masu dumi ta cire hannunta a nasa ta kaɗa masa kai tace “Insha Allahu zanyi bakin ƙoƙarina kaima ka kulamin da kanka.

Sakinta yayi ya juya da sauri ya nufi matakalar jirgin ya shiga itama ta juya tana tsane hawaye da tisue ta shige mota suka juya suka nufi gidan sarauta Gaban Beebah na faduwa suka shiga gdan sukayi parking ya saukesu Khausar dake ƴar gda ce ta nufi part ɗin Hajiyan soro itakam Beebah gaisawa kawai sukayi ta miƙe ta nufi sashin Hajiya Kilishi tana babban parlour tana ganinta ta miƙe ta tarota tana cewa.

Sarkin yawo kukan bakwa gajiya Beebah ke ko nauyin jikinki bakiji koda yake ɗaurin gindi kika samu nayi magana mijinki yace motsa jiki kikeyi" ƙasa tayi da kanta cikin ladabi tace “Wlh Kilishi ciwon mara ne yake damuna har bacci yake hanani" cikin jimami tace “Subhanallahi kuma kunje asibiti?"

Ɗaga mata kai tayi tace “Munje sun duba sunce kwanciyar Bbyn ne ba daidai ba amma suna saka ran zai koma daidai kafin lokacin haihuwa" ajiyar zuciya Kilishi tayi tace “To Allah yasa yanzu me kikeso kici me za'a dafa Miki?" Dariya tayi sarai Kilishi tasan halinta itama tayi dariya tace “shikenan in kin gama dariyar sai ki faɗa" rufe idonta tayi tace “Kunun tsamiya nakeso da wainar gero...." Zaro ido Kilishi tayi tace “taɓ amma Wannan jikan namu akwaisa da iya baro aiki bari nasa ayi Miki kije ki kwanta kafin a gama"

Ɗakin Kilishi tashige ta kwanta bata kuwa jima ba bacci yayi gaba da ita ba ita ta tashi ba sai yamma likis ta tashi ta tarar duk abinda tace an haɗa mata suka tafi gida sunaci suna hirarsu dare yayi kowacce ta nufi ɗakinta.

Da farko zaman nasu babu wata matsala lokaci guda abubuwa suka rinƙa canzawa musamman lokacin da cikin Beebah ya tsufa duk wani taimako da Khausar keyi mata ta daina saidai tayi idan bazata iya ba tabari gata da zurfin ciki ta kasa faɗa masa tana buƙatar ƴar aiki domin tana ganin hakan a matsayin shiga tsakanin mace da mijinta, musamman da kullum ya kira zaice mata Khausar ta kirashi tace masa anyi kaza anyi kaza, itadai takanyi murmushi kawai ta bagarar da zancen.

Wani abu dayake damun Beebah yawan baƙi da sukeyi ƙawayen Khausar kuma Bama iya mata ba harda maza haka zasu raba dare suna busa musu shisher a gidan itakuma tayita amai saboda bata kaunar ƙamshin flavor ɗin tun tana ma fitowa babban parlourn Saida fitowar ta gagareta saboda wasu abubuwan hankalinta baya iya ɗauka kusan karo biyu tana kama wata ƙawar Khausar Jidda suna romance da wani cikin abokan nasu a cewarsu da faɗa.

Abu na biyu da yasa ta daina fitowa indai taji motsinsu yawan kallo da samarin ke binta dashi jin kunnenta akwai lokacin da taji Wani cikinsu na cewa shifa yana haɗiyar yawu akan kishiyar nan ta Khausar ranar baram² suka rabu a gidan tanata fadan ita wlh sai tayi maganin Beebah ace don masifa mijin ta kama ta riƙe abokan nata ma da take samun nutsuwa dasu suma sun fara cewa sun fara haɗiyar yawu.
Beebah bata gane abinda take nufi ba shiyasa bata wani ɗauki abin da muhimmanci ba, itadai kullum burinta da addu'arta Allah ya rabata da cikin jikinta lfy.
Cikin hakan ne kuma ta kama wata rashin lafiya me zafi wadda ta sanya dole Hajiya Kilishi da tazo taga irin mugun zaman da sukeyi ta dauko Larai tace taje ta zauna da ita, Larai na kula da ita Kilishi nayi shikam Habeeb kullum cikin yo aike yake da kiran waya, kwananta takwas a kwance da yamma tana kitchen ɗin sashin nata ranar jikin nata da ɗan sauƙi, kunu take damawa taji bayanta ya wani amsa.
Ai batasan sanda takai ƙasa ba tana keta gumi ashe wasa farin girki lamarin na gaske yana tafe, ji tayi bayan ya ɗan saki ta yunƙura zata miƙe taji mararta ta riƙe babu shiri tayi zaman ƴan bori a gurin ta rinƙa matagugun azaba.

Baba Larai ce taji shirun nata yayi yawa ta nufi kitchen ɗin ta tarar da ita cikin mawuyacin hali ai da gudu ta isa kanta ta tallafota tana tambayarta menene? Babu damar mgn sai ido sai hawaye fita tayi da sauri tana ƙwalawa Khausar kira ta fito ɗaure da towel, Baba Larai tace “ko zaki kiramin Hajiya Kilishi Gimbiya Beebah ce batada lafiya ina tunanin haihuwa ce Azo a kaita asibiti....."
[5/13, 8:06 PM] AM OUM HAIRAN: _*Paid book 37-38*_

_Ku biya ta acct detail  3184512451 First bank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241._
_Normal 300 PC 700_
_Ƴan Niger zaku biya 500f ta wannan number +227 95 04 58 22_

_Ban amince a juyamin littafi ta kowacce siga ba_

★★★~~~★★★~~~★★★

Wani mugun tsaki Khausar taja tana yiwa Baba Larai wulaƙantaccen kallo tace “kuma Ni meye nawa cikin haihuwarta zakizo ki dagamin hankali kamar nice Habeebun da yayi cikin.....
Ƙara ƙasƙantar dakai Larai tayi zatayi mgn Khausar ta daka mata tsawa tace “ki matsamin anan munafuka in kinada abinyi kiyi mata in baki dashi ki zuba mata idanu duk abinda Allah yaga dama yayi, Ni banida lokacin batawa akan abu mara muhimmanci....." Fuuuu ta shige ɗaki Baba Larai ta girgiza kai lallai wannan mata takai mara imani.
Da wannan tunanin ta koma kitchen ɗin ta tarar da Beebah ciwo har yaci uban na baya daƙyar ta iya bata amsa lokacin da take tambayarta wayarta ta ɗauko cikin saa kuwa babu pin a jiki ta miƙa mata, a wahale ta kamo mata number Kilishi ta kirata ta sanar da ita abinda ake ciki, kafin wane wannan sai gata suka tattageta sai asibiti cikin ikon Allah kamar jiran isarsu asibitin ta haifo yaronta sankacece kyakkyawa me kama da ubansa.

Murna gurin Kilishi kamar akansa ta fara samun jika, da kanta ta gyara abinta bayan maijego ta huta suka koma gida.
Tun kafin su isa labarin haihuwar ya cika dangi masu murna nayi ƴan baƙin ciki suma ba'a barsu a baya ba suna nasu a bayan fage, kadama Khausar da yan fadarta suji labari sun kasa zaune sun kasa tsaye, duk inda takai ga iya makircinta wannan karon kasa ɓoye baƙin cikinta tayi hatta Habeeb Saida ya fahimceta a kalamanta aikuwa mutuncinta ya ciwu ba ƙarya don Saida ta gwammace dama tsautsayi baisa ta kasance matar Habeeb ba a wannan rana, ya wulaƙantata da gaske.

Gabaɗaya ya ɗauki hankalinsa ya mayar dashi kan Beebah da bbynsu yaso yazo yaga jaririn amma campany sunƙi bashi hutu dole haka ya hƙr saidai hotuna da aketa yiwa yaron ana tura masa da videos, a tsarin gidan sarautar duk jaririn da aka haifa mai martaba ne yakeyi masa huɗuba amma shi wannan jaririn bai samu wannan gatan ba, koda aka faɗawa Mai martaba samun ƙaruwar da ɗan nasa yayi baice komai ba Saida akayi zancen huɗuba nanne ya magantu da cewa ai kamar yanda ya yafewa uwar jaririn ubansa to shima jaririn ya yafesa. Beebah da taji wannan ɗanyen hukunci Saida tayi kuka kamar ranta zai fita wai akanta itakuwa wacce irin baƙar kadara ce data zama silar rusa shaƙuwa da soyayyar dake tsakanin uba da ɗansa?

Kilishi ce ta rinƙa tausarta da samu tayi shiru amma duk jikinta a sanyaye yake musamman

lokacin da Yaya Ahmad yazo yima yaron huɗuba tayi nadamar biyewa Habeeb su ɓata ran iyayensu, wai a haka ma gara shi akanta ita batama san makomarta da nata iyayen ba.
Yaya Ahmad dakansa ya shigo har ɗakinta ya tambayeta ko tanada sunan da takeso a kira ɗanta dashi? Girgiza kai tayi tace ta bawa Kilishi zabi.
Kilishi taji daɗin wannan dama da Beebah ta bata tayi murmushi tace “To a kirashi da Ibrahim Khalilullah" ajiyar zuciya Beebah tayi ta rungume ɗanta tana hawaye tace “Allah ka rayaminshi ka tsareshi ka albarkaci rayuwarsa" ranar suna ta zagayo akayi shagalin suna itadai Beebah kawai bin mutane takeyi da kallo komai ba daɗinsa takeji ba hankalinta ya haɗu yanzu iyayenta kawai take kewa da shauƙin gani. Bayan kwanaki da yin suna Kilishi tana kulawa da surukarta sosai kamar yanda zata kula da ƴarta ta cikinta har sukayi arba'in Beebah taci gaba da kula da ɗanta yaronta kyakkyawa me shiga rai.

Zaman nasu yaƙi daɗi kullum abubuwa ƙara lalacewa sukeyi ita Beebah dake ba ma'abociyar son hayaniya bace bata wani biyewa Khausar ko zata kwana tanayi mata habaici da baƙaƙen maganganu, saima dai tayi murmushi ta ɗauki ɗanta tabar mata parlourn. Gashi zuwa lokacin iskancin Khausar kullum ƙara gaba yakeyi har takai ba ko yaushe take zaman gdan ba kuma duk lokacin da taga dama tanada damar shigo da samarinta da ƙawayenta, abin yana damun Beebah saidai batasan ta yanda zata sanar da Habeeb halin da ake ciki ba.
Ana haka kuwa Habeeb yayi musu zuwan bazata, Beebah na kwance a ɗakinta ita da Hudais kamar yanda suke kiransa bacci ya ɗauke ta me nauyi kasancewar daren jiya sun kwana suna fama dashi ita da Baba Larai ciwon ciki ya hanashi bacci.

Ji tayi an ɗauke hannunta daga saman cikin Hudais data rungume yana bacci, aikuwa kamar an ɗala mata duka ta buɗe idanunta a razane ta saukeshi akan Habeeb ta tashi da sauri cike da matsanancin farin ciki tace “Hero....." Yanda ta kira sunansa da yanayin tsananin mamaki ya bashi nishaɗi ya ɗaga Hudais ya cilla sama ya cafe yaron ya buɗe idanunsa yana ƙifƙiftawa Habeeb ya haɗe shi da ƙirjinsa ya ɗora bakinsa a na yaron yana tsotsar lips ɗinsa yana sake saita injin idanunsa akanta.
Ƙasa tayi da kanta tana wasa da zara-zaran yatsunta tace “Sannu da hanya amma ka shammaceni shine ko a waya baka faɗa min zaka shigo ba" ajiyar zuciya yayi ya lumshe idanunsa yace “Yanayin kewarki da nake ciki itane ta hanani faɗa Miki zanzo nafison nayi Miki zuwan bazata" murmushi tayi tace “Ai Shikenan ka kyauta gara da ka dawo dama wannan photo copyn naka ya hanani sakat kwana biyu baya barni bacci da dare"
Kama kunnen yaron yayi ya murɗa a hankali tayi saurin riƙe hannunsa tace “Kay Hero...."
Dariya sukayi a tare yace “Faɗa zanyi masa daya hanamin ke bacci" murmushi tayi tace “tab ai ji nayi kamar raina ka taɓa kasan kuwa yanda nakejin Hudais a raina?"

Tsuke fuska yayi yace “Ya muke dashi a ran naki?" Zama tayi tace “Nifa yanzu ji nakeyi duk duniya zan iya hƙr da komai da kowa akan Hudais kuma zan iya cin mutuncin kowa akan Hudais kasan ma me...."
Ɗagowa yayi fuskarsa babu walwala yace “Harni kenan ko?" Yanda taga fuskarsa a ɗaure yasa gabanta faɗuwa tayi saurin saita nutsuwarta yayi ajiyar zuciya ya miƙe ya fice da yaron a kafaɗarsa hakan ya bata damar miƙewa tasa rigarta ta fito ta nufi kitchen ta haɗo masa kayan sha ta nufi ɗakinsa ta buɗe ta shiga ta aje masa yanata yima yaron wasa yaron bata ɓangale baki.

Tsiyayowa tayi ta miƙa masa ya ɗago yayi mata wani mugun kallo ta sunkuyar dakai jikinta duk yayi sanyi ta miƙe zatabar gurin ya riƙo hannunta ya tashi ya tsaya a gabanta yace “Na shafe tsayin wata shidda da damuwar rashin ki kewarki tana neman ƙarar da numfashina na kasa jurewa saboda damuwa tayimin yawa inason inzo in ganku dawowata ace irin tarɓar da zakiyimin kenan Wyf ɗan da kika sameshi dani yazo duniya ta dalilina wai yau shi kike faɗa min yafini a gunki ko?...."

Hawayen fuskarta ta share tace “baka fahimceni bane wlh ba haka nake nufi ba Hero idan da mutumin daya samu daraja da ɗaukaka a duniyata bayanka ne waye na amince na rasa komai akansa kaine Hero kayimin uzuri soyayyarka itace ta sabbaba soyayyar Hudais a zuciyata saboda shiɗin tsatsonka ne jikinka ne wlh da banasonka ba lallai nasoshi ba har na rinƙajin abinda nakeji akansa, kayi hkr idan hakan ya ɓata ranka....."
Rungumeta yayi yana sauke ajiyar zuciya yana shafa bayanta suka zube a gadon ta janye ta ɗauki cup na juice ɗin takai masa bakinsa ya kurɓa tare da riƙewa da hannunta yayi kissing yatsunta yace “komanki me kyau ne Wyf meye yasa nake sonki ne?"
Dariya tmbyr ta bata tace “Nima ina yawan tambayar kaina meye yasa" dariya sukayi tare ya kwantar da Hudais yace “ki taimakamin wanka nake buƙata kuma na gaji" murmushi tayi zatayi magana ya ɗora hannunsa a bakinta yace “Sai kinyi fah" karyar dakai tayi tace “Lissafina ya kwance kamar ba anan zaka sauka ba ai ko?" Harara ya maka mata ya nufi bathroom ɗin tasan abinda yake zuciyarsa bashida kaɗan wannan tasa tabisa sukayi wankan suka fito ta zaɓo masa kaya yasa bayan ta shafeshi da mai.
Ana shirin suna wasan zilliya so yake ya cafke ta itakuma taƙi sai waskewa takeyi da dabara dai ta bari ya kyaleta sa haɗe da dare.

Fita sukayi parlourn tashiga kitchen tana tambayarsa me yakeso ta girka masa? Bin kitchen ɗin ya rinƙayi da kallo cike da mamaki “Wannan sauyin kuma yaushe ya faru?" Murmushi tayi taci gaba da aikinta batare da ta bashi amsa ba, yasan tunda tayi shiru batada amsar badawa ne yaja numfashi yana bin komai da kallo harta gama ta zuba a flat suka koma dinning dake parlourn suka zauna sunacin abincin yana binta da kallo sai yanzu ya lura da ramar da tayi ya

kira sunanta ta ɗago yace “Kin rame kuma tun shigowata gdannan nake ganin sauye-sauye da bangane musu ba na tambayeki kuma kinyimin shiru"
Ƙasa tayi da kanta ya kuma kiran sunanta ta ɗago yace “ke fah nake saurara" a gajiye tace “Da kayi hƙr tunda ka dawo kome ke akwai zaka fahimta Hero don Allah ka daina tambayata akan lamarin gidannan" zubanta idanu yayi yana nazarin kalmar ta.

Ya daina tambayarta to in bai tambayeta ba wa zai tambaya? Bai kuma mata magana ba har suka gama ya miƙe ya dauki Hudais suka fice daga gidan karon farko da yaron ya fara fita batare da uwarsa ba a cikin watanninsa biyu da sati biyu.
Kai tsaye gdansu ya nufa a hanya Khausar taga motarsa Saida ta kusa yin karo saboda firgici duk da bata ganshi ba kasancewar bakin Glass ne da motar tasani ko tantama babu shine a ciki domin Beebah har yanzu bata wani son hawa mota ita kaɗai takeyi ba, shi kuwa bai gane motar ba saboda ba wani saninta yayi da ita ba koda sukayi clear ɗin sunayin kwana ta tsaya ta sauke ƙawarta Deedah da wani abokinsu tace suyi maza su nemi wata motar mijinta ya dawo zata tafi gida, yawon da baayi ba kenan ta nufi gda.
Habeeb kuwa yana isa gidan sarautar bai nufi cikin gdan ba kai tsaye ɓangaren Mai Martaba ya nufa ya shiga ya ishe shi a zaune saman Kilishi yanacin dabino, sallamarsa ya amsa masa ya gaisheshi da girmamawa amsawa yayi ya tashi zaune tare da zubawa Hudais idanu ya miƙa hannu Habeeb ya miƙa masa shi.
Zubawa yaron idanu yayi yana jinjina kai yace “Shine takwaran nawa?" Shafa sumarsa yayi yace “Shine dama shi ɗaya ne ai" murmushi ya miƙa masa shi yace “yayi kyau yaushe ka dawo?" Amsa ya bashi sukayi shiru na ɗan lokaci Mai Martaba ya miƙe yace “zan shiga ciki a gaida mutanen gidan"
[5/14, 6:24 PM] AM OUM HAIRAN: _*BMGJY Bonus 39-40*_

_Ku biya ta acct detail 3184512451 First bank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241._
_Normal 300 PC 700_
_Ƴan Niger zaku biya 500f ta wannan number +227 95 04 58 22_

_Ban amince a juyamin littafi ta kowacce siga ba_

Assalamu alaikum My Fan's shin ko kunsan cewa bigi sai bigi babban goro sai magogin ƙarfe, tabbas ramin kura sai ƴaƴanta,
Nasan zakuce yau dame kuma Oum Hairan tazo mana? To ku daina tambayar kanku sabbi kuma shahararrun kayan mata ne masu ban mamaki daga taskar Siyat yar mutan Katsinawan dukko da Oum Hairan.

Muna da kayayyaki kamar haka👇🏼
Maganin gyaran Nono, maganin ƙarin hips, Sirrin matsi na musamman, gumbar dagake babu wata, humra mai taken madarar ƙauna, muna dafa kazar amarya da haɗin jijjiɓi musamman don masu jego tare da aikawa ko ina kuke a fadin Nigeria, munada maganin sanyi wanda duk shaharar sanyi muddin kikayi amfani dashi yanda ya dace to kin rabu dashi kenan.
Sannan munada kaloli na kayan Malama A'isha Mai Da'ira musamman turaruka wanda ke da kanki saikin dawo idan kikayi amfani dasu domin zasu janyo Miki hankalin mijinki zasu sanya nutsuwa da fahimtar juna tsakaninku zaki zama tauraruwarsa domin an haɗasu ne da wasu keɓantattun ayoyin Alkur'ani mai girma domin sharewa mata hawayensu babu boka babu Mallam, karki manta cikin kalolin turarukan mu akwai wanda Bama taɓa siyarwa me kishiya saboda haka kiji tsoron Allah in kinsan kina da kishiya karki siyeshi domin gudun shiga haƙƙinta.
Mai buƙata DM me 09013718241.

★★★~~~★★★~~~★★★

Da sanyin jiki Habeeb yace “A fito lafiya Allah ya ƙara lafiya" shima tashi yayi ya nufi cikin gidan wani abu ne me kama da almara ya bashi mamaki lokacin daya shiga sashin Kilishi suna zaune ita da Hajiyan ƙofa  suka tareshi da farin ciki ya zauna suka gaisa Kilishi ta miƙa hannu ta ɗauki Hudais tace “Ashe sun dawo" kallonta yayi da sauri yace “su wa fah?" Murmushi tayi ta kawar da maganar da cewa “kai mana saukar yaushe?" Ajiyar rai yayi yace “wlh zuwan kenan Kilishi na sameku Ify ya wajensu Hudah" amsawa tayi tanama yaron wasa Hajiyan ƙofa tace “ina Khausar yarinyar kirki kwana biyu bata leƙomu ba" annunrin fuskarsa ne ya ɗauke Allah ɗaya ya manta da wata halitta Khausar a gidansa tunda ya shigo Beebansa ta ɗauke hankalinsa.

Murmushi Hajiyan soro tayi “komai yanada lokaci" abinda ta faɗa a ranta kenan ta miƙe tace “A gaishe su bari naje Hajiya amma dai a duba lamarin nan abin baiyi kama da tatsuniya ba domin megadin gidan ne ya tabbatar min da hakan" Habeeb baisan akan me ake magana ba shiyasa bai wani bawa maganar muhimmanci ba, bayan fitarta sukaci gaba da tattaunawa da Hajiya Kilishi saidai ya lura duk a tsarge take.

Shine yace “Kilishi baki tambayeni Beebah ba?" Murmushi tayi na yaƙe tace “abubuwa ne suka sha kaina tana Lafiya dai ko?" Cikin jin daɗi yace “To ƙalau nazo na tarar da ita amma bansani ba ko kafin nazo tayi cuta saboda naga ta rame sosai bayan ramar naga sauye-sauye a gidan na tambayeta taki bani amsa ko kinada wata masaniyar?"

Numfashi Kilishi ta sauke tace “Karka damu babu ciwon da Habeebah tayi kawai dai akwai abinda yake damunta nasha tambayarta tun kafin ta haihu sai tacemin babu komai nidai roƙon da nakeyi maka kasa ido sosai akan lamarin gdanka tabbas akwai ɓaraka wacce muka kasa gane daga ina take"

Jinjina kai yayi cikin mutuwar jiki yace “Shikenan Kilishi insha Allahu zanyi ƙoƙarin hakan na gode da shawara" shafa kansa tayi ya tashi ya fice bai koma gidan ba sai dare lkcn daya shiga part ɗin Khausar ya fara shiga ya tarar da ita saman sallaya da casbaha a hannunta

tana lazumi wanda a zahiri ƙarya takeyi jin tsayuwar motarsa ce tasata saurin shimfiɗa sallayar da ɗaukar casbin.

Zuba mata ido yayi baisan meye yasa kwata-kwata jininsa bai haɗu da Khausar ba indai zai ganta sai yaji yanajin haushinta amma yau sai yaji ta ɗan burge shi kaɗan.

Tasowa tayi ta tsugunna cikin salon sabuwar kirsarta tace “Wellcome My Paradise shigowa haka babu sanarwa?" Tayi maganar da sigar tambaya tana miƙewa ta miƙa hannu ta karɓi Hudais karon farko da yaron ya taɓa zuwa hannunta ta cillashi ta cafe harda juyawa tana masa rawa tana cewa.

“Yarona yafi na kowa yau Mom ɗinka ta hanani ganinka ta ɓoyeka ko kuma Dad ne keda alhakin laifin nan ne?" Zuciyar ɗa da mahaifi sai Habeeb yaji ta daɗa burgeshi, baidai ce komai ba ya karɓi Hudais ya fice can ƙasan maƙoshi yace “Good night ba haka taso ba amma dake ƴar duniya ce sai tace “Ok sir a huta gajiya sosai sleep well" tana faɗin haka ta rufe ƙofarta ta tsaya a jiki ta cilli da casbin da hijjab ɗin cikin baƙin ciki ta dawo ta zauna a gefen gadon tabbas bazata bari damarta ta kufce mata wannan karon ba ta shirya yin duk abinda tasan zaisa ta samu zuciyar Habeeb itama haihuwa takeso so takeyi yayi mata ciki.
Kwanciya tayi tare da ɗaukar wayarta ta kunna data aikuwa video call Yafi goma ta tarar tayi saurin amsa wanda ke shigowa yanzun Deedah ce tana kwance a gado ita da wani guy boobs ɗin ta a hannunsa Khausar tace “Ahhhh Deedah meye yasa kikemin haka ne Please zo ki cini....."

********

Hanyar shiga sashin Beebah yabi ya buɗe ƙofar parlourn wani ƙamshi me daɗi ya bugi hancinsa ya sauke ajiyar numfashi yanabin parlourn da kallo, ƙamshin Room spray na HAREEM na sake saukar masa da wata sihirtacciyar kasala.

Kamar ɗan maye haka ya buɗe ƙofar ɗakin ya shiga tana tsaye jikin madubi tana gyara gashinta ya zubanta idanu yana haɗiyar yawu kawai dama yau ta shirya jiƙa masa aiki ne, matsawa yayi ya kwantar da Hudais a gadonsa ya tako a hankali yana kallon fuskarta da taketa sakar masa murmushi ya ɗora hannayensa biyu saman bombom ɗinta yana shafawa a nutse ta lumshe idanuwanta tare dayin ɗage ta sauke masa wani sassanyan kiss a dokin wuyansa ta janye ta rungumeshi ta gaba boobs ɗin ta ya gogi ƙirjinsa ya saki wani siririn Nishi.
Janyewa tayi taje ta kulle ƙofar ta jashi suka shiga bathroom ita da kanta ta wanke abinta tas tasa hannu ta kama sarauniyarsa da taketa Nishi ita kaɗai tare da danna kanta dake tsiyayar da ruwan daɗi.

A hankali ta ɗora lips ɗinta saman nipples ɗinsa ta lasa “Ahhhhhh!" Ya fitar da wani sauti me kashe jiki yana kai mata damƙa, da sauri ta zille tanayi masa dariya tace “Kaikam bazakayi wahalar faɗawa tarkon mata ba ku dubeshi yanda ya wani rikice Hero dubi dick ɗinka yanda take nish....."

Da gudu ta nufi hanyar ficewa Ƙara ta saki Ikcn da ya cafki gashinta yayo baya da ita ta faɗa ƙirjinsa yasa hannu da ya fito da boobs ɗin ta ya ɗora harshensa yana lasa ta saƙalo wuyansa yanashan nonon nata tana shafa twins ɗinsa zuwa joystick ɗinsa.

Da wannan suka kashe glub suka dulmiya duniya me faɗi ta ma'aurata wacce batada na biyu, tabbas an bawa soyayya haƙƙinta a wannan daren Habeeb jin Beebansa yakeyi har tafi masa kowanne lokaci koda yake ba ƙaramin gyara tasha ba Kilishi ta kashe kudi wajen shiryata tunda dama ita baayi mata na aure ba sanda ya kamata ayi mata ɗin ciki yayi shigar sauri.

Wannan rana Beebah tasha ruwan albarka ƙin barinsa tayi ya kwanta Saida sukayi wanka sannan suka kwanta.

Kwana biyun da yayi mata kamar zasu haɗiye juna saboda so ƙauna da kuma kulawa, ranar da yabar ɗakinta ya koma ɗakin Khausar duk sai ta rinƙa jinta kamar mara lafiya to shima a ɓangarensa haka abin yake kwana yayi da kewarta ga wani filling da yake damunsa amma baitaɓa sha'awar kasancewa da Khausar ba.

Haka akaci gaba da tafiyar da rayuwa a gidan Prince Habeeb abin come gaba come baya lamarin Khausar yana mugun ɗaurewa Beebah kai indai Habeeb na gida to tana maƙale da Hudais idan kuwa ya fice ko a hannunta yake ajiyeshi zatayi haka yaron zaiyita kuka saidai idan Beebah taji tasa Baba Larai taje ta dauko mata shi.

Wata rana bata mantawa rana ta farko da suka fara samun saɓani me tsayi dashi tun safe ta tashi da ciwon kai hakanan dai ta daure tayi ayyukanta Baba Larai tayima Hudais wanka ta goyashi yanata bacci a bayanta.

Itama sanin ba ita keda alhakin kula dashi ba yasa ta koma ta kwanta bacci me daɗi ya ɗauke ta batasan meye ya faru ba tajiyo hargowarsa a parlourn yana ƙwala mata kira ta tashi zumbur ta fito tana mayen bacci ta nufo parlourn ta tarar dashi tsaye yanata huci.

Bata kawo komai ba ta matsa gabansa tace “Gani Hero....." Kalmar ce ta maƙale Ikcn da taga wasu tartsatsin taurari a cikin ƙwayar idanunta, Saida ta kifa saboda shigar da marin yayi mata takai dubanta inda taga yana duba ta kuwa miƙe da sauri tana dubansa tana duban gurin tace “Meye ya kawo kaskon shisher da kwalin sigari parlour na Hero dama kana....."

Sake kaiwa bakinta naushi yayi daya sabbaba mawa bakinta fashewa ya nuna ta da yatsansa ya fara magana cikin yanayi me nuna tsantsar tashin hankalinsa da matsanancin fushin da yake ciki yace “Ashe haka kika zama Habeebah yaushe! Yaushe hakan ta fara faruwa bansani ba? Yaushe nayi saken da har kika lalace haka batare dana farga ba Habeebah garin yaya meye yayima rayuwarki zafin da zaki ɗaukar wa kanki wannan matakin meye daɗi a shaye-shaye Beebah wannan itane sakayyar da zaki......."
Jikinta ne ya rinƙa rawa cikin mugun tashin hankali ta furta “innanillahi wa inna ilaihirraji'un" ya miƙe ya fice da sauri daga parlourn itakuwa kasa motsawa tayi daga gurin tsabar tashin hankali da kiɗima da wannan lamari me kamar mafarki. Zubewa tayi a gurin ta ɗora kanta saman kujera zuciyarta nayi mata suya so take hawaye ya zubo mata amma ya gagara zuba sai ƙuncin zuciya.

Baba Larai ce ta shigo parlourn ganin uwar ɗakin nata cikin wannan hali yasata matsawa gabanta da sauri tace “Ya subhanallahi Gimbiya ina abinda yake faruwa naga Yarima ya fita cikin tashin hankali kedin da nazo jin baasi a gurinki kema na tarar dake cikin halin da yafi nasa meye ne yake wakana?"
Cikin rawar murya ta ɗago idanunta da suka kaɗa sukayi jawur tace “Baba Larai wai dama ina shaye-shaye?" Wani kallo Larai tabita dashi na ko kin zauce ne kafin takai ga magana ta riƙo hannunta wani kuka me ciwo ya ƙwace mata tace “Don Allah Baba Larai kar kice banayi ki tabbatarwa da Hero na inayin shaye-shaye Ni nakasa tantancewa nice ko photo copy na ne Larai na kasa ganewa meye yake faruwa da Hero ya amincewa zuciyarsa niɗin ƴar maye ce, yaushe na fara shaye-shaye yaushe na zama hakan?....."

Rufe mata baki Baba Larai tayi cikin kaɗuwa da jin kalamanta tace “Shi Yariman ne yace Miki kina shaye-shaye?" Girgiza kai tayi tace “Ba cemin yayi ba kamani yayi dumu-dumu...." Zaro idanu Baba Larai tayi tace kina shaye-shayen?" Cikin kuka tace “Eh.... Eh Baba Larai kusan hakan ne ki duba gabas dake duk wani nau'i na abinda mata ke amfani dashi na shaye-shaye gashi can a ajiye to waye ya ajiye idan bani ba?"

Shiru ce ta gauraye ɗakin babu abinda kakeji sai sautin kukan Beebah Baba Larai na share mata hawayen, daƙyar Baba Larai ta aro juriya tace “Wannan abin shiryayye ne akayisa don asa kokwanto a cikin yardar dake tsakaninki da mijinki kiyi hƙr ki ƙara haƙuri insha Allahu wannan makircin bazaije ko inaba Gimbiya Yarima yafi kowa sanin halinki idan yaje ya zauna ya samu nutsuwarsa ta dawo shi da kansa zai ƙaryata idanunsa da zuciyarsa amma fah sai kinyi

hƙr kin jure lamarin gdannan namu Gimbiya akwai makirci idan akaƙi mutum aka sakoshi a gaba ba dune yake kaiwa labari ba ke ki godewa Allah mijinki na sonki uwarsa na sonki bata karɓar suka kowacce iri ce indai akanki ne kai tsaye take cewa bazaki aikata ba"

Da wannan kalaman tayita rarrashinta har tasamu ta daina kukan ta tashi ta ɗebe kaskon shisher da kwalin sigarin ta bawa Baba Larai tace ta fice dasu daga sashin nata, har Baba Larai ta juya zata tafi ta juyo tace “Yarnan kiyi iya bakin ƙoƙarin ki kiga bakiba da ƙofar da za'a a gane da damuwa tsakaninki da mijinki ba kinji?"

Amsawa tayi da to Baba na gode Allah yabar ƙauna" ko bayan fitar Baba Larai ta daɗe a tsaye kafin ta shiga ɗakinta ta rubuta masa gajeren saƙo ta tura masa lokacin yana tare da Najeeb a gdansu yaji alamar shigowar saƙo Najeeb ya dubeshi yace “Waye?" Zaro wayar yayi daga aljihunsa ya buɗe saƙon murmushi ya dubi Najeeb yace.
“Bansan meye yasa muke kokawa da zuciyata wajen tabbatarwa kaina  Wyf bazata aikata ba amma wani sashi na zuciyata yana gargaɗina ɗan Adam a cikin sakanni yakan canza ɗabi'a"
Murmushi Najeeb yayi yace “Guy kana masifar son yarinyar nan kada kabawa munafukai dama su shiga tsakaninku kada fah ka manta akanta ka rantse zaka iyayin komai to meye ma idan tana smoking ɗin kawai hƙr zakayi kuci gaba da rayuwarku a haka....."

Miƙewa yayi yace “Koda Wyf na smoking zan iya rayuwa da ita badon abin ya girgiza ni Najeeb duk da nasani kaima baka goyon bayan aurena da Beebah ka faɗa min wannan shiri ne makirci ne haka Kilishi ma da na faɗa mata tace  min wannan ƙarya ne Habeebatullah bazata taɓa aikata barnar nan ba sannan ta kuma horona a karo na barkatai na ƙara sa ido a takun zaman gdana, Najeeb na yarda Beebahta bata shaye-shaye amma to meye yake sata bacci tunda na dawo kullum cikin bacci take?"

_Wannan Page Bonus ne bayanshi duk wani page da zaku gani paid ne kiji tsoron Allah ki biyani haƙƙina ki karanta cikin salama_
[5/17, 8:26 PM] AM OUM HAIRAN: _*BMGJY Bonus 41-42*_

_Ku biya ta acct detail  3184512451 First bank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241._
_Normal 300 PC 700_
_Ƴan Niger zaku biya 500f ta wannan number +227 95 04 58 22_

_Ban amince a juyamin littafi ta kowacce siga ba_

Assalamu alaikum My Fan's  shin ko kunsan cewa bigi sai bigi babban goro sai magogin ƙarfe,

tabbas ramin kura sai ƴaƴanta,
Nasan zakuce yau dame kuma Oum Hairan tazo mana? To ku daina tambayar kanku sabbi kuma shahararrun kayan mata ne masu ban mamaki daga taskar Siyat yar mutan Katsinawan dukko da Oum Hairan.
Muna da kayayyaki kamar haka👇🏼
Maganin gyaran Nono, maganin ƙarin hips, Sirrin matsi na musamman, gumbar dagake babu wata, humra mai taken madarar ƙauna, muna dafa kazar amarya da haɗin jijjiɓi musamman don masu jego tare da aikawa ko ina kuke a fadin Nigeria, munada maganin sanyi wanda duk shaharar sanyi muddin kikayi amfani dashi yanda ya dace to kin rabu dashi kenan.
Sannan munada kaloli na kayan Malama A'isha Mai Da'ira musamman turaruka wanda ke da kanki saikin dawo idan kikayi amfani dasu domin zasu janyo Miki hankalin mijinki zasu sanya nutsuwa da fahimtar juna tsakaninku zaki zama tauraruwarsa domin an haɗasu ne da wasu keɓantattun ayoyin Alkur'ani mai girma domin sharewa mata hawayensu babu boka babu Mallam, karki manta cikin kalolin turarukan mu akwai wanda Bama taɓa siyarwa me kishiya saboda haka kiji tsoron Allah in kinsan kina da kishiya karki siyeshi domin gudun shiga haƙƙinta.
Mai buƙata DM me 09013718241.

★★★~~~★★★~~~★★★

Miƙewa Najeeb yayi yana cewa “Kada kayi mata hukunci da baccinta waina watanka nawa da dawowa ne?" Baisan meye halaƙar tambayarsa da tambayar da Najeeb keyi masa ba amma haka yace masa biyu na shika na uku ina tunanin ma sati me zuwa zan koma" murmushi Najeeb yayi yace.

“Kuma sau nawa ka kusanceta daga dawowarka zuwa yanzun?" Kafe Najeeb yayi da ido Najeeb ya numfasa yace “Ta iya yiwuwa kaine matsalar ko Ikcn da kana London kullum maganarka kayi missing Beebah kayi missing Beebah ta yuwu ka sake jefa ƙwallo a raga ne tunda naga Khalisa tunda ta samu ciki batada aiki sai bacci ƙila itama nata ne yazo da haka...." Dariya Habeeb yayi yace “Da gaske zai iya zama hakan ko?" Ɗagansa kai yayi yace “Don tabbatarwa kana zuwa gida ka ɗauketa kuje a dubata hakan zai cire maka kokwanto"

Numfasawa yayi sukayi musabaha tare da sallama kowa ya kama gabansa zuciyar Habeeb ta kasa gasƙata masa abubuwan daya gani amma shaiɗan yanata taka rawarsa na son sai ya tabbatar masa.

Koda ya shiga gdan baiyi ƙasa a gwiwa ba ya nufi part ɗinta Khausar na ƙoƙarin ɗauke masa hankali da salon kirsarta ya watsa mata wani mugun kallo ya buɗe ƙofar ya fice ya nufi sashin Beebah tana zaune saman sallaya da alamun sallah ta idar Hudais na zaune a gabanta da kayan wasa yanata yan kararrakinsa kamar gyare inda ita kuma ta kifa kanta a cinyarta bacci na fusgatta taji an buɗe ƙofar ta ɗago idanunta cike da mayen bacci ta saukesu cikin nasa, shi ɗin ma itan yake kallo fuskarsa babu wani yanayi da zaka tantance walwala ko akasinta.

Haka ya tako ya zauna yana ɗaukar Hudais da ganin uban nasa yasashi sakin wasan da yakeyi ya fara miƙa masa hannu, lakacewa yaron kumatu yayi yana maida dubansa gareta yace “Meye yake damunki?" Yanayin yanda yayi tambayar yasa ta kasa gane me yake nufi sai kawai tayi ƙasa da kanta tace “Wallahi tallahi Hero ko maganin mura bantaɓa sha ba da niyyar ya fitar dani daga hayyaci na Please kada ka fara dasawa rayuwata kokwanto bayan Allah banda wani gata bayan...."

Rufe mata baki yayi yace “Ya isa nasani ina nufin game da lafiyarki kamar akwai wani abu dake damun jikinki ina ganinki saɓanin yanda nasanki" numfashi ta sauke tace “Ni babu abinda yake damuna yanzu ɗazun ne ma kafin shigowarka ta farko kaina yayi ciwo shine naje na kwanta bacci ya ɗaukeni" Jinjina kai yayi yace “tashi ki rakani unguwa" da sauri ta dubesa ya ɗaganta gira ta sani yanda ya haɗe yaci ganye ta tabbata babu kalmar data isa ta furta masa da zai saurareta hakanne yasata miƙewa ya ɗauki Hudais suka fita.
A babban parlourn suka wucce Khausar itace tayi mata sannu bata samu damar amsawa ba saboda wani malolon baƙin kishi da takaici dayake neman kassara mata zuciya, har suka shiga Mota suka tayar tanata takaicinta.

Jifa tayi da glass na cup na hannunta ta cire ɗankwalinta ta jefar ta nufi ɗakinta kamar sabon kamun hauka ta ɗauki wayarta ta kira lambar Deedah tana ɗagawa tace “Saida nace Miki mu canza salo wannan bazai yiwu ba kikace zai yuwu to yanzu me gari ya waya mun haɗa makircin ƙarshe gashi can ya ɗauke ta da ɗanta sun fice nikam hƙr na ya ƙare a gdannan babban burina ko zan rasa inga na rabashi da wannan ƴar Iskar Yarinyar wlh indai tana rayuwa a da'irarsa bazai taɓa kallon wata mace ba"
Tsaki Deedah tayi tace “Nifa wlh da kinbi shawarata ta da tuni tabar mana gdannan amma kika tsaya kina cewa wai kinfiso kibi komai a sannu to ai ga sannun nan kina gani mijinki kusan shekara da watanni ya gagareki saidai kiji dariyarsa a makotan...."

Cigaba sukayi da tattaunawa can sukayi sallama Deedah tace zasusan yanda zasuyi, itakam Khausar bata yarda da shawarar Deedah ba ta kira Hajiyan ƙofa bugu ɗaya ta ɗaga tace “Hajiya nifa lamarin nan ya fara isata wlh idan bata barshi ba ni zan barshi Mama tace mu shigar da boka na bakin kogi maganar ke kince a'a kuma alamu sun nuna itama hanyar da kikace kar mubi ita yakebi.
Yanzu ace duk kyauna da ƙirata bantaɓa burge Prince ba indai ba aikin asiri ba, haba Hajiya a

duba wannan lamarin fah mazan titi ma haɗiyar yawu sukeyi idan sun ganni sai mijina ne zaice banyi masa ba nikam na gaji wlh na gaji sha'awar Habeeb na neman kasheni"

Murmushi Hajiyan ƙofa tayi tace “Yaro yaro ne to ke banda abinki kina tunanin akwai asirin dayake cin waɗannan kafaffun mutanen ne? Haba Khausar kamar baa wannan ahlin aka tsirar dake ba ai in faɗa Miki indai jinin Khalil ne to ba asiri ba ko tsafi ne asarar kuɗinki kawai zakiyi basajin bayaƙi da kiranye, Khausar mantawa ma kikayi shekara nawa kikayi keda uwarki kuna badda kuɗi wajen ganin kun samu Habeebun amma yaƙi samuwa? To ki nutsu wannan aikin bana gaggawa bane akwai shirin da nakeyi duk zakujishi amma sai bayan Habeeb ya koma shine aikin zaifi tafiya yanda akeso ke nifa Khausar na daɗe da ƙayyadewa wannan bamagujiyar adadin kwanakinta a wannan gidan kedai kiyi duk me yuwuwa kiga kin cusa kokwanto a zuciyarsa kafin yabar ƙasar nan"

Kwantar da murya Khausar tayi tace “Kina gani fah nasa mata kaskon shisher da kwalin sigarin da kwalbar maganin mura har uku har buɗewa nayi na zubar a kan carpet ɗin Hajiya sigarin fah har kunnata nayi Saida ta ƙare na kashe kuma na zubar da tokar a Carpet ɗin amma hakan baisa yaji wani ɗar ba yanzu haka ma ya ɗauketa da ɗan su sun fice sun barni da gadin gida"
Murmushi Hajiyan ƙofa tayi tayi ƙasa da muryarta tace “zan rubuto miki mataki na gaba" saurin katse wayar tayi lokacin da taji an turo ƙofar, daga bakin kofar ya tsaya fuskarsa a washe kai bazakace ya taɓa shiga damuwa ba ya tsaya yana kallon Khausar taja numfashi tare da ƙoƙarin saita nutsuwarta don tasani karamin abu baya kawosa ɗakinta tace “Ina farin ciki da farin cikin me sani farin ciki halan anyi maka albishir da sarautar Dutse ne?"

Murmushi yayi ya kwantar da kansa jikin ƙofa yace “zan iya samu taimako daga gareki Wyf ce takeson wainar fulawa ta manja" murmushi tayi tace “to ai akwai komai a kitchen ɗin parlour tayi mana" murmushi yayi yace “batada Ify ashe duk wannan kasalar shigar ciki ke gareta...."
Da wani mugun sauri ta ɗago tace “Ciki kuma?" Annurin fuskarsa ne ya ɗauke ya zubanta manyan lulu eyes ɗinsa nandanan ta daburce tace “Nothing karka kawo komai a ranka kawai naga Hudais baifi five months ba.

Naji tsoffi suna cewa idan yaro yasha ciki lalacewa yakeyi...." Juyawa yayi ya fice yana cewa

babu abinda zai sameshi zan tafi dasu London a kula dasu acan ina jira ki kawo min wainar" da wannan ya fice ta zube a ƙasa ta ɗora hannu aka tana shirin rusa ihu tayi saurin toshe bakinta ta miƙe jiri na ɗibanta ta nufi kitchen ɗin parlour harta haɗa kayan wainar wata zuciyar ta hanata kawai tayi komawarta ɗaki.
Shima yana can yanata lelen matarsa ya manta da batun wata waina bai fito a ɗakin ba sai sha biyu da rabi sukayi sallama ya tafi ya kwanta.
Kacokan ya ɗauki kulawarsa da tattalinsa ya ɗorawa kanta ita da cikinta da ɗan su gefe kuma kullum sabbin abubuwa ɓullowa sukeyi zaman kullum ƙara rikicewa yakeyi Khausar ta dage kuma tana samun nasara donma ubangiji yana tare da me gaskiya a duk inda yake baya sanya makircinta yin dogon zango.

To yauma tun safe yayi asubancin tafiya Lagos zai karɓo saƙo dake tafiyarsa saura kwanaki uku, Beebah ke kwance a ɗaki ko parlourn ta kasa fitowa saboda zazzaɓi batasan wainar da ake toyawa a wajen ba sai yamma liƙis taji hargowar mutane a babban parlourn, zuciyarta bata bata taje taga su waye ba tunaninta mutanen Khausar ne.
A hankali taji hayaniyar na matsota ta tashi da sauri dake kwance take daga ita sai under sikert ta ɗauki hijjab batakai da sawa ba aka buɗe ƙofar aka shigo babu zato babu tsammani taji wani ƙato da aka cukuikuyo yana cewa “Hajiya ki taimakeni kice su sakeni wlh ba halina bane kece kika takura sai na zo Hajiya idan suka kasheni ya Iyata zatayi Ni kaɗai ta haifa saboda lafiyarta na yarda da sharaɗin da kika gindaya min na zuwa yau mijinki bayanan......"

Bata gane komai cikin maganganun da Saurayin yakeyi ba saidai bin waɗanda suke zagaye dashi da kallo da takeyi Mai Martaba Alh Lukman Mahaifin Khausar Hajiyan ƙofa Hajiyan soro da Jakadiya sai Baba Larai da keta sharar hawaye da Hudais a bayanta sai Hajiya mandiya Khausar da keta taunar cingam.
Cikin rawar murya Beebah tace “Wai meke faruwa ne? Waye kai?" Wata shaƙa Mai Martaba yayi mata data sanya numfashinta ɗauke wa yayi watsi da ita a gefe cikin ƙunar zuciya yace “Shiyasa tun farko naki amincewa Habeeb auren wannan bamagujiyar yarinyar saboda duk yanda kakai ga son kaga sunyi daidai bazasuyi maka daidai ba domin basu gaji daidai ɗin ba mutanen da suke bautar gumaka da duwatsu ace sune zaka zaɓawa ƴaƴanka matsayin uwa? Tur da wannan zaɓin wannan zaɓen tumun dare ne....."
Hajiyan soro ce tace “Allah ya taimake ka duk da ance ba'a shaidar mutum amma fah komai yakan nuna alama Habeebatullah batayi kama da wacce zata aika....."

Tsawa ya buga mata ya nuna ta da yatsa yace “Dake da Ummusalma bakinku ɗaya kuna goyan bayan rashin gaskiya to bari kiji Wlh tallahi na rantse da girman Allah yau yarinyar nan sai tabar cikin ahlina Ni a matsayina na uban daya haifi Habeeb na sawwake mata aurensa kuma mun

karɓi Ibrahim ta fito ta fice min daga gidan ɗana kafin nasa a fitar da ita.........

_Ku ƙara yimin uzuri my lovely Fan's aradun Allah duk inda nayi kuna raina koda yake nasani soyayyarku da wannan labari me farin jini ke gajarce uzurinku gareni, wlh tun jiya nayi muku typing kamar yanda na alƙawarta wani uzurin yazo yasha kaina.🤗_

_Wannan Page Bonus ne bayanshi duk wani page da zaku gani paid ne kiji tsoron Allah ki biyani haƙƙina ki karanta cikin salama_
[5/18, 8:31 PM] AM OUM HAIRAN: _*BMGJY Bonus 43-44*_

_Ku biya ta acct detail  3184512451 First bank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241._
_Normal 300 PC 700_
_Yan Niger zaku biya 500f ta wannan number +227 95 04 58 22_

_Ban amince a juyamin littafi ta kowacce siga ba_

Cikin ƙunan zuciya ɓarin jiki da tashin hankali ta miƙe tsaye idanunta na ganin duhu ta nufi wardrobe domin ɗauko kayanta tasa Hajiyan ƙofa tace “Matsiyaciya ubanme kikazo dashi da zaki ɗauka? Ina haka akazo dake a cikin tsumma zaki wani buɗe wardrobe kinga maza zo kama hanya kafin dare yayi Miki" lumshe idanunta tayi ta juyo ta dubesu ta girgiza kai zuwa yanzu furucinta ya ƙare batada wata kalma da zata iya furtawa domin kare kanta tabbas komai nisan gona dole zaaje kunyar ƙarshe wannan shine dalili na farko da yasa taji a ranta zata iya rabuwa da Habeeb rabuwa ta har abada.
Ƙofa ta nufa tana shirin fita ta juyo ta dubi Hudais dake bayan Baba Larai kawai sai taji wani kuka ya ƙwace mata ta matsa takai hannu zata kwanceshi, Baba Larai batayi mata gardama ba ta kwanto mata shi Hajiyan ƙofa tayi saurin karɓeshi tana cewa “Allah ya kiyaye ya ƙara raɓar jikin wannan annamimiyar matar maci amanar ƙauna kekam kin cika butulu....." Wani kallo tabi Hajiyan ƙofa dashi ta juya ta fice da sauri Hajiyan soro na ƙwala mata kira amma bata juyo ba saboda Zuciyarta ta riga ta gama ƙeƙashewa batajin daidai da second ɗaya zata iya ƙarawa cikin wannan ahlin gara ta fita kamar yanda suka shirya tozartata dayi mata ƙazafi.

Abin takaici da mamaki wai maigadin da komai a gidan ita keyi masa shine ne cewa da ita "Ummah tagai da Assha" wai harda cewa yake "aje aci gaba da tallan Burkutu....." Ko tana cikin hayyaci itan ba ma'abociyar kula kowanne shirme bace bare yanzu da takejin jiri na ɗaukar ta bata iya gane komai kawai daɓa ƙafarta takeyi ko ina.
Batayi aune ba batasan meye ke faruwa ba kawai saiji buɗe idanu tayi taganta a gadon asibiti hannunta da ƙafarta nannaɗe da bandeji, ta rinƙa raba idanu tana kallon asibiti da wani irin yanayi na rashin tabbaci.

Ji tayi ance mata "sannu!" Ta karkata akalar idanunta kan wanda ke mgnr cikin yanayi na rashin madafa ta zubansa idanu tanason tuno inda ta sanshi shi ta kasa tunawa ganin yana nufota yasata janye injin idanunta daga kansa ta zubawa selling idanu, hakan ya bashi damar matsowa har inda take ya zubanta idanu a hankali yace "inane yanzun keyi Miki ciwo?"
Shiru tayi masa brain nata na tariyo mata dalilin faɗawarta wannan halin ta yunƙura zata tashi da sauri mutumin ya riƙe ta tare da ƙwalawa wata nurse kira suka taimaka mata ta tashi zaune ta dubesu cikin rashin hayyaci tace "kwanana nawa anan?" Kallon juna sukayi namijin yace "biyu" cikin tashin hankali tace "Na shiga uku ɗana Hudais ina yake a wanne hali yake yanzun?" Babu me amsar wannan tambaya tata domin basusan komai game da itaba har gara ma Dr Amin shi yanayiwa yanayinta kallon sani amma ya rasa gane inda yasanta, kalmar ta ɗaya ta sanyashi jin wata faɗuwar gaba ta ɗarsar masa.

Hawaye ne ya rinƙa zubo mata wani na bin wani ta ɗago cikin kuka mara sauti tace "Don Allah ku taimaka min ku faɗamin halin da Hudais yake ciki inajin tsoron kada wani abu ya sameshi gashi mahaifinsa baya gari...."
Dafa gefen gadon Dr Amin yayi yace "Kiyi hƙr kinga yanzu bakida lfy ƙafarki akwai ciwo sakamakon accident ɗin da kika samu kuma abinda ke cikinki yana samun barazanar zubewa idan kika cika takurawa da tunani komai zai iya faruwa" batace masa komai ba kuma bata daina kukan da takeyi ba ta kwantar da kanta a cikin cinyarta can ta ɗago tace "Wai nan ɗin wanne gari ne?" Nurse Zainab ce tace "Kina ne Abuja ko kinsan wani anan?" Da mugun sauri ta dago tace meye ya kawoni Abuja....." Maganar ce ta shaƙeta saboda irin kallon da Dr Amin yake yi mata ta kawar da kai ta fara ƙosawa da wannan mugun kallon nashi da ta rasa dalilinsa.

Kwanciyarta Nurse Zainab ta taimaka mata ta gyara Dr ya fita yana cewa Zainab a bata kulawa zanje gda na ɗan huta idan na dawo za'a kwance wannan bandejin aci gaba da treatment din ƙafar a kula sosai" jinjina masa tayi ya dubi Beebah yace "Madam ko kina bukatar a taho Miki

da wani abu?" Baisamu arzikin ko daga hannu ba hakan ya tabbatar masa wannan duk inda ta fito miskilar gaske ce bai takura kansa da son sai yaji daga gareta ba ya juya ya fice yanajin wani irin yanayi me nauyi game da ita a zuciyarsa saidai shi da kansa gargaɗin kansa yake yi domin yanayi ya nuna itan matar wani ce ko kuma sakin wani ce.
Da wannan mutuwar jikin ya isa gdansa ya buɗe ya shiga yayi parking ya fito ya nufi kofar da zata sadashi da asalin cikin parlourn gidan ya buɗe ya shiga babu kowa a parlourn don haka kai tsaye ya nufi sama acan ya jiyo hayaniyar yaran ya isa ya bude dakin nasu sunata wasansu suna ganinsa sukayo kansa suna “Oyoyo Dad"  kama hannunsu yayi yana musu yar gajerar dariya yace “Ina Mom ɗinku?" Karamin ne ya karyar dakai yace “Yau Mom hutu takeji tace kada mu dameta" yasan ƙiriniyarsu shiyasa ya saki hannunsu yace “Ok kuje kuyi alwala bari nayi wanka nazo muyi jam'in sallar Azahar" shigewa ciki yaran maza guda biyu sukayi da gudu yayi murmushi ya nufi ɗakin uwargidan nasa ya buɗe tana kwance a gado tana latsa waya tana ganinsa ta tashi tanayi masa murmushi ta tarosa tayi hugging nasa tare da kissing ƙirjinsa tace “your are welcome my jannati" shafa kanta yayi yace “Welcome sweeter ya fama da ƙiriniyar yara?"

Rausayar dakai tayi tace “Sun dameni habeebty shiyasa nace suje suyi playing games su barni na huta" Safeenah kenan macen gaske ta samu lambar yabo wajen iya kula da miji matsalarta ɗaya baƙin kishi ko kaɗan bata ƙaunar taga wata mace ta raɓi mijinta wannan yasa bata ƙaunar duk wani abu da zaisa mijinta yaji a ransa ta cancanci yayi mata kishiya, ta gwammace ko zatasha wahala itadai tasha indai zata rayu da Dr Amin ɗin ta ita kaɗai, wannan kenan.
Jansa tayi har bathroom sukayi wanka suka fito yaje sukayi sallah su da yaransu sannan suka zauna cin abinci sunacin abincin zuciyarsa na gurin petiant ɗinsa yarinyar ta tsaye masa a rai, yanason jin dalilin barowarta gda shikam yanayinta yana nuna masa duk inda ta fito babban gidane batayi masa kama da matar yara ba.
To yau ɗin ma bai iya bawa Safeenah labarin petiant din tasa da baisan sunanta ba sai ita ce tace “Nikam Sweeter ya labarin yarinyar da kace tsautsayi yasa ka bigeta a Kano Amma ka kawota asibitinka saboda ka bata kulawa?" Numfashi ya sauke yace “har yanzu babu wani labari game da itan saidai yanayi yana nuna itaɗin matar wani ce Inma mutuwar aure tasa ta baro gidanta ko kuma wata babbar damuwa to koma dai menene inason ta kara samun sauƙi sai muyi magana a nutse"
Jinjina kai tayi tare da cewa “To Allah yasa muji alkhairi" amsawa yayi da Amin ya miƙe yace “inajin bacci zanje na ɗan kwanta hudu ki tasheni" itama miƙewa tayi suka tafi ɗakin tare suka kwanta suna ƴar hirarsu ta ma'aurata har bacci ya ɗauke su.

***********

Kwanan Habeeb ɗaya a Lagos hankalinsa ya dawo gida saboda yinin da yayi yana kiran wayar

Beebah tana ring amma ba'a ɗagawa, gashi duk wani wanda zai samu bayani ta gurinsa ya kira wanda ya ɗaga ne zaice masa kawai ya dawo gida babu lafiya wasu kuwa basa ɗagawa, lkcn da Najeeb da Hajiya Kilishi suka sanar dashi gidan babu lafiya dare yayi nisa don a kallah lokacin sha biyu ta wucce.
Dole tasa ya kwanan zaune sai wajen asuba ya samu bacci barawo ya ɗauke shi aikam babu shiri ya tashi saboda ko a mafarkin baiga alkhairi ba karfe takwas jirginsa ya daga sai Birnin Dutse yayi saa kuwa Najeeb na jiransa kai tsaye gdansa ya nufa dashi cike da tausayin halin da aminin nasa zai zama a ciki, shidai ya hakikance duk wannan abun da akace ya faru koda Habeeb kamawa yayi da idanunsa yanda yakeson yarinyar nan bazai taɓa yanke hukuncin da Mai Martaba ya yanke wa auren su ba.
Tun daga babban parlourn ya fara fuskantar tabbas gidan ba lafiya lau yake ba domin kuwa babu wata alama da take nuna an gyara shi yau, haka ya kutsa sashin Beebah yana ƙwala mata kira amma shiru yanda yaga ɗakin a hargitse kayanta duk a baje a kasa yasa gabansa faɗuwa ya juya ga Najeeb yace “Batada lafiya ne?"

Sunkuyar dakai Najeeb yayi ya riƙe kafaɗarsa da ƙarfi ya jijjigashi yace “Ka sanar dani meye ya faru da Wyf bayan tafiyata?" Janyewa yayi yace “kazo muje cikin gida zakaji komai" to dake neman bayani yakeyi baiyi musu ba yace “nasan ma bazai wucce suna can ba" da wannan suka fita suka nufi gidan sarautar suna zuwa ya fita a motar ko parking Najeeb bai gama yi ba ya shige ciki yana ƙwalawa Kilishi kira, tana ɗakinta tanaba Hudais madara taji kiran nasa gabanta ya yanke ya faɗi tasan yau hauka ne a gidan harsai anyi kamar ayi masa turu.
Miƙewa tayi ta fita yana ganin Hudais a hannunta yace “Ina Wyf ɗin take Kilishi jikin nata ne ya matsa ne?" Sunkuyar dakai tayi hawaye ya zubo mata tace “Tabbas Habeebu Wlh tallahi Habeebatullah bata cikin mutane masu dauɗa da zunubin zina amma kash abin tur da Allah wadarai anyi amfani da wani saurayi da kuma shaidar da maigadin gdanka ya bayar an kitsawa Mai Martaba ƙarya da gaskiya akan cewa tun lkcn daka tafi London Beebah ke kawo maza gidanka sai jiya asirinta ya tonu Habeeb Mai Martaba yayima Beebah korar kare tare da aron bakinka ya datse igiyoyin auren dake tsakaninku, bayan haka kuma ya karɓe Ibrahim daga gareta, wlh tun jiyan da abin ya faru na baza mutane su lalubomin ita don na hakikance wannan ƙazafi ne ƙage ne..........
[5/19, 7:59 PM] AM OUM HAIRAN: _*BMGJY Bonus 45-46*_

_Ku biya ta acct detail 3184512451 First bank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241._
_Normal 300 PC 700_
_Yan Niger zaku biya 500f ta wannan number +227 95 04 58 22_

_Ban amince a juyamin littafi ta kowacce siga ba_

Tunda Kilishi ta fara mgnr jikin Habeeb ya ɗauki wata rawa ya miƙe tsaye da nufin ya fice jiri ya fara ɗaukarsa dole ya koma ya zauna yana tare da dafe kansa dake sara masa da ƙarfi jikinsa na ƙara ɗaukar tsuma ya furta “Innanillahi wa inna ilaihirraji'un Allahumma ajirni fih musibati wa'akalifni khairin minha" yayi wannan furuci yafi sau ashirin kafin ya aro juriya ya dago idanunsa da suka kaɗa sukayi jawur ya zubasu akan Kilishi yace “Yanzu ina ta tafi?" Cikin sarewar murya Kilishi tace “Inda nasan inda ta tafi da bazakaji meye ma ya faru ba Habeeb" Sake dafe kansa yayi yana ayyana abubuwa da yawa tabbas ya tabbata wannan tsabar sharrine da makirci aka ƙullawa Habeebah ko kaɗan baiga laifinta ba domin Hausawa sunce in wani yaƙika da yini wani da shekara yake neman ka kuma ƙasar Allah me yalwa ce in aka ƙyamace ka anan idan kayi gaba murna za'ayi dakai, Amma shima Yakamata kafin ta tafi ta dubashi meye ma yasa bata kirashi ba ya nema masu mafita domin ya haƙiƙance ko Shari'a bata isa rabashi da matarsa ba matuƙar yana numfashi a doran duniya bare kuma ma akan karya da son zuciya.

Miƙewa yayi ya nufi ƙofar fita yana haɗa hanya kamar ɗan ƙwaya sukaci karo da Mai Martaba a hanya ko kallonsa baiyi ba yayi gaba abinsa Najeeb yace “Habeeb Mai Martaba na magana" batare daya juyo ba yace “Me zanyi masa to son rayuwata yakeyi da zaimin magana ya barni na mutu ma mana tunda burinsa kenan.
Yana faɗin haka yana shiga Mota dake Najeeb bai cire key ɗin ba ya kunna ta da mugun gudu ya fice daga gidan sarautar yanda yake tuƙin ya tsorata kowa don tabbas ba cikin hayyaci yake ba.
Shikuwa kamar yanda zuciyarsa ke gudu wajen ganin ya isa inda zaiga Beebah haka yake keta mugun gudu a hanyar ya nufi ƙauyen su Beebah karo na biyu tun bayan aurensu da yazo ƙauyen ya tsaya yana ƙare wa gdansu Beebah kallo yasha gyara kamar baa ƙauye ba yananan tsaye Baba Jimo ya fito ya tsaya turus ganin Habeeb ɗin a tsaye jikin mota.
Cikin hassalar bala'i ya nufoshi yana nunashi da yatsa yace “Wato kai kunnen ƙashi ne dakai ko nace karka ƙara takowa gareni shine ka sake dawowa halan ajali ne ke ɗawainiya dakai....."

Cikin karayar zuciya Habeeb yayi ƙasa hawaye ya zubo masa yace “Wlh Baba ba laifina bane ko a mafarki bantaɓa jin a raina akwai ranar da zan iya rabuwa da Beebah ba Bana Beebah rayuwata ce ka taimakeni ka bani matata......
Kallon bakada hankali ya rinƙa bin Habeeb dashi can yace “Kai yaro fice cikin ƙwayar idanuna kaga nayi kala da wasanka? Zakazo kana cewa na baka matarka wacce matar ke

gareka a gurina?" Miƙewa Habeeb yayi cikin nunkuwar tashin hankali yace “Wai Beebah banan tazo ba Baba?" Duk da Baba Jimo yana cikin halin tsananin fushi Saida gabansa ya faɗi yace “batazo ba ina tayi cemaka tayi zatazo nan?"
Hannu Habeeb ya zuba a kansa yace “Na shiga uku Ni Habibu Habeebah ina kike....."

Cakumarsa Baba Jimo yayi yace “Na rantse da abar dogarona kamar yanda ka ɓatar min da Bibo kaima labarinka saiya shafe saina ɓatar dakai...." Shi baima damu da riƙon da yayi masa ba hawaye kawai yake shara yana cewa “Mai Martaba ka cuceni ka wargatsamin gda ka tafi da farin cikina, yanzu ina Beebah tashiga ita ba cikakkiyar lafiya ba?"
Fir Baba Jimo yaki sakin Habeeb kawai sai huci yakeyi yau ga ranar yayansa Uda gashi mutuwa tayi gaggawa, daƙyar mutane suka raba hannun Baba Jimo da kwalar rigar Habeeb rigima ta sarƙe shi Habeeb na roƙonsa ya bashi matarsa idan yasan tazo shi kuma yana rantsuwar saiya fito masa da yarsa rigima har gidan Dagaci koda Dagaci yaji abinda ke faruwa a bakin Habeeb hankalinsa yayi mugun tashi shima tabbas abin akwai tashin hankali gashi babbar damuwar baasan inda za'a nemi Beebah ba.
Duk yanda Dagaci yaso Baba Jimo yabar Habeeb ya tafi yaji da damuwarsa hanawa yayi Saida Dagacin yasa aka kira irin bokayensu na tsubbu suka tabbatarwa da Jimo Habeebah tananan cikin aminci kuma zata dawo saidai basusan inda take ba, to sannan ne fah hankalinsa ya kwanta yabar Habeeb ya tafi amma da sharaɗin duk inda Habeebah take ya nemo masa ita tunda ubansa bayason zamansa da ita to ta gama aurensa har abada.
Shidai bai bawa mgnrsu muhimmanci ba burinsa kawai sanin inda Beebah take, hakanan ya ɗauki hanyar Dutse ikon Allah ne kawai ya kaisa gida kai tsaye ɓangaren Khausar ya shiga ya tarar da ita taci wanka sai faman taunar cingam takeyi kamar karuwa.

Babu furuci ba komai ya ajiye mata takarda a cinyarta ya fice daga ɗakin da sauri ya nufi ɗakin Beebah ya faɗa gadonta yaja rigarta ya rungume a ƙirjinsa numfashinsa na ɗaukewa yana janyoshi da ƙyar yanda zuciyarsa ke masa zafi a yanzu
Haka baya buƙatar kowa a tare dashi ji yake yi ma kamar ya tashi yabar garin, zuciyace ta bashi shawarar dole ma ya bar garin da daren ya tattare komansa washegari daga masallaci ya ɗauki mota sai Abuja Saida ya shiga cikin garin Abuja ya kira babban amininsa da sukayi karatu dashi a Oxford cikin murna engineer Wali yazo ya taroshi daga yanayi ya fahimci Habeeb na cikin damuwa haka dai suka ƙarasa gdansa zama Habeeb yayi ya dafe kansa da yakeyi masa wani mugun ciwo, dafashi Wali yayi yace “Nayi mamakin ziyararka ta bazata haka duk da dai yanayinka ya nunamin baka cikin nutsuwa shin ko zan iya sanin meye ke faruwa?"
Iska ya furzar ya miƙe ya nufi wani ɗaki ya buɗe ya shiga bathroom ya watsa ruwa yana fitowa ya kwanta zazzaɓi na sauko masa me zafi.

Shigowar Wali ce ta sashi sake jan bargo Wali ya janye yace “wai meye yake faruwa ne Habeeb ina matanka ko wani abu ya faru ne?"
Numfashi ya sauke me huci yace “Ka kiramin likita" baiyi masa jayayya ba ya dauki wayarsa ya latsa wayar cousins dinsa Dr Al'Amin yayi masa bayani yace masa ok yanzun yanakan wata petiant ne amma yana gamawa zaizo. Haka sukayi sallama ya aje wayar sukaci gaba da zaman kurame Wali ya gaji yace “Don Allah ka faɗamin meke faruwa ina Hudais da mamansa?"
Zubawa Wali ido yayi can yace “Bansan inda Habeebah take ba tafiyar da nace maka nayi zuwa Lagos wasu abubuwa suka faru har yasanya Mai Martaba yanke hukuncin sakarmin mata da bakinsa bada nawa ba kuma ya ƙwace mata ɗanta ɗaya data ɗauki so ƙauna da burin duniya ta ɗora masa ɗan da takejin zata iya rabuwa da komai dominsa Zubair Habeebah na sona amma na tabbatar da a yanda take da haƙuri da kawaici kuma a lkc guda idan hƙrnta ya kare take da kafiya Wallahi ba zata nemeni ba koda kuwa sona zai zama silar yankewar numfashinta, meye yasa Mai Martaba zai rabani da zuciyata Zubairu Habeebah rayuwata ce inajin yanda zuciyata take zafi da zugin ciwo tsaf zata iya daina aiki indai babu Wyf a kusa dani Wanne taimako zaka bani ta dawo gareni Zubair don Allah Please help me....."
[5/20, 9:07 PM] AM OUM HAIRAN: _*BMGJY Bonus 47-48*_

_Ku biya ta acct detail 3184512451 First bank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241._
_Normal 300 PC 700_
_Yan Niger zaku biya 500f ta wannan number +227 95 04 58 22_

_Ban amince a juyamin littafi ta kowacce siga ba_

Jinjina kai da girman lamarin Engineer Wali yaci gaba da yi can Habeeb yace “kasa na faɗa maka damuwata kuma kayimin shiru Shikenan tunda bakada abin faɗa kaje kaima kubarni na mutun in hankalinku zai kwanta...." Katseshi Wali yayi yace “Not ka gane Friend ina tunanin rayuwa irin taku ta gidan sarauta meyesa bakuson bare a cikinku ne meye yasa kuke yanke hukunci da son rai Wallahi duk da cewa bantaɓa ganin Maman Hudais ba amma zuciyata bata amince zata aikata wannan abinda akace ta aikata ba haba shi Mai Martaba hankalinsa ne ya gushe ko kuwa rufa ido akayi masa yarinyar da batasan kowa ba sai kai da Ahlinka yarinyar da kai da kanka Saida kukasha ƙwarbai kafin ta amince dakai har ku fara gudanar da Sunnah da ita yarinyar da kowa ya sani ko ƙawa bata taɓayi ba sannan batada fitina kullum cikin nutsattsen yanayi take Habeeb wato kayi gaggawa daka datse igiyar aurenka dake kan ƙanwarka Khausar inada yaƙinin ita tasan komai kuma bazai wucce shiri da tuggunsu ba"

Numfashi ya sauke yaci gaba da cewa “Kai akaso a dasawa kokwanto tsana da ƙyamar Maman Hudais sai aka ga wannan bazai yiwu ba domin bakai ka dasawa kanka yarda da soyayyarta ba shine aka juya lamarin kan Mai Martaba ta yanda zaka tabbatar da abin shiri ne

Meye ya kawo Mai Martaba gidanka a wannan lokacin kuma meye yasa ba'a bari anji abinda ita Beeban zatace ba sannan meye yasa ba'a kiraka ba domin sanar dakai a daidai lokacin? To duk waɗannan abubuwan abin dubawa ne amma bamu da lokacin dubasu kawai ta ina kake tunanin zamu fara neman yarinyar nan?"
Taɓa ƙofar akayi hakan ya dakatar da hirar tasu Engineer Wali ya tashi ya buɗewa Dr Al'Amin ya shigo yana duban Habeeb sukayi musabaha ya dubi Wali yace “Bro wake ba lafiya?" Kallon Habeeb Wali yayi yace “Gashinan abokina ne da nake baka labari munyi karatu a Oxford dashi ya fara karantar harkarku mahaifinsa Sarkin Dutse yasa ya juya zuwa ɓangaren mu kaganshi nan ciwon soyayya ne ke wahalar dashi ko kunada maganin matsalar?"
Murmushi Dr Amin yayi yace.

“Turƙashi lamari ya ɓaci kenan ciwon so akwai wahala Nima gashi ina neman faɗawa a karo na biyu duk da dai inata kwaɓar zuciyata kada ta shigar dani inda bazan fito ba" yana maganar yana gwada BP ɗinsa ya dubeshi da sauri yace “Ya Salam Engineer ka rage wannan damuwar kaga yanda BP naka yayi sama kuwa?
Gaskiya ka rage damuwar komai zai wucce insha Allahu girgiza kai yayi ya sharce hawayen dake ƙoƙarin zubo masa yace “Kayi aikinka kawai babu wani abu da zai iya rabani da wannan damuwar sai dalilinta" daga haka bai kuma cewa komai ba Dr Amin ya gama rubuce rubucensa ya bawa Wali ya juya yana cewa “Ka kula da kanka Please akwai yanayin hauhawar jinin da ka iya haifar da komai Allah ya shiga lamarin" amsawa Wali yayi suka fita tare har asibitin suka sayi maganin sannan ya juyo yana mamakin yanda yayan nasa bashi labarin yanda akayi ya sami petiant ɗin tasa da ya dauki kulawar duniya ya ɗorawa.

Komawa yayi tare da yima Habeeb bayanin magungunan ya karɓa ya zubesu Saida ya takura masa sannan yasha maganin yaci gaba da jinyar jikinsa tare da baza cigiyarta jaridu talabijin da rediyo duk da kasancewar Amin ɗan nacin karanta jaridu kwana biyun yanayin jikin Beebah da kuma rashin lokaci yasa baisan wainar da ake yi toyawa ba.
A haka Beebah Saida ta shafe kwanaki arba'in a asibitin tana jinyar ƙafarta sannan taji sauƙi

sosai lokacin kuma cikinta ya fara bayyana sosai abinka da itan ba doguwa bace sosai shi yasa cikinta baya ɓuya watanni biyar kowa na iya ganinsa, Dr Amin dakansa ya yankar mata katin files na awo a asibitin sai lokacin ne ya fara tunanin ta yanda zaijewa da Safeenah maganar, koda ya tunkareta tayi masifar bashi mamaki yanda ta nuna ai babu komi ya kawota su zauna har zuwa lokacin da zatayi bayanin daga inda take ita da kanta take cewa dashi yarinyar ta bata tausayi daga ganinta wartako akayi daga gidan mijinta kodai asiri ko kuma bakin ciki ya hanata faɗar daga nahiyar da take.

Yaji daɗi sosai a ranar kuwa Beebah ta dawo gidan da zama Safeenah nata bata kulawa musamman dataga cikinta ya fara tsufa haka tayita zolayarta hardai ta saki jiki sukaci gaba da rayuwarsu a gidan gwanin ban sha'awa babu hantara bare kyara duk da cewa zuciyar Beebah na gurin ɗanta da mijinta amma haka take daurewa saidai idan kewarsu ta dameta ta shige ɗaki tayi kukanta ta ƙoshi idan Safeenah ta ganta ta rinƙa bata hƙr daƙyar Safeenah ta samu Beebah ta bata labarin abinda ya fito da ita daga gidan mijinta sosai Safeenah ta kaɗu da jin wannan mugun makirci ta tausaya mata taso ta faɗawa Dr Amin amma fir Beebah taƙi barinta ta rinƙa roƙonta tabarshi batason komawa gidan Habeeb akanta abubuwa da dama sun faru dashi gashi har mahaifinsa yanajin ta cancanci ya ari bakinsa ya saketa.
Ajiyar zuciya Safeenah tayi tace “Shirme ne kawai da ɓacin rai ai Shari'a ce kawai take da ikon sakarwa mutum mata shima kuma sai idan ya amincewa hakan, Beebah har yanzu kinanan matsayin matar mijinki kawai dai basu iskar yanada amfani amma dai don Allah karki azabtar da bawan Allah ki daina cewa bazaki komawa aurensa ba yayi don ke basani kema kinyi dominsa kiyi hƙr ki bayyana masa inda kike ko ya samu sauƙin damuwa kada kiyi kisan rai"

Batajin wannan magiyar abubuwa da yawa suke sata ƙin saurarar Safeenah idan ta tuna ta rabu da komai saboda Habeeb ta rasa komai sabodashi ta zaɓeshi fiye da iyayen da suka kawota duniya tabarsu tabisa amma ta kasa samun mafaka a gurinsa ɗan da takejin shine raba gardamarta shima sun karɓe sun barta batada tsuntsu bare tarko.
Takanyi kukan nadama da tunanin ta yanda zata tunkari iyayenta.
Kwanaki sukayita tafiya cikinta na tsufa har ta shiga kwanakin haihuwarta kullum sai sun fita motsa jiki Allah kuwa ya kawo mata haihuwar da sauƙi a gida ta haifi yarinyarta mace cikin dare ita kaɗai a ɗaki.

Sai bayan haihuwar ta kira Safeenah ta sauko tazo taga abin mamaki ta koma da gudu ta taso Dr Amin dakansa ya gyara yarinyar suka gyara maijego Safeenah ƙin komawa saman tayi ta zauna a gurinsu.

Karon farko taji tanason sanar dashi abinda ya shafeshi wayarta ta dauka ta latso number sa ta rubuta masa gajeren saƙo kamar haka.
_“Inayiwa Mijina fatan alkhairi da nasara akan duk abinda yakeyi yanzu, ina mai farin cikin sanar dakai yau ajiyar ka ta fito mun samu ƙaruwar ƴa mace....."_
[5/24, 8:42 PM] AM OUM HAIRAN: _*BMGJY Bonus 49-50*_

_Ku biya ta acct detail 3184512451 First bank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241._
_Normal 300 PC 700_
_Ƴan Niger zaku biya 500f ta wannan number +227 95 04 58 22_

_Ban amince a juyamin littafi ta kowacce siga ba._

Tana gama rubutawa ta karanta tare da tura masa sannan tayi maza ta kashe layin.
Habeeb dake kwance saman kujera three sistar yaji shigowar saƙo kamar bazai buɗe ba ya gyara kwanciya, zuciyarsa taƙi nutsuwa ya ɗauki wayar ya buɗe saƙon baisan sanda ya tashi tsaye ba yana duba saƙon number babu suna ya sake duba saƙon yace “Habeebatullah kenan? Kece kika turomin saƙo?"
Da sauri ya fara kiran layin abin takaicin ta riga ta kasheshi wannan tasa shi zama daɓar tare da dafe kansa yana furta Innanillahi wa inna ilaihirraji'un sake gwada wayar yayi har zuwa lokacin a kashe ransa ne ya fara faɗa masa to ko ta koma Tsaunin gawo ne?
Da wannan tunanin ya tashi ya zari key na mota ya fice daga dakin komawa yayi ya zauna tare da duba agogo 3:20am yasani koda yake motar kansa ce ba ƙaramin ƙalubale zai fuskanta a garin Abuja kafin yace zaije Kano daga Kano ya ɗauke hanyar Tsaunin gawo kwanan zaune yayi asubar fari zakara ya bashi saa ya ɗauki hanya wajen goma ya isa Kano ya ɗauki hanyar Tsaunin gawo lokacin daya isa duk maza suna gona.

Jumme ya tarar tana shanyar ganyen albasa ya tsaida motarsa ya fito tana ganinsa ta nufi gida da sauri ya bita tare da cewa “Barka da safiya Mama!" Tsayawa tayi ya rusuna ya gaisheta, cike da kunya irin tasu ta mutanen karkara ta amsa ya sosa kansa yace “dama Habeebah nakeson gani...." Da sauri ta juyo tace “Tana ina ɗannan Nima ita nakeson gani"
Wani abu yaji me nauyi ya saukowa ƙirjinsa daƙyar ya miƙe tsaye ya koma cikin motarsa ya kira wani yaro ya zaro kuɗi da baisan adadin su ba ya bashi yace yakaiwa Jumme ya tada motar yabar ƙofar gidan baiyi nisa ba ya tsaya ya ɗora kansa bisa sitiyarin motarsa ya lumshe idonsa hawaye suka fara sintiri Mai Martaba ya cutar dashi duk shine yaja masa amma yanzun wai dashi yake fushi saboda ya sakar masa zaɓin nasa.

Ajiyar zuciya yayi tare da tada motar ya koma cikin garin Kano anan ya samu wani hotel ya sauka ya huta yana kwance wayar Wali ya shigo yana gani amma ya kasa ɗagawa saboda ransa a cushe yake kalma ko ɗaya bayajin zai iya furtawa me amfani.

Kira na biyu ne ya sashi ɗagawa Wali yace “nazo gdanka bakanan ina kaje?" Buɗe idanunsa yayi cikin gajiya yace “ina Kano" amsawa Wali yayi yace “Ok dama inason ka rakani gidan Al'Amin ne" a yatsine yace “
Ko kwanaki kace nazo muje nace maka banida interest akan hakan so waima meye Ni sai ka rinƙa jana gidan matan aure?" Murmushi Wali yayi ya riga yasan halin izza da son isa irin ta Habeeb shiyasa yace “Allah ya huci zuciya dama Ahmad abokinka ne ya dameni tun jiya nazo naga bbynsu ƙanwar Mamansu ce dake zaune a gidan ta haihu shine dake naji kace kanason zuwa ka gaisa da Ahmad na sanar dakai"
Numfashi ya aje yace “ok kaje inna dawo ka rakani tunda Ni yanzun saina shiga Dutse zan wutto nan" sallamewa sukayi ya tashi ya fara shirinsa ya ɗauki mota sai dutse koda yaje bai saurari mai martaba ba sashin Kilishi ya shiga suka gaisa cikin watanni biyar ɗin duk ya rame ya susuce sai ido da hanci kawai taja fasali tace “Meye yasa bazaka fawwalawa Allah komai ba Habeebullah ubangiji ba da kansa yake cewa (ashe haka zan barku kara zube? Shin bazan jarabceku ba?) Habeeb Allah nason bayinsa masu haƙuri da fawwala masa komai daya shafesu" hawaye ya share ya miƙe zai bar wajen ta riko hannunsa tace “meye ne?" Kasa yayi da kansa

Yace “Ta haihu Kilishi yanzu Shikenan yarinyata bazata Sanni matsayin ubanta ba?" Da sauri Kilishi tace “Habeeban? Yaushe ta haihu ina kaji kai ya akayi ka sani???" Ta jero masa tambayoyin cike da ruɗewa ya kawar da kansa yace “yau da asuba naga saƙonta kuma tun lokacin nake kiran wayar taƙi shiga" jinjina kai tayi tace “To a bibiyi number mana ai za'a gano daga inda ta rubuto saƙon" sosai yaji daɗin shawarar Kilishi domin da gaske ya manta da ana wani bibiyar number waya don gano daga inda ake amfani da ita.
Fasa shiga ɗakin nasa yayi ya fito ya kira Najeeb tare suka yini a campanyn layin wayar ba ƙaramin al'ajabu Habeeb ya shiga ba da akace masa Beebah tana garin Abuja inda tayo test ɗin ne suka kasa ganowa saboda layin ba akan waya yake ba.
Jikinsa har ɓari yakeyi da aka sanar dashi inda take ashe zuciyarsa ce a gurin shiyasa ya kasa barin Abuja ko zaman London ya kasa ko yaje baya jimawa yakejin hankalinsa ya dawo Abuja.

A ranar bai kwana a Dutse ba ya wucce Abuja ya nemi Wali yayi masa bayanin komai shima ya

cika da mamaki nan suka kuma ɗimawa suka fice domin Habeeb ya hanashi kwanciyar hankali gani yakeyi suna fita zasu ganota.
Haka suka shafe kwanaki suna jigilar nema abu kamar wasa sai gashi sun ɗauki kusan sati. Ranar wata asabar tun safe suke zaga gari yamma suna zaune cikin wani garden Habeeb ya kifa kansa saman tables ɗin abin duniya yabi yayi masa zafi, wayar Engineer Wali tayi ring ya zarota a aljihunsa tare da manna ta a kunnensa suka gaisa yace “kace zakazo taron raɗin suna kuma banganka ba" numfashi ya sauke yace “kayi afuwa abune yayi yawa Wlh amma bari yanzu mu taho dama muna ta arear taku" kallonsa Habeeb yayi kamar yace bazashi ba Wali yace “karkace komi don Allah inci wannan arzikin Dr Amin yafi ƙarfin haka a gurina"

Tashi yayi suka nufi mota daga inda suke zuwa gidan Dr Amin babu nisa suna isa suka ishe Dr Amin ya fito raka baƙi suka gaisa yayi musu jagora zuwa parlourn baƙin aka cika musu gabansu da abinci Habeeb dai tsakurar abincin kawai yakeyi Dr Amin ya kira wayar Safeenah yace “A kawo ma su Engineer Wali Ummusalma su sanya mata albarka" Habeeba dake zaune saman gado Safeenah ta duba tace.
“Kanin Dr ne yazo ki kai musu Bbyn su ganta" itadai Beebah hakanan taji gabanta na faɗuwa, ta jima bata tashi ba Saida Safeenah ta matsa sannan Beebah ta tashi ta fito daga dakin ta ɗauki kwalliya ta ban mamaki sai sheƙi takeyi.
Nufar ɗakin bakin tayi idanunta na kan Ummusalma.

Ta shiga dakin tare da sallama yana ganinta ya miƙe da mugun sauri ya fara nunata da yatsa itama ɗagowar da zatayi tayi tozali dashi ta sake ware injin idanunta akansa tace “Hab... Habeebullah....." Saurin juyawa tayi da mugun gudu zata fice a dakin yayi wani kukan kura ya cafkota cikin tsananin farin ciki ya kira sunanta sai hawaye sharrrr a ijiyarsa itakam itama zamewa tayi ta zauna a ƙasa ta rungume Ayyana mikin ciwon dalilin nesantata dashi yana dawo mata sabo ta rushe da kuka me ciwo tare da rungume Ayyana ƙam a ƙirjinta.
Tausayin kansu yaji ya ƙara nunkuwa a zuciyarsa ya zauna yana share hawayen idanunsa yace “Bantaɓa....." Saurin ɗaga masa hannu tayi tace “Don Allah kada kacemin komai Habeeb basai ka sanar dani halin da zuciyarka ta shiga ba saboda yanayinka ya nuna hakan idan kace zaka sanar dani zaka cusamin tausayinka a lokacin da tausayin bazai mana amfani ba nasan kanasona ka rayu dani a ranka tsayin shekaru ka zaɓi rabuwa da manyan jigogin rayuwarka saboda ni so amma hakan ta gaza samuwa kayi ƙoƙari inada yaƙini bazan taɓa maye gurbinka ba....."

Yanda ya ambaci sunanta da ƙaraji yasata miƙewa yakai hannunsa zai karɓi Ayyana ta janye har zuwa lokacin idanunta hawaye yake zubarwa yace “Meye yasa zaki hanani ɗaukar jinina" girgiza kai tayi tace “Ba jininka bace" daga haka ta nufi hanya ta fice daga dakin da sauri tanaci gaba da kukanta me taɓa zuciya. Safeenah data rako baƙi ta tsaya da mamaki tace “Beebah...." Bata kulata ba ta shige daki ta faɗa gado ta rushe da kuka me sauti tana cewa “Na shiga uku Ni Habeebah ya akayi Habeeb yasan ina garin nan har ya biyoni maɓoyata?"
Safeenah ce tace “Waye shi?" Ɗagowa tayi a gajiye idanunta ya kaɗa yayi jajir tace “Shine wanda nake baki labari mijina a baya uban ƴaƴana, Maman Ahmad nasan mijina yana sona amma inajin kamar mun rabu kenan"
Girgiza mata kai Safeenah tayi tace “ ba zaku rabu ba zakuci gaba rayuwa fiye da baya me daɗi kuma kyakkyawa bari naje naga meye ke faruwa Beebah har abada Habeeb naki ne"

Ficewa tayi daga ɗakin ta nufi ɗakin baƙin ta zubawa Habeeb idanu babu ko tantama ga kama nan a fuskar Ayyana.
Miƙewa sukayi dukkansu Dr Amin da jikinsa ya jima da yin sanyi tausayin Habeeb ya cika zuciyarsa tabbas Habeebah ta cancanci soyayya a gurinsa shima ya cancanci ta soshi ashe shiyasa kullum take cikin damuwa, hawayen Habeeb ya share yace “Insha Allahu zaka rayu da matarka da yaranka wannan abu duka ya faru ne a cikin gaibu sama da watanni biyar Beebah take gdana take zaune da iyali na nasani Tanaji da ganin mutumcin Safeenah ita kaɗai ce zatayi maka aikin rarrashin zuciyarta nasan zata sauko"
Kallon Safeenah yayi yace “Mijinta ne kije ki ɗauki masa ƴarsa ya ganta ashe Ummusalma ɗin da ta zaɓawa yarinyar sunan surukarta ne" fita Safeenah tayi ta dauko Ayyana ta dawo ta miƙawa Habeeb ya  rinƙa zuba musu hoto shida yarinyar don a yau yakeson zuwa ya dauko Kilishi tazo taga takwararta tunda yasani yanzun ko giyar wake yasha bazaice zai ɗauki Beebah yakaiwa Kilishi ba duk da alamu sun nuna cikin waɗanda ta riƙe a ranta babu Kilishi.

Kuɗi ya zara masu nauyi ya bawa Safeenah yace a bawa Beebah kafin yawo sukayi sallama suka tafi zuciyar Habeeb wasai yau yaga abar ƙaunarsa, suna zuwa gidansa ya haɗa kayansa yace da Wali yakaishi airport yau ɗin nan Dutse zai kwana.
Bakwai ya shiga gdansu ya tarar da kowa a babban parlourn ciki harda Khausar tana durƙushe gaban Sarki Khalil tana kuka.
Bai sauraresu ba ya wuce zuwa ɓangaren mahaifiyarsa tana ganinsa tace “Ya kiraka kenan?" Dubanta yayi da rashin fahimta yace “Wa ba?" Kawar da zancen tayi tace “Ina labarin ƴata da jikata" fara'arsa ya faɗaɗa yace “yau naga Zuciyata taganni saidai taƙi aminta dani Kilishi Kinga shaida" nan ya fara nuna mata hotunan ta rungumeshi tana dariya tace “Alhmdllh Ya sunan Bbyn?" Shafa kansa yayi yace “yau da yamma yayan abokina Engineer Wali  wato Dr Amin ya kiramu ana suna a gidansa ƙanwar matarsa ta haihu muka tafi domin tayasu murna shine ya

kira matarsa domin ta kawo mana Bbyn abin mamaki sai ga Wyf ɗauke da wannan kyakkyawar yarinyar tana ganina ta kira sunana na mike, amma fah Kilishi Wyf ta sanar dasu Ni mijinta ne a baya banda yanzu inda Ni kuma nayi musu bayanin komai yanzu dai sun bani hƙr sunce zasu tausheta"
[5/25, 3:12 PM] AM OUM HAIRAN: _*BMGJY Bonus 51-52*_

_Ku biya ta acct detail  3184512451 First bank ko kati MTN ta WhatsApp number 09013718241._
_Normal 300 PC 700_
_Ƴan Niger zaku biya 500f ta wannan number +227 95 04 58 22_

_Ban amince a juyamin littafi ta kowacce siga ba._

_End! End!! End!!!_

Tunda Habeeb yabar garin Abuja yabar Safeenah da Dr Amin da rikicin Beebah don gabaɗaya ta rikice musu cikin kwanakin batada wata walwala indai kaga tana dariya to ba'a sako mata zancen Habeeb bane da zarar anyi mata zancen shi zata haɗe rai ta fara kumbura ga Safeenah da nacin magana ta rinƙa nuna mata damuwarta da lamarin Habeeb kenan har sai taga ta ƙosa tana shirin tashi tabar gurin sannan zata ƙyaleta.
Abin da yake bawa Safeenah mamaki bai wucce yanda tasha kama Beebah tana kuka ko kuma cikin bacci taji tana ambaton sunan Habeeb ɗin ba amma kuma a zahiri idan akayi mata batunsa sai walwalarta ta ɗauke, to yauma kamar ko yaushe tana zaune a ɗaki ta gama yima Ayyana kwalliya tana taje mata gashinta taji Muryar Safeenah na cewa.
“Ashe bakine damu a gidan sannunku da zuwa" duk da batasan su waye ba Saida gabanta ya faɗi haka tadai maze taci gaba da yiwa ƴarta wasa a haka Safeenah ta shigo ta sameta fuskarta wasai alamun farin ciki tace “Kizo kinada manyan baƙi a parlourn baƙi" bata jirayi abinda zata ce ba duk da taga alamar cewar a tattare da ita ta juya ta fice bayan ta karɓe Ayyana a hannunta, jiki babu ƙwari haka ta miƙe ta ɗauki mayafinta ta yafa ta fice daga dakin ta nufi ɗakin baƙin gabanta naci gaba da faɗuwa.

Tura ƙofar tayi ta shiga tare da sallama idanunta ya sauka kan Jumme dake zaune gefenta mahaifinta ne riƙe da Hudais sai Kilishi dake dauke da Ayyana, tsayawa tayi turus tanajin wani faduwar gaba na shigarta tare da bin iyayen nata da kallo ɗaya bayan ɗaya.
Riƙo hannunta akayi ta juya ta dubi wanda ya riƙe hannun nata ganin Habeeb ne ya ɗaganta

gira tare da janta har zuwa inda mahaifan nata ke zaune tana isa ta zube a gabansu da sauri jikinta na rawa tana wani irin kuka ya ƙwace mata data kasa sanin na meye farin ciki ko nadama? Tabbas tayi farin cikin ganin iyayen nata sun taso takanas dominta, sannan nadamarta ta tsayin watanni ta dawo mata sabuwa tabbas da tabi umarnin Mahaifanta ta nuna jajircewarta da bata fuskanci wani wulaƙancin ba tasani yan ɗakin da mijinta yafito da mahaifiyarsa sun sota sun kaunaceta da kaunar da mijinta yake yi mata, duk da tasan cewa bata isa kaucewa kaddararta ba tunda Allah ya ƙadarta Habeeb shine uban ƴaƴanta to ko bataso sai ya zama mijinta amma tayi wasarairai da ƙimarsu.....
Cikin kukan me taɓa zuciya ta buɗe baki tace "Jumme Baba nasani na cusa baƙin ciki da damuwa a zuciyarku duk da cewar kunyi ɗawainiya dani tundaga samuwata har zuwa girma na, a lokacin da zan nuna muku tabbas kuɗin iyaye ne na kwarai duk da rashin hasken musulunci a cikin rayuwarku baisa kunyi wasarairai da tarbiyya ta ba, kawai sai ƙaddara ta jefomin shi cikin rayuwa ta har naji a raina gara na barku dana barshi, inason Habeeb nasani shima yayi domin Ni yayimin halaccin da maza masu irinsa sunyi ƙaranci a duniya saboda Ni ya amince ya rasa komai daya mallaka ta bangaren mahaifinsa ƙarshe kuskuren mu mu biyu ya haifar min da damuwar da har na mutu bazata goge ba, ko sanda bana cikin musulunci ban kaunaci zina ba na ƙyamace ta na tsaneta har kawo lokacin da Habeeb ya zama mijina, kwatsam waini Habeebah saboda son zuciyar kishiyata kishiyar surukata da iyayen kishiyata yasa sukayi amfani da ƙiyayyar da mahaifin mijina yakemin aka barratani da mijina a lokacin da nake buƙatarsa aka rabani da ɗana da nake kallonsa a matsayin gata na..."

Kukanne yaci ƙarfinta daƙyar ta buɗe bakinta tace "nasani haƙƙinku ne wlh badon banason Habeeb ba amma na zaɓi yi muku biyayya wannan karon matuƙar zaku yafemin kuskurena na baya da rudin ƙuruciya yasani aikatawa kuyimin afuwa ku yafemin don...."
Rufe mata baki Jimo yayi yana murmushi yace "Kayyah Bibon Baba wannan ai ya zama shuɗaɗen labari ƙaddararki ce kamar yanda Liman ya fada mana ina zamukai rabon Waɗannan yaran Habeebah dakin matsa ma wajen yimin biyayya da tuni ba labarina akeyi ba kila da tuni ƙasa ta jima da rufe idanuna kece da hƙr Bibo da ban hau dokin zuciya ba da baki wulakanta ba kuma da da haka ta faru mu zaki nufo mu share Miki hawayenki nikam na yafe Miki tun ranar da hasken musulunci ya ratsa Zuciyata Habeebatullah kije ki rayu da mijinki da yaranki cikin aminci kuma na tabbatar kafin Ni mahaifiyarki ta jima da yafe miki"

Kwantar da kanta tayi saman cinyar mahaifinta taci gaba da rera kukanta na farin ciki tana gdy ga Allah da ya ƙadarta mata ganin wannan rana itakam da basu yafe mata ba da batasan ya zatayi da rayuwarta ba.
Ji tayi an kama gashinta anja ta ɗago tare dayin murmushi ashe Hudais ne ta miƙa masa hannu ya taho jikinta ya kwanta luf yana sauke ajiyar zuciya ta dubi Kilishi tace "Kilishi dama a gurinki

yake ba a matar babansa ba?"
Murmushi Kilishi tayi tace “babanshi ai bashida mata tun washegarin ranar da kika bar gidan itama ta bari gara kema kullum muna hasashen dawowarki itakam ta tafi kenan yanzu haka ma tayi aure shekaran jiya ta tare a gidanta" ajiyar zuciya ta sauke dama tasan auren Khausar da Habeeb wataran dole zai ƙare don da gaske Habeeb yake Khausar bata tsarinsa amma bataso ace itane sanadi ba.

Ranar yini akayi ana hirar yaushe gamo iyayenta kamar su mayar da ita ciki Safeenah sai hidima takeyi da baƙi tsakanin Beebah da Habeeb kuwa Saidai kallo kawai Allah yasani tasan baiyi mata komai ba amma ta ƙudurce a ranta matukar ba Mai Martaba ne ya amincewa zamansu matsayin ma'aurata ba to ta hkr dashi itakam ta daidaita da nata iyayen shima tanaso taga ya samu daidaito da mahaifinsa a washegari suka ɗauki hanyar Dutse harda Beebah tunda suka taho gabanta ke faduwa bata fatan ace su sauka a gidan sarauta saboda komai zai dawo mata sabone.
Ga mamakinta sai taga sun nufi wata babbar unguwa ta manyan attajirai an buɗe musu wani get sun shiga yayi parking suka fito shine yayi musu jagora har cikin gidan yana nuna musu ko ina Saida ya gama nune nunensa sannan ya juyo ya dubi Habeebah yace “gidanki ne da zaki rinƙa sauka idan kinzo hutu daga London saboda ina tunanin nan da 2 weeks zamu tafi" Saida taji wani dam a ƙirjinta tayi masa wani mugun kallo sannan ta kawar dakai anan sukaci sukasha kukunsa ya shirya musu komai Saida suka gama sannan ya ɗebesu suka nufi tsohuwar unguwar su shima tsohon gidan cikin watanni biyar zuwa shidan ya gyara shi sosai ya sake masa kayan cikinsa Saida suka gama dubawa sannan ya dubeta yace.

“Wannan kuma nakine halak malak Habeebah bansan dame zan saka miki soyayyarki gareni ba sannan bansan dame zan goge Miki tabon mikin da akayi Miki a duniya kawai saboda a rabani dake ba wlh tallahi Habeebah tun kafin bayyanar gaskiya Ni nasan bazaki taɓa aikata abinda akace kin aikata ba kuma Kilishi ma da su Hudah sun shaideki akan hakan, mun riga mun yanke hukunci Baba da Jumme zasu zauna cikin wannan gidan saboda wata hatsaniya da tasa suka baro garin Tsaunin gawo dalilin karɓar addinin Musulunci da sukayi"
Tunda ya fara maganar take kallonsa idanunta na zubar da hawaye tana girgiza masa kai har Saida ya gama sannan tace.
“Bana bukatar komai daga gareka Habeeb Ni burina naga kun daidaita tsakaninka da mahaifinka yaci gaba da sonka da janka a jikinsa kamar yanda yake yi a baya burina ya karɓeni matsayin suruka nasani inasonka saidai so bazai rufe mana idanu a karo na biyu mu kara yin abinda zamu zo yaci gaba da bibiyarmu har jikokin mu ba, nasan kafini sanin girman haƙƙin mahaifa akan ƴaƴansu...."

Tunda ta fara maganar yake kallonta har ta gama yayi murmushi yace “hakane kema kince wani abu saidai ki sani Mai Martaba jikinsa yayi sanyi tun lokacin da naje na nuna masa hotunan Ummi na na sanar dashi kin haifa min ƴa mace a ranar yake cemin naje na dawo dake ɗakinki komai ya wucce a manta da duk wani abu daya faru dama shi tunda abin ya faru yake tuntuntuni akan abin sai gashi yaron da kansa yazo ya ƙaryata kansa batare da wani ya takurasa ba yace sashi akayi yazo a daidai lokacin aka shirya plan na yanda za'a gayyato Mai martaba yazo ya kamaki da kansa,
Idan baki gasƙata abinda na faɗa Miki ba yanzun mu wucce gidan sarautar kiji da kunnenki....."

“Basai kunzo ba Ni nazo" sukaji an faɗa a bayansu juyawar da zasuyi sukaga Mai Martaba tsaye da dogarawansa jikin ƙofa ya tako fuskarsa dauke da murmushi har gaban Beebah ya riƙo hannunta yace “So da yawan lokaci munayin hasashe baibai da daidai mukan hasaso abinda yake saɓanin gsky sai zukatanmu su tafi akansu har su rinƙa tursasamu akan cewa wannan abin shine daidai, na hasashi kuskure na tafi akansa nayi jayayya da abinda ubangiji ya hukunta karshe nayi zaɓi sabanin na ubangiji na takura masa Saida ya karɓa bisa shawarwarin Ƙanina Lukman da Hajiyan ƙofa ashe duk a keken ɓera suka ɗora ni yanzu gashi Ni da idanuna yayanku Ahmad ya ɗaukeni ya kaini wani hotel na kama Khausar da hannu na da maza tana shaye-shaye turr da wannan asara da taɓewa Habeebah duk da an daɗe ana faɗamin Khausar ba sa'ar auren Habeeb bace bantaɓa yarda ba sai ranar kuma abin mamaki harda yaron da akace kece kika gayyato shi don buƙatar kanki saboda Kinga mijinku bayanan daganan na tabbatar duk wani abu daya faru makirci ne akayi amfani dani don shiga tsakaninki da mijinki Habeebah kiyi hkr ki rayu a gdanki tare da ƴaƴanku kamar yanda nakewa kowacce ƴa dana haifa fata"

Sosai Habeeb yaji daɗin yanda mai martaba ya wankesa ya sani ba don Allah ya kawosa yayi bayani dakansa ba da babu kalmar da zai yi amfani da ita wajen fahimtar da Beebah,
Shida mai martaba da Kilishi ne suka tafi inda suka bar Beebah da iyayenta sunata mamakin karamcin surukanta sunata hirarsu ta yaushe gamo nan suke faɗa mata mutuwar Baba Uda taji mutuwarsa sosai har hawaye tayi.
Rayuwarta me takeyi ita da iyayenta saboda Kilishi ta hanata komawa gdansa tace ta bari tayi arba'in ransa baiso ba hakanan ya hkr ya haɗa nasa ya nasa ya wucce London.
Yanda Habeeb ya mayar da hankalinsa wajen kula da iyalinsa abin ba'a cewa komai bayan tayi arba'in ya harhaɗa masu nasu ya nasu suka ɗauki hanyar birnin London daga wannan lokaci

komai ya wucce rayuwa ta saitu kamar babu wani abu daya taɓa faruwa komansa Beebah komai ya tashi yi da ita yake shawara, ga yaransu dagwai dagwai gwanin ban sha'awa Saida Ayyana ta shekara Biyar sannan Beebah ta sake haihuwar yaronta namiji yaci Sunan Mahaifin Beebah wato Muhammad kasancewar bayan musuluntarsa cewa yayi akirasa da Muhammad.

_Tammat bih hamdullah_

_Wannan littafi Mai farin jini nan  na kawo karshensa kuskuren dake ciki Allah ka yafe mana ba don halinmu ba Allah ka bamu ikon amfana da abubuwan amfanin cikinsu._